murmushi SEEDRAH tayi, Zeey ta fito suka gaisa kana ta mika mata laidar data sako kayan da jiya suka bata, Zeey ta karb'a taje ta d'auko mata nata da ta barshi a nan, ta amsa tare da yi musu godiya tayi musu sallama ta fita.
a bakin kofar gidan suka had'u da Kamal, ta d'auke kai tayi gaba..
kamar zaiyi mata magana sai kuma ya yi shitu, yabi bayan ta da kallo har ta b'acewa ganin sa. sakai ya yi ya shiga gidan.
Zeey ya tarar ita kad'ai a tsakar gidan,
ta gaishe shi ya amsa tare da tambayar ta ina Mukhtar?, dan tun jiya yake neman sa bai gansa ba, ya yi masa kiran duniyar nan a waya baya d'aga wa.
ta ce "Ai ni rabo na da Ya Mukhtar tun jiya da kuka fita sallar magriba, kai d'aya ma kazo ka ci d'anwake na baka kushe ba, kuka fita da yarinyar jiyan nan, wai wace ce ita ne Ya Kamal ko me iya girkin ne ka samo?."
ta karashe maganar tana dariya. shima dariyar ya yi mata yanufi d'akin Mukhtar yana fad'in
"Bari na duba shi ko yana ciki ina zuwa dai."
ya na zuwa bakin kofar d'akin  Mukhtar ya tura kofar yajisa a rufe gam, har ya yuya
zai wu ce ta jikin windon d'akin yajiyo karar wayar sa.
ya maso jikin windon tare da zuge glass d'in windon ya leka. can ya hango sa kwance saman katifa rigingine fuskarsa na kallon sama.
kofar ya dawo ya shiga bubbugawa yana fad'in
"Mukhtar kazo ka bud'e min kofar nan."
sai da ya yi ta bubbuga kofar kamar zai b'alla kafin ya taso yazo ya bud'e masa, baya ya yi ya koma ya zube kan katifar yana mai dafe kansa.
Kamal ya shigo d'akin tare da mai da kofar ya rufe, ya tako gaban sa yana mai kare masa kallon tuhuma, hannunsa ya zura cikin aljuhunsa ya zaro agogon Mukhtar d'in da jiya ya gani yafad'o daga jikin Nasiba, ya mika masa yana fad'in. "Ga agogon ka da ka mance da shi jiya."
kai Mukhtar ya sunkuyar yana mai taunar lips d'in sa na kasa, tabbas yana mai danasani da nadamar aikata wa yarinyar nan fyad'e, wan da shi kansa baisan ta yan da akayi zuciya ta kaisa ga ai kata hakan ba, tun bayan faruwar haka jiya yarasa ina zai tsoma rayuwar sa ya shigo gida babu wan da ya sani ya kulle kansa har yau.
Kamal ya dube sa da kyau ya ce

"Me ka aikata kenan kasan girman laifin abun da ka aikata kuwa Mukhtar?!, yaushe ne halin ka ya juya izuwa halin banza Mukhtar? mu da muka biyo su domin share tantamar mu ko matan banza ne, shine kai zaka nuna halin banza a kan ta, yaushe halinka ya koma haka ne Mukhtar?."
da sauri Mukhtar ya d'ago tare da ruko hannun Kamal murya a raunace ya ce
"Aboki na kafi kowa sanin halina, kasan wannan ba halina bane, wlh tun jiya da hakan ta faru nakasa samin sukuni a rayuwa ta, ban san yan da akayi har na kai ga aikata hakan ba, tabbas na yar da idan mace da na miji suka keb'e guri guda to shaid'an ne cikon na ukun su, shi ya angiza ni izuwa aikata hakan, wlh ban san ta yadda akayi na sinci kaina cikin aikata hakan ba."
d'an shiru Kamal ya yi bashakka yasan ko waye abokin nasa, tabbas shaid'an ya sami galaba a rayuwar sa a karon farko.
ya ce "To sun ce bazasu kyale ba zasu shigar da kara kotu."
da sauri Mukhtar ya ce
"Ina maraba da karb'ar duk wani hukuncin da za a yi min, wata kila hakan zaisa zuciyata tasami sassauci daga halin da nake jin kaina yanzu, Kamal zuciya ta kamar zata fashe dan zafi."
ya janyo hannun Kamal ya d'aura shi dai-dai kahon zuciyarsa.
Kamal ya jinjina kai cike da alhenin abin kana ya ce
"Bakaci abinci ba tun jiya har yau taso kaje kayi wanka muje  kaci abinci."
kai ya girgiza cike da jin zafin da zuciyarsa ta ke ya ce
"Ina jin kunyar had'a ido da Maman Zeey, bansan da wani ido zan kalle ta ba."
Kamal ya ce "Maman Zeey bata san komai ba kuma nasan zata fahimce ka dan tasan wani irin tarbiyya ta baiwa d'an ta, je kayi wanka kazo muje kaci abinci."
ya mike jiki a sanyaye yashige bayi...

SEEDRAH tana komawa gidan Goggo Larai, ta sami Nasiba har tayi wanka.
babu laifi jikin ta ya dad'a warwarewa suka saka kayan su suka ajewa goggo nata sukayi mata sallama suka tafi.
sai da SEEDRAH ta raka Nasiba har gida kafin ta wuce gidan su dan ga gida ga gida ne sakanin gidan su da gidan su Nasiba.
ta shiga da sallama direct d'akin Mamarta ta wuce.........!

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna KARSASHI kada ku manta kafin zuwan KARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 KARSADHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciyar masoya salon labarin na daban ne. ko dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa KARSASHI! ƘARSASHI!! KARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08034690734_

*________________________________________*

*🌈🅺AINUWA 🆆RITER'S✍🏼*
*🅰SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association
```

*_________________________________________*

🅿️4

Mama da ke zaune cikin d'aki tana ninke kaya ta amsa.
SEEDRAH ta karaso ta aje jakarta tana cire mayafin ta ta ce
"Barka da gida Mama ina kwana."
batare da Mama ta amsa gaisuwarta ba ta ce
"Amma ai bamuyi dake zaki kwana ba kikasa babun ku yazo yana ta yimin masifa."
zubewa SEEDRAH tayi kan kuje ra tana fad'in
"Ayya Mama jiya baki ga ruwa ake da daddare ba shi yahana mu dawowa, a gidan goggo Larai muka kwana da Nasiba."
"Shi ne bazaki kira gida ki fad'a ba? kin san halin Baban ku sarai idan ya shigo bai ganki ba yarika kira kenan."
"Yi hakuri Mama, wayar tawa a gidan Nabila na barta jiya sai yau naje na d'auka." SEEDRAH ta fad'a tare da gyara zama tashiga taya Mamar tata ninke kayan su data wanke musu da safen nan.
Mama ta ce "Sabo da shashanci irin naki waya ya kwana wani guri ke a wani gurin, Allah ya shirya, sai ki tashi kije ki d'aura girki da ma yanzu nake da shirin shiga kitchen d'in wankin kayan ki ya sai da ni."
ta ce "To me za'a girka Mama?."
Mama ta ce "A kwai shinkafa a store da Abba'n ku Sulai ya aiko da shi d'azu, ina ga akwai ragowar manja da yaji a kitchen sai ayi mai da yaji, dan Baban ku baice komai ba game da girki ga rana tana ta yi."
kai SEEDRAH ta jinjina ta ce
"Mama haka za'a girka zallar mai da yaji babu wake?."
"To ina kika ga waken waken daya kare tun ba yau ba, je ki girka abin da ya samu kawai."
a hankali SEEDRAH ta mike tana jinjina lamarin dake dad'a ta'azzara game da mahaifin nasu. abun kamar wani kariyar arziki gida kamar gidan su babu wan da zai ga gidan ya ce basufi karfin komai na rayuwa ba. sai gashi abun da zasuci ma yana kokarin fin karfin su, wai har ya kaiga d'an uwan mahaifin su ke aiko musu da abinci, wanda a da mahaifin su yana daga cikin masu kud'in unguwar su,
rayuwa kenan.
takuma jinjina kai tana fita daga cikin d'akin Mama.

A sakar gida ta tadda su Suhailat da Halimatu yayun ta wan da suke uba d'aya da Umma wato mahaifiyar su kishiyar Mama.
Suhailat rike da waya a kunnen ta tana daga d'an can gefe, Halimatu tana yiwa Umma tsifa.
"Ina kwana Umma."
SEEDRAH ta fa d'a tana karaso in da suke.
Umma ta ce "Lafiya lau kawayen amarya andawo ne?."
ta ce "Eh." Halimatu ta dube ta ta ce "Baba sai tambayar ki yake ko d'azu ma sai da yayi magana."
"Ai yanzu Mama take fad'a min jiya ruwa ne yahana ni dawowa nakwana a gidan goggo Larai."
SEEDRAH tayi maganar tana wuce wa kitchen, tashiga kiciniyar d'aura abinci.
tana gamawa ta zuba a kula mai d'an girma ta kai d'akin Umma kana ta d'au na d'akin su takai, sannan ta dawo ta d'auki na  Baba ta nufi d'akin sa.
da sallama ta shiga d'akin nasa,
Baba da ya ciro hular kansa yana kokarin ajiwa da alama yanzu yashigo gidan, ya amsa sallamar.
takaraso ta aje tray'n data dauro kular abincin da plt da cokali, ta d'ago tana fad'in
"Sannu da dawowa Baba."
ya ce "Yauwa SEEDRAH yanzu Maman ki take ce min wai gidan goggon ku kika kwana."
ta ce "Eh Baba ruwa ne ya tsare mu shine na biya gidan ta."
ya ce "To a rika kiyaye wa dai, je ki kirawo min Maman naki."
ta ce "To Baba."
ko da taje ta sanar wa Mama Baba na kiran ta hijabin ta ta d'auka ta ce wa Mama zata shiga gidan su Nasiba ta duba ta jiya sun kwana tana zazzab'i.

Koda ta shiga gidan su Nasiba a tsakar gida ta tadda Mama Kubura kishiyar Maman Nasiba wacce a hannunta take tun bayan rasuwar Maman Nasiba, ta gaishe ta tana tambayar Nasiba'n ta na ciki ne?.
ta ce mata Eh.
ta shige d'akin a kwance ta iske ta tayi shiru kamar me yin bacci,
tana ganin SEEDRAH tayi mata murmushi, SEEDRAH ta dube ta da kyau daga jiya zuwa yau kawai tayi wata y'ar rama, girgiza kai tayi cike da tausayawa tana zama kusa da ita.
a hankali Nasiba ta mike zaune, tana mai cigaba da k'wak'ulo murmushin yake da bai kai ciki ba dan b'oye damuwar ta.
SEEDRAH ta ce "Yajikin dai Nasiba Allah yasa dai bata gane komai ba."
ta ce "Ta so ta gane dan tun fitar ki d'azu dana fita zan shiga bayi tarika bina da kallo, har tana tambayata wai ko ciwo naji a kafata taga kamar ina d'ingishi, na ce mata a'a babu abin da yasame ni a kafar, SEEDRAH ina tunanin ranar da zata gane bazata tab'a yar da kan anyi min fyad'e bane, za ta ce maza nake bi da ma can tasaba fad'a shike nan zata sami hujjar da zata kafa har Baba ya yarda."
kukan da ke son kwace mata ne yasa ta yin shiru tana mai zubda kwalla.
da sauri SEEDRAH ta rike hannunta yayin da tuni itama hawaye yafara zuba a idon ta ta ce
"In sha Allah bazata tab'a ganewa ba kidage da sarki da ruwan zafi har gurin ya gama warkewa

gaba d'aya, yanzu tun da ta fara kawo zargi kan tafiyarki to zata saka miki ido ne sosai dan gano abun da take zargi,to kada kibata kofa kiyi kokarin ganin komai yayi normal ta inda zaki jirkita mata tunanin ta takasa gane komai, kuma bazata ganen ba in sha Allah."
kai Nasiba ta gyad'a kana tashiga share hawayen ta, itama SEEDRAH hawayen nata ta share nan suka shiga d'an tab'a hira sai wajen karfe 3 kafin ta koma gida...

Da yamma SEEDRAH na share d'akin Mama wani yaro yashigo ya ce "Wai SEEDRAH ta zo inji wani a waje."
Mama dake zaune sakar gida ita da su Umma ta ce
"Inji wa kenan kuma izinin wa ya nema daya zo gurin ta? je ka ce masa an bashi izinin zuwa wajen ta ne."
Umma ce ta dakatar da yaron da fad'in
"Je ka ce ta na zuwa." kana taci gaba da fad'in
"Idan ma ba'a bashi izini ba yanzu idan ta fita in tasan shi takuma aminta da shi sai ta bashi izinin zuwa wajen mahaifinta ya nemi izini sai ya cigaba da zuwa."
Mama ta ce "To ai sai ki zo ki je kiga ko waye ne, ai yanzu haka ma ita tasa shi ya zo zaiyi zuwan gashin kansa ne."
mayafi SEEDRAH taja ta fito tana turo baki gaba
"Ni wlh ban san da zuwan kowa ba koma wane ne zan je nasa me shi ni."
tayi waje tana cigaba da turo baki da kunkuni, dan ita ba'a tab'a zuwa gurin ta haka kai tsaye ba hasali ma bata hira ko a waya ne dan ko saurayi bata da shi bawai kuma babun bane saurarar su ne bata yi.
da mamaki take kallon wan da ke tsaye a kofar gidan nasu yana jin gine a jikin mashin d'in sa. b'ata fuska ta kumayi taja tatsaya jikin get, tana mai mamakin yan da a kayi yasan gidan su har ya zo.
Kamal kuwa na ganin ta yasaki murmushi kana yata ko in da take.
"Madam barka da warhaka, suna na Kamal." ya fad'a yana mai cigaba da sakar mata murmushin sa mai sanyi.
fuska takuma had'e wa ta ce "Me kazo yi gidan mu ko kazo ne har nan d'in ma kakirawo d'an uwan naka ku kuma aiwatar da mugun nufin ku a kan mu?."
kai ya jinjina kana ya ce "Kizamo mai yafiya mana, wlh bai aikata abun da ya aikata da gangan ba sharrin shaid'an ne."
wani irin murmushi ta sake wan da ya dad'a bayyano da ainahin k'yan fuskarta kana ta gimtse ta ce
"Wai ku mutane bakwa da kunyar yiwa shaid'an kazafi ne? ranan gobe kaje ka tsaya gaban ubangiji ka ce shaid'an ne ya sashi, shikuwa shaid'an zaifito yakare kansa dan baka da hujjar dazaka kuma dogara da shi kan shed'an ne yasaku aikata ba dai-dai ba, dan baka tab'a ganin sa da ido ba, ya tabbata kuwa kune shaid'anun kanku."
ido ya zuba mata yana ji da kallon yanda take zuba zance y'ar karama da ita da iya tsara zance kamar wata babbar mace.
murmushi ya yi ya ce
"To Allah dai yana son me yafiya, da ma nazo ne naga ya jikin nata, dan Allah ko zaki kirawo

min ita nagaishe ta da jikin?."
baki ta tab'e ta ce "Bazata zo ba bata bukatar gaisuwar taka kaje ka da abin ka mun yafe."
ta juya tana kokarin shiga gida ya yi saurin datakar da ita ta hanyar shan gaban ta ya had'e hannayen sa biyu alamun roko ya ce
"Dan Allah kuyi hakuri kuyafe wa aboki na wlh abokina mutumin kirki ne sharrin shaid'an ne kawai da kuma kaddara, idan kuka bashi da ma zai zo har nan ya nemi gafarar ta shi kansa yanzu haka yana cikin mawuyacin hali da matukar damuwa da tashin hankali had'e da nadamar abun da ya aikata,
amma ki sani babu bawan da ya wuce kaddara na tabbata shi yafita shiga damuwa da tashin hankali acikin halin da yake yanzu, yakuma shiryawa karb'ar duk wani hukuncin da za'a yanke masa."
wani kallo ta wurga masa ta ce
"Yafita shiga damuwa da tashin hankali?,
bayan ita ya yi wa mugun illa a rayuwar ta, shi me yaragu a jikinsa?."
tayi masa tambayar tana k'afe sa da manyan idanunta.
d'an lumshe ido ya yi tare da kuma bud'e su a kanta jin yadda idanunta ke yawo cikin jikin sa. ya ce
"Sanin ita ya raunata shiyasa ya shiga damuwar dan Allah kizamo mai dai-dai ta lamura dan suffarki yafi kama da mutanen kwarai, nafuskanci har yanzu baki huce ba zamu dawo nan da kwana uku da shi kan nan nasan kin dad'a hucewa kibamu damar ganin ta."
k'wafa tayi tare da shige wa cikin gida batare da ta kuma ce da shi komai ba, shima ya haye mashin d'in sa ya yi gaba.
ko da ta koma gida Mama ke tambayar ta wane ne?, ta ce daga cikin abokan ango ne.
ta fad'a mata hakanne dan bata so ta tsananta bincike a kansa.

Washegari da safe bayan SEEDRAH tayi sallah a d'akin su d'akin Mama ta dawo ta kwanta sabo da damin ta da Suhailat take da waya, duk da nauyin bacci irin nata har idan ana surutu a guri sai tayi da gaske kafin baccin ya d'auke ta.
cikin jin dad'in baccin da take taji ana bubbuga ta da karfi, mika tayi cikin magagin bacci takuma juye tagyara kwanciyar ta.
da karfi Halimatu ta d'aka mata duka a cinyar ta da zanin ta ya yaye tagefen santalelen cinyar ta d'aya, ta na fad'in
"Banza mai shegen d'an banzan nauyin bacci har wani abun guduwa ya faru a gudu a barki kina wannan shegiyar baccin naki."
a d'an razane ta mike tana susa gurin da Halimatu ta zuba mata duka tana fad'in
"Wayyo ni me nayi miki?."
Halimatu ta ce "Banza tashi dalla kowa ya fito ke kina d'aki kina baccin asara, gawasu can sun kuma janyewa Baba kud'i a account d'in shi."
da sauri ta duro a gadon tana fad'in
"Yau ma kuma?." waje tayi da sauri Halimatu tabi bayan ta.
a can parlour'n Baba ta tadda duk y'an gidan tsaye curko-curko Baba ya na zaune yadafe kansa da duk hannayen sa biyu.
hankali tashe tazube gaban sa tana fad'in

"Baba wai sun kuma kwashe maka kud'i!?."
hannunsa ya janye a kansa yad'an zuba mata ido kana ya gyad'a mata kai ya ce
"Wannan karon ko sisi basu barmin ba duka suka kwashe."
hawaye ne ya ciko idon ta kan kace me sun fara tsiyaya ta ce
"Baba katashi kaje banki mana su binciko maka masu ai kata maka haka ai dai dole zasu san ko su waye ne."
kai ya girgiza ya ce "Ba na tunanin zasu yimin komai a kai dan wancan karon ma dasuka ce zasu bincika har yau babu wata kwakkwaran amsa, nayi sintirin banki harna gaji, amma dai zanje dan yau kam gaba d'aya suka kwashe ni, dan jiya da daddare aka turo min da kud'in dana siyar da filaye da sauran kaddarorina kan zan gina wani masana'an ta, yau da safen nan kuma suka kwashe duka da ragowar kud'in da ke cikin accaunt d'in."
ya mike ya na fad'in "Bari dai naje ko bankin basu fito ba zan jirasu har su fito."
yazari makullin motar sa ya yi waje..

Gaba d'aya y'an gidan yau basu da walwala duk wan da ka gansa kasan yana cikin damuwa, gashi suna ta kiran Baba baya d'agawa.
tun safe sai wajen k'arfi uku kafin yadawo, gaba d'aya suka hallara a parlour'n sa, nan yake sanar musu banki sunyi iya binciken su sunce basu gano wad'an da suka aikata masa hakan ba, amma yaje wani sati yadawo kafin sun dad'a fad'ad'a bincike.
basuji dad'in jin hakan ba sai dai basu da yadda zasuyi..

Kamar yanda Kamal ya ce wa SEEDRAH zasu dawo da Mukhtar bayan kwana uku, hakan kuwa akayi da yamma suka zo kofar gidan su SEEDRAH ya ai ka aka kirata, tana ganin sune ta b'ata fuska a jikin get ta tsaya ta hard'e hannayen ta akirji.
murmushi Kamal ya yi suka karaso in da take.
Kamal ya dube ta da murmushi d'auke a kan fuskarsa ganin yanda tawani sha kunu, shi harga Allah yarinyar dariya take bashi idan yaga tana wani b'ata rai ga iya zare zance kamar wata babba, a kallon da yake mata shekarun ta bazasu wuce 17 zuwa 18 ba.
ya ce "Ranki shidad'e barka dawarhaka da fatan kina lafiya?.
kad'a kwayar idanunta tayi ta ce " Gashi dai kana gani."
kai ya girgiza Mukhtar daya d'an sunkuyar da kansa ya d'ago "Barka da yamma ya gida?."
batare da ta amsa masa ba ta ce "Kufad'i a bin da ya kawo ku nagode da gaisuwa."
Kamal yad'an gyara tsayuwar sa ya ce
"Ina fata zuciyarki tad'an sanyaya cikin kwanaki ukun nan, kamar yadda na fad'a miki zamu dawo bayan kwana uku gani ga Mukhtar dan Allah ki kirawo mana kawarki munimi gafarar ta."
"Bama bukata kuje abun ku kudai cigaba da zaman jiran kira daga kotu."
da sauri Mukhtar ya ce "Please dan Allah kiyi hakuri ki kirawo mana ita dan Allah! badun niba, a shirye nake da karb'ar duk wani hukuncin daya sauka a kaina amma kafin nan ina so na had'u da ita nanemi yafiyarta dan Allah!."
baki ta tab'e kamar zatayi magana sai kuma ta juya ta nufi gidan su Nasiba.
a gurin wanke-wanke ta isketa tana wanke-wanke,ta sunkuyo kanta a hankali ta ce
"Mutanen nan ne suka zo wad'an da suka bimu a unguwar su Nabila, ranar d'ayan ne yazo wan da yad'auke ki a mashin d'in sa ya kaiki gidan goggo wai shi Kamal yaso nakiraki naki, shine ya

ce zasu dawo bayan kwana uku ban fad'a miki bane,suna ta magiya wai dan Allah kifito hakuri sukazo baki da niman yafiyar ki."
rau-rau Nasiba tayi da ido ta ce "Ki ce wan da ya yi min fyad'e ni babu in da zan je yatafi bana ma son ganin fuskarsa."
SEEDRAH takuma rage murya ta ce
"Ki yi hakuri kizo wlh nayi ta musu kora da hali har nafito na ce musu bazan kirawo ki ba bakiga yan da suke ta rokona ba, shi kamma Mukhtar d'in bakiga yadda yake yi ba kamar zai zubda min kwalla."
kai Nasiba ta sunkuyar cike da d'acin rasa budurcin ta bata kuma yin magana ba.
SEEDRAH ta sunkuya ta shiga taya ta wanke-wanke dama saura kad'an ne ta gama, suna kammalawa Nasiba ta mike taje ta d'auko hijabinta taleka d'akin Mama Kubura ta ce da ita zata shiga gidan su SEEDRAH.
daga nan suka fito SEEDRAH na gaba Nasiba na biye da ita.
in da ta barsu nan suka iske su, tun kan su karaso gurin Mukhtar ya kafe Nasiba da ido yanajin zuciyarsa babu dad'i.
nan take yaji kunnuwansa sun amsa da ihu da magiyar da take masa lokacin da yake kokarin yimata fyad'e da kuma karanta mai tsananin karfi a lokacin da yashige ta yafasa budurcin ta.
rumtse idanunsa ya yi da karfi tare da kai hannunsa ya toshe kunnuwansa da karfi yana girgiza kansa tare da taune lab'b'ansa.
jiki a sanyaye Nasiba ta tsaya d'an gefe da SEEDRAH, Kamal ya kai hannu yana d'an bubbuga kafad'ar Mukhtar daya lura da halin da ya shiga ganin Nasiba, sai a lokacin ya bud'e idanunsa da suka kad'a sukayi jajir.
da sauri Nasiba ta juya zata bar gurin ganin fuskar mutumin daya keta mutuncinta.
da sauri Kamal ya ce
"Dan Allah kada ki tafi ki saurare mu ko da na mintuna biyu ne,
ki sani akwai masu yiwa y'ammata fyd'e su gudu ko da kuwa an neme su baza a same su ba, amma shi da kansa yakawo kansa domin ya nemi yafiyar ki kafin hukuncin da zai zartu a kansa, ki sani Allah yana son me yafiya idan kayafewa d'an uwan ka sai shima yagafarta maka."
cak ta tsaya yayin da hawaye ke zuba a idon ta,
Mukhtar da gaba d'aya jikin sa yagama yin sanyi ya jawo kafafun sa da kyar zuwa gaban ta ya zube guiwowinsa a kasa, tare da had'e hannayen sa biyu, murya a matukar raunace ya ce
"Dan Allah dan Annabin sa mai dubun daraja! ina mai rokon ki daki yafe min, ina mai nadama da da nasanin aikata miki haka, hakan ba halina bane dan ban tab'a ai katawa ba sharrin shaid'an ne, na roke ki kiyafe min daga nan kuma ki kaini in da zaki kaini aje a yanke min duk kan hukuncin daya da ce da ni, amma kafin nan ina mai rokon yafiyar ki."

Yadda yake maganar cikin rauni sosai ga hawaye nabin gefen fuskarsa namiji kamar shi da zuba goiwowinsa a kasa da kuka da magiya da roko.
yasa SEEDRAH jin jikinta ya yi sanyi, ta dafa kafad'ar Nasiba da ke hawaye ta dubi Mukhtar ta ce
"Ka tashi zata yafe maka in sha Allah amma dai ka cutar da rayuwarta kam."
kai ya jinjina ya ce "Na sani shi yasa nake son gyara kuskure na, idan ta amince zata aure ni nikuma a shirye nake nashare mata bakin cikin dana jefa rayuwar ta ciki."

wani irin d'agowa Nasiba tayi ta dube shi sai kuma ta juya da sauri had'e da sassarfa tanufi cikin gida, tana mai zubda hawaye masu zafi.........!

Mommyn Twins ce

🌺 *ƘARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna ƘARSASHI kada ku manta kafin zuwan ƘARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 KARSADHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciyar masoya salon labarin na daban ne. ko dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa ƘARSASHI! ƘARSASHI!! ƘARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta

wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08034690723_

*________________________________________*

*🌈🇰AINUWA 🇼RITER'S✍🏼*
*🅰SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*________________________________________*

🅿5

Da mamaki SEEDRAH ta ke kallon sa sannan ta ce
"Aure kuma?." kai ya gyad'a cike da tabbatar da gaskiyar sa.
Kamal ne ya dube ta ya ce "Ko bakya goyon bayan hakan ne?, Har idan ta amin ce shine hanya mafi sauki da zai bi ya rarrashi zuciyar ta."
baki ta tab'e a kasan ranta ta ce "D'an shishshigi watakila ma kai ka tsara  hakan ma." a fili kuwa ce wa tayi
"An tab'a auren da babu so bare kauna? bugu da kari kuma yanzu a kullace take da shi a zuciyarta ta ya ma hakan zai faru bayan shima ba son ta yake ba, kawai kuje ba lallai bane hakan ta yuwu."
da sauri Mukhtar ya ce "Ina son ta da gaske tun ranar dana yi mata fyad'e zuciyata takamu da son ta, son ta da damuwar abunda nayi mata sune suka had'u suke damuna, dan Allah ki tabbatar mata da ce wa zuciyata tana tare da ita."
Kamal ya ce
"Kwarai kuwa dan aboki na baya karya dan Allah ki shawo mana kanta."
hararar sa tayi kana ta juya ta soma tafiya ta na fad'in
"Amma ya iya mugunta ai."
wani sassanyan murmushi Kamal ya bita da shi yana shafa gefen fuskarsa ya yin da idanunsa ke kanta har ta shige gidan su Nasiba, sai sannan sukuma suka tafi.
```

A d'aki SEEDRAH ta iske Nasiba kwance a kan katifa tana kuka, ta zauna a gefen ta tare da dafa kafad'arta kana tayi saurin mai da hawayen da taji sun ciko mata ido tayi kokarin rarrashin kawar tata gudun kada ta kuma karyar mata da zuciya.
SEEDRAH ta ce "Naseeba kiyi hakuri nasan d'aci da kunar da kike ji a zuciyar ki amma ki sani auren Mukhtar shine kad'ai rufin asirin mu, tabbas naga son ki cikin idanun Mukhtar kibashi dama kawai."
mikewa Naseeba tayi zaune tare da share zafafan hawayen da suke zubo mata tarike hannun SEEDRAH cikin zubda kwalla  ta ce
"Ni ma hukuncin dana yankewa kaina kenan a yanzu haka na aminta da auren nasa,
dan nasan hakan ne kad'ai rufin asirina, dan babu wan da za'a kwashe masa ni a kaini gidansa ya iskeni sauran wani yazauna dani cikin aminci, shi d'in daya rusa katangar budurcina da shi zan rayu a haka ko da bana son sa."
kuka ne ya kwace mata takifa kanta a cinyar SEEDRAH tashiga rera sabon kuka.
duk dauriyar da SEEDRAH takeyi  kan kada tayi kuka tacigaba da karfafa mata guiwa sai da ta fashe ita ma da kukan suka cigaba da rera kukan tare.
jin motsin Mama Kubura a tsakar gida yasa su sassauta kukan nasu, SEEDRAH bata bar gidan ba har sai da taga zuciyar kawar tata yad'an sanyaya...

A b'angaren su Mukhtar kuwa  kullum sai sun zo unguwar su SEEDRAH watarana ta fito watarana taki fito wa,idan har kuma ta fito taje kira musu Naseeba bata yadda tafito haga zasu karaci tsayuwar su sutafi..
bayan sati biyu Mukhtar ne yakai kansa da kansa kotun musulunci dake nan cikin garin Kaduna, yakuma fad'i laifin daya aikata harya kai ga zuwa da kansa kotu dan a yanke masa hukuncin daya dace da shi a musulunce.
da fari alkalin yabukaci da azo da wacce yayi mata fyad'en Mukhtar d'in ya hana faruwan haka ta hanyar fad'in, shi bai ma san ta ba.
yayi hakan ne kuma badun komai ba sai dun kare martabar ta a idon duniya.
a take a gurin a ka yanke masa hukuncin bulalu kamar yadda addinin mu ya shar'anta, bakuma tare da tozarci ba, duba da irin namijin kokarin da yayi nakawo kansa da kansa domin a yanke masa hukunci, wanda a zamanin mu na yanzu ba kasafai ake samun masu tsoron Allah irin haka ba, su aikata laifi susan basuyi dai-dai ba har sukawo kansu gaban shari'a dan a yanke musu hukunci ba.
sab'anin da yanzu ma mutum zai aikata laifin gashi a bayyane a na gani kiri-kiri ya aikata ya kuma yi musu haka za'ayi ta tuka shari'a da shi karshe ma shari'ar tabi iska...

Bayan an gama yanke masa hukuncin yana kwance a kasa shame-shame yana sauke numfashi a jikkace. da kyar ya iya d'aga wayansa da tun zuwan sa kotun ya kashe, ya kunnata kana yakira Kamal da tun d'azu yake ta zaryar niman sa baigansa ba yakira wayansa kuma baya shiga.
Kamal na d'agawa ya ce "Mukhtar ina ka shiga ne tun d'azu nake ta kiran wayar ka baya shiga?."

ido Mukhtar ya rumtse jin yadda jikin sa ke masa rad'ad'i da mugun tsami ya ce
"Kazo ka taimaka min muje gida."
jin muryar sa hankali tashe Kamal ke tambayansa meke faruwa yana kuma ina?.
ya shaida masa inda yake, hankali a mugun tashe Kamal yanufo koton cike da tunanin abun da yakai Mukhtar d'in koto, dan Mukhtar bai fad'a masa zaizo kotu ba.
da tunanin ko iyayen Naseeba ne suka kaishi koton Kamal ya iso kotun.
ganin halin da abokin nasa yake ciki hankalin sa yakuma mummunar tashi.
da taimakon mahukuntan kotun Kamal ya iya d'aga Mukhtar da baya iya motsa ko da d'an yatsansa, suka d'aurashi a mashin.
direct asibiti yanufa da shi,
da fari a kaki karb'an shi a kace sai yazo da hukuma, sai da Kamal ya yi ta had'asu da Allah kafin suka karb'e shi suka shiga bashi taimakon gaggawa.
har yamma suna asibitin sai sanan Mukhtar ya farka daga baccin da ya ke, sakamakon alluran baccin da a ka masa.
Kamal ya matso bakin gadon da yake kwance cike da tausayi yana yi masa sannu, kana ya juya da sauri yana fad'in
"Bari naje na samo maka abun da zaka ci."
Mukhtar ya ce "A'a bana jin yunwa Maman Zeey fa tasan ina asibiti kuwa?."
shiru Kamal yad'anyi kana ya ce "Ni ma tunanin da nake tayi ke nan tun d'azu idan har ta ganka cikin wannan halin me za'a cemata."
ido yad'an rumtse tare da bud'e wa ya ce
"Ka fad'a mata ina asibiti itama tazo ta yanke min hukuncin daya dace da ni."
ya yi maganar yana mai taune lab'b'ansa cike da kunar zuciya.
Kamal ya girgiza kai tare da zaro wayarsa ya lalub'u lambar Maman Zeey.
bugu d'aya a na biyu ta d'a, bayan sun gaisa ya ce da ita suna asibiti da Mukhtar.
cikin matukar tashin hankali take tambayar sa abun da ya sami Mukhtar d'in, bata iya nutsar da zuciyarta bama taji amsar da zaibata ta ce masa wani asibitin?.
yafad'a mata sunan sa ta kashe wayar tare da d'aukar mayafinta da kud'i tayi waje.
Zeey tabi bayan ta da sauri tana tambayarta meke faruwa ta ce mata Mukhtar ne yake asibiti.
itama hankali tashe ta d'au mayafin ta tabi bayan mahaifiyar tasu, suka tsari napep suka nufi asibitin.

Ko da suka iso ganin halin da d'an nata yake ciki yasa Maman Zeey nufar gadon da yake kwance tana fad'in
"Me ya same ka haka Mukhtar b'arayi ne sukayi maka haka kokuma hatsari kayi?."
rumtse idanunsa ya yi da karfi yana mai cike da dana sani. tabbas baka da makiyi irin shaid'an idan kuma kabiyewa zuciya da shaid'an ke tunzura shi izuwa aikata sab'on Allah hakika kana cikin asara da tab'e wa had'e dajin kunyar duniya, idan baka hankalta ba kuwa har da ma kunyar lahira data fi ta duniya.
Maman Zeey ta ruko hannunsa tana cigaba da fad'in
"Mukhtar meya sameka haka!?."
tayi maganar hankali a matukar tashe kana ta juya ta dubi Kamal ta ce
"Kuyi min magana mana me ya same shi haka!?."

Zeey da itama hankalin ta ya mugun tashi ta ce
"Ya Mukhtar meya same ka haka?."
tayi magana hawaye na ciko mata ido.
sai sannan Mukhtar ya bud'e rinannun idanunsa ya zubawa mahaifiyar tasa kana yakankame hannun ta dake rike da nashi  sannan ya ce
"Maman Zeey kiyafe min kiyafe min dan Allah."
wasu zafafan k'walla ne suka zubo masa.
Kamal ya dubi Zeey da tuni hawaye ya soma zuba a fuskarta ya ce
"Ki d'an bamu guri zamuyi magana."
jiki a sanyaye taja kafafunta tayi waje.
hannun Maman Zeey
Mukhtar yakuma rike wa gam hawaye na wanke fuskarsa, gaba d'aya jikin ta yagama sanyi tana tunin wani irin babban abu ne yasami d'an nata haka.
cikin rawar murya Mukhtar yake fad'in
"Maman Zeey kema ki yanke min hukuncin daya dace da ni kamar yanda suma suka kayi min sannan kiyafe min."
cikin rashin fahimta ta ce
"Me kake fad'a ne kam mene ne? kayi min yan da zan gane wani irin hukunci a ka yanke maka haka me ka aikata haka akayi maka irin wannan mummunar hukuncin haka!."
"Fyad'e na aikata, hukuncin fyad'e a ka yi min ke ma kiyi min naki kuma dan Allah idan kika yi min ki yafe min."
wani irin waro ido Maman Zeey tayi tare da d'an ja da baya.
a hankali Kamal ya matso yashiga yi mata bayani cikin sanaki, yadda abun ya faru da zuwa gidan su Naseeba yanzu da suke akan niman aurenta da yake har zuwa yau dayakai kansa kotu a ka yanke masa hukunci.
hawaye tashiga sharewa kana ta matso taruko hannun Mukhtar ta ce
"Nayefe maka Allah ya yafe maka, duk da ina da tabbaci da yakinin yafiyar ubangiji a gare ka, tun da har kabi ta hanyar da zai yafe makan, Allah ya dad'a tsare ku da sharrin shaid'an me ingiza mutum izuwa ga halaka."
wani irin dad'i ne ya mamaye zuciyoyin su ganin yan da ta fahimce su cikin sauki...
kwanan Mukhtar biyu a asibitin a ka sallame shi,babu wan da yasan dalilin da yasa a ka kwantar da shi a asibiti ko 'yar uwarsa na jini wato Zeey har yau bata san dalilin kwanciyar nasa ba, ko ta tambayi dalilin sai dai ace mata hatsari yayi duk da kuwa shatin bulala da take gani a jikin sa sai dai bata kawo komai a ranta ba, a ranar kwanan sa na biyun a ka sallame sa.

A cikin satin manya suka shiga maganar auren shi da Naseeba, hamaifin Naseeba ya aminci da batun auren sakamakon kiran Naseeba da ya yi ya tambayeta tana sonsa bata da zab'in daya wuce Eh dan hakan ne kad'ai take ganin mafita cikin rayuwar ta da take wa kallon ragegge.
aka kuma sa aure wata biyu masu zuwa, har kuma yau babu wan da yasan da batun fyad'en da Mukhtar ya yi wa Naseeba in ban da Kamal da SEEDRAH sai kuma Maman Zeey kasan cewar mahaifin Mukhtar d'in baya raye 'yan uwan mahaifin su ne suka wuce gaba kan maganar auren, sai dai har yau Naseeba taki ta bawa Mukhtar da ma ko da sau d'aya ne su had'u. ko da sunzo kofar gidan su sai dai SEEDRAH ta fito, dan yanzu tafara rage jin haushin su tun da Kamal ya

bata labarin hukuncin da Mukhtar d'in yakai kansa a ka yanke masa....
yanzu shirye-shiryen biki SEEDRAH ta ke dan ita ke gudanar da tsare-tsaren bikin dan idan ta Naseeba ne ma kada a yi komai, ita dai a d'aura aure a kaita shine take ganin rufin asirin rayuwar ta.
bayan watanni biyu aka d'aura auren Naseeba da angonta Mukhtar, ta tare a cikin gidan su Mukhtar d'in a d'aya shashin dake bayan na Maman Zeey.
a ranar da yamma kowa ya watse yarage Naseeba da SEDDRAH sai kawarsu Nabila kasancewar gidanta babu nisa dana Naseeba'n. har wajen sallar isha suna tare da Naseeba a shashinta.
Nabila tayi ta zolayar Nasiba cikin zolayar da tun d'azu take ta mata ta ce
"Yau yarinya zaki gane shayi ruwa ne idan kika shiga hannun wannan bawan Allah'n, ba haka kukayi ta min dariya ba lokacin nawa,to ni yanzu anshani na warke har na saba yanzu babu wani ragowar zafi sai dad'i."
bugu SEEDRAH ta kai mata tana fad'in
"Allah ya shirye ki Nabila yanzu dai kin zama 'yar iska."
dariya ta yi ta ce
"Babu wani iskance ai gaskiya ce saura kema ki shigo hannu, ke kam nasan sai makota sun kawo miki d'auki sabo da tsabar tsoro irin naki."
"Allah ya sawake to ni anfad'a miki ma zanyi aure yanzu ne tun yayu na basuyi ba, kin san ai gidan mu bi da bi ne,sai Halimatu da Suhailat sun tashi kafin nan na kara girma babu katon gardin dazaici zalina."
SEEDRAH ta fad'a tana dariya.
Naseeba kuwa shiru tayi bata ce ko kala ba yayin da zuciyarta ke kuna, Nabila bata san komai game da fyad'en da akayi mata ba tana yi mata kallon wata cikakkiyar budurwace, k'walla ne suka ciko idon ta.
Nabila kuwa cigaba da fad'in
"Ko shekaru talatin zaki kai kafin kiyi aure ni na tabba a irin tsoron ki sai kin tara makota SEEDARH, yarin ya kiyi shiri yau fa zaki yabawa aya zakin ta, gobe da safe ina zuwa nakuma sake yi miki wani gashin dan nasan wanda zaiyi miki a darennan bazai wadatar ba sai an taimaka miki da safe."
ta karasa maganar tana duban Naseeba da tuni idanunta suka ciko da kwalla.
lura da yanayin da ta shiga yasa SEEDRAH girgiza mata kai ta dubi Nabila ta ce
"To tashi ki tafi gidan ki an fad'a miki kowa raguwa ce irin ki zuba ido kiyi kallo zakisha mamaki aure kuma ba yanzu ba."

"Sai yaushe? ni da nake saran a karshen watannan a ramawa kura aniyarta, yadda mukasha wuya a auren su haka kuma zasu rama mana."
cewar Kamal da yanzu shigowar su ya sinci cancen a sama yakuma cab'e. Mukhtar nabiye da shi suka shigo ciki.
SEEDRAH ta hararesa tare da murgud'a masa baki, dama taga take-taken sa tun ba yauba taki basa fuska ne.
shiko 'yar karamar dariya yayi yadubi Nabila yana fad'in
"Ko ya kikace kawar mu?."

dariya Nabila tayi ta ce "Wlh kuwa ina goyon baya d'ari bisa d'ari."
mikewa SEEDRAH tayi ta d'au gyalen ta da jakarta tana fad'in
"Sai kuyi kuma ai kanku a ke ji."
ta nufi kofa.
Kamal yabi bayan ta. Nabila ma ta mike tana dariya tayi musu sai da safe tayi waje.
a can waje ta iskesu suna ta dirama dariya tayi dan tasan halin SEEDRAH sarai bata kula samari tun suna makaranta ma irin samarin da ake nacikin aji ita bata sauraran su bare ma har ta tsaya zance da su, shi yasa da yawan samari suke ce mata wai tana da girman kai ko dun taga tana da kyau ne, kuma sam abun ba haka yake ba sai in kazauna da ita zaka fahimci halin ta sassanya kamar ruwan randa, ita dai haka rayuwarta yake da kin kula samari, a cewar ta wai bata kai na tsayuwa da saurayi ba sai idan yayun ta sun matsa sun bata guri..
Kabir mijin Nabila da yanzu ya iso gurin d'aukar matar sa shima yayi ta taya Kamal d'in kamfen, ita dai SEEDRAH bata saurare su ba har ya d'au matar sa sukayi gaba.
da kyar ta amince Kamal ya d'auke ta a mashin d'in sa, dan cewa tayi abin hawa zataje ta nima ya kaita gida bazata hau mashin d'in sa ba. a hanya yayi ta fallasa mata irin son da yake mata da ke kunshe a zuciyar sa tun ranar da kaddara ta had'asu.
ita dai tana jin sa suna isa kuwa ta sauka  ta shige gida ta barsa nan tsaye a kofar gida...

A b'angaren amarya da ango kuwa kamar yanda Mukhtar yasha alwashin samarwa zuciyar Naseeba salama da cire kiyayyarsa da kuma mantar da ita abun da ya faru cikin kwanakin da basufi bakwai ba.
ya samar wa zuciyarta nutsuwa had'e da tarin kwanciyar hankali da santsar kauna da soyayya da kulawar da yake nuna mata, ba shi kad'ai ba har da mahaifiyar sa da kuma kanwar sa.
a yanzu amarya Naseeba zamu iya cewa bata da wata matsala a rayuwar ta dan mijin ta yazame mata bango majingina, ga uwa uba kular mahaifiyar sa da kanwarsa gare ta.
cikin wata d'aya ta mance da wani mummunar abu yatab'a faruwa da ita, har take jin farin had'uwar su da shi shine yazamo first night d'in su kamar yanda Mukhtar d'in ya datsa mata jin hakan a zuciyarta.
sai dai muyi fatan d'aurewar farinciki ga wannan family....

A d'an wannan saikon kuwa Kamal ya sami nasarar sace zuciyar SEEDRAH amma fa sai da yasha wuya dan sai da yayi dagaske wajen iya sato zuciyar nata,
wani zazzafar sosaiya ce ke gudana sakanin su me cike da fahimtar juna.

SEEDRAH ce zaune tsakiyar d'akin Mama tana duba wasu litattafai, dan wata mai kamawa zata fara zuwa, Kasu open university, poly d.s, university Kaduna.
Mama ce ta shigo rike da flaks da laida a hannunta ta dire shi tsakiyar d'akin.
SEDDRAH ta ture littatrafan gefe tare da gyara zama ta mika hannu ta d'au cup tana fad'in
"Allah dama yunwa nake ji."

"Me ya hanaki tashi kinimi abincin."
cewar Mama tana zama gefen ta.
ta ce "Mama karatu nake kin san wani wata me kamawa Baba ya ce zan fara zuwa makaranta."
Mama ta ce "Uhm Allah ya nufa." kallon ta SEEDRAH tayi jin yanda ta amsa mata, sai kuma ta d'au flaks d'in ta tsiyaye ruwan zafi tafe da bud'e laidar, ido tad'an tsura cikin laidar ganin biredi da lipton da siga ne kad'ai a ciki.
ta ce "Mama ina sauran kayan tea d'in?."
baki Mama ta tab'e kana ta ce
"Sha abunda ya sauwaka ki godewa Allah hakan ma an samu, kijira samuwar na rana ma tukun dan bamuda tabbacin samun sa."
kai SEDDRAH ta jinjina kana tashiga had'a lipton da siga.

Alhaji Musa wato Baba ne tsaye cikin parlour'n sa, kallo d'aya zakayi masa kasan yana cikin muguwar damuwa da tashin hankali.
a yaune karshen yarjejeniyar su da banki kan bashin banki daya ci, tun shekarun baya da suka wuce, lokacin da aka kwashe masa kud'i na farko a accaunt d'in sa, hannun jarin sa yayi kasa sai da yaje yaci bashin banki kafin ya d'an farfad'o.
gashi yanzu ankuma yi masa mai gaba d'aya, duk kaddarorin da yake da su ya d'auka ya siyar yazuba kudin cikin asusun sa na banki wasu da baisan ko su waye ba suka kuma kwashe masa kud'i cikin account duka basu rage masa ko sisi ba.
gashi yayi sintirin banki har ya gaji ba'a gano wad'an da suke aikata masa hakan ba.
gashi yau banki ta nemesa kan kud'in ta daya ci, an kuma bashi wata guda yadawo da kud'in.
hankalin Alhaji Musa bai dad'a dugunzuma ba sai da yaga wata gudan da a ka bashi ya kare.
da sassafe tun bai tashi daga bacci ba yasami kira daga banki.
ko da yaje banki suke shai da masa sun sami masaniya kan yasai da kaddarorin sa daya ajiye musu a mazaunin jingina kafin su bashi bashi, suka kuma nuna b'acin ransu a kan hakan, sannan suka ce masa sun bashi awa ashirin da hud'u yadawo musu da kud'in daya karb'a, idan kuma ba haka ba zasu sa gidan sa da yake ciki da motar hawan sa a kasuwa yau kuma zai bar gidan.
cikin matukar tashin hankali yabaro bankin
da tunanin in da zai sami kud'i, bashi da su bashida dalilin su,abun da yayi masa saura daga gidan da yake ciki da iyalinsa sai motar da yake hawa, hatta abincin da zaici da iyalinsa nason fin karfin sa dan ma d'an'uwan sa na tallafa masa da abincin.
hankali tashe ya nufi gidan kanin sa Alhaji Sulaiman...........!

Mommyn Twins ce

🌺 *ƘARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin Iokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna ƘARSASHI kada ku manta kafin zuwan ƘARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin Iabarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 KARSADHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciyar masoya salon labarin na daban ne. ko dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa ƘARSASHI! ƘARSASHI!! ƘARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08034690723_

*______________________________________*

*🌈 K AINUWA W RITER'S✍🏼*

* 🅰SSOCIATION🤝*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*______________________________________*

🅿6

Ko da Alhaji musa ya isa a parlour'n kanin nasa suka yada zangon su, nan Baba yake shaidawa d'an uwan sa abun da ke faruwa. Alhaji Sulai
ya jinjina lamarin matuka. ya gyara zaman sa ya ce
"A gaskiya wad'an nan 'yan yawu d'in basu kyauta mana ba sakanin mu da su sai sakayyar Allah, wlh Yaya Musa duka-duka kud'ina da suke cikin account d'ina basu kai kud'in da banki suke bukata ba, kuma nasan tun da suka d'au zafi ba lallai bane su karb'i kad'an ba, amma dai muje ko Allah zai sa su karb'a su kara mana lokaci har Allah yasa mu samu a kaimusu sauran."
Baba yashiga yi masa godiya da irin rufin asirin da ya yi masa suka d'unguma zuwa banki, sai dai sukayi rashin sa'a banki sun d'au zafi sosai bisa karya musu yarjejeniyar da sukayi kan siyar da kaddarorin daya nuna musu a matsayin jingina.
suka ce bazasu karb'a kud'in da ya yi kasa da abunda suke binsa ba, haka suka baro bankin cike da matukar damuwa.
gidan Alhaji Sulai suka dawo da tunanin mafita, suna zaune sunyi jugum-jugum Abba wato Alhaji Sulai yad'an zaburo tare da d'aukar wayar sa da yake kara alamun shigowar kira.
ko da ya gamai kiran nasa zaman sa yagyara tare da d'aukar kiran ya kara a kunnen sa yana amsa sallamar da ake tacikin wayar.
daga cikin wayar akace
"Ina kwana Abba ya gida dasu Ummi?."
Abba ya ce "Lafiya lau sai dai mu yanzu rana ce ba safiya ba, ya harkokin dai?."
ya ce "Alhmdllh."
"To masha Allah Allah ya taimaka."
```

ya ce "Amin amma Abba yanaji muryar ka haka gidan lafiya dai ko?."
kai Abba ya girgiza cike da alhenin halin da suke ciki ya ce
"Gaskiya kam a kwai damuwa dan har nafara tunanin neman ka ma sai ga kiranka."
bayanin abun da ke faruwa yashiga zayyana masa, daga cikin wayar yad'an ja numfashi kana ya ce "To basai ya basu gidan da motar ba kawai yaje ya kama haya."
Abba ya ce "Gidan haya kuma Usman? da tarin iyalai ai gidan haya bazai yiwuba Allah dai ya kawo mana mafita kawai amma muna cikin damuwa."
"Amin." yafad'a a takaice tare da kashe wayar sa.
jugum su Baba sukayi kowa da kalar tunanin sa..

A can kasar Spain USMAN SULAIMAN inkiya S.MAN
kyakkywan saurayi ne ajin farko, yahad'a duk wani abun da cikakken namiji yake takama da shi, S.Man d'an kimanin shekaru 30 da 'yan d'ori, dogo ne me faffad'an kirji yana da haske sai dai ba can ba, yana da zubin karfafan maza zaratan maza.
juyi ya yi daga kwancan da yake a kan wata lafiyayyen gado,
yana kwance ruf da ciki kafafunsa suna ririto a kasa yayin da kafafun nasa suke sanye cikin takalmi sau ciki irin na 'yan kwallo.
yana sanye da kayan kwallo a jikin sa.
cikin rashin damuwa da halin da wan mahaifinsa yake ciki da yanzu Abba yagama sanar masa abun da ke faruwa, ya wurga wayar can gefe kana
ya mike tsaye.
yashige bathroom dan yanzu ya dawo daga gurin kwallo gaba d'aya a gajiye ya dawo.
bayan wasu mintuna yafito d'aure da farar towel a kugunsa yanufi gaban gado wayar sa ya d'auka tare da dannawa lambar Abba kira.
Abba da suke zaune har lokacin shi da Baba ya d'aga kiran tare da sallama.
cikin ko oho ya ce "Har yanzu zaman jiran mafita kuke?."
Abba ya ce "To ya zamuyi Usman yanzu a bun da nake tunani shine na had'a kan takardun kaddarorina muje bankin abasu idan kud'in bai kai ba in yaso sai a cire na accaunt d'ina nasan dai zasukai."
ya ce "No Abba hakan baiyi ba taya za a yi ka aikata hakan bayan nan gaba idan rai yayi halinsa kaddarorin namune, baka tunanin hakan zai haifar da matsala yau she kake ganin zai samu wad'annan kud'ad'en ya biya a ina ma zai samu tukun, bayan ya rigada ya dawo talaka."
Abba ya katse shi da fad'in
"Kai kasan gawan fari ne wato fatan mutuwa kake min ko? kanka d'aya kuwa Usman kasan me kake fad'a kuwa nafa fiskanci zaman kasar arnan nan nason mai daka wani iri, a shekaran nan zaka dawo kasar nan dan babu abun da zaman can ke tsinanawa sai rashin daraja, tun da ka kammala karatun ka kadawo gida imma kasuwancin ne a kasar mu ma anayi, idan aikin gwamnatin ne ma duk akwai a nan in kwallon ne ma duk anayi, idan ba ka kira ka bada taka gudumawar bane to ka kashe wayar ka."
baki S.Man ya tab'e tare da d'aga kafad'a cikin halin ko oho ya ce "To Abba ai dai gaskiya ce kuma ni ba fatan mutuwa nake maka ba,zan bashi aron kud'in idan yana bukata amma da sharad'in zai dawo min da kud'i na duk san da na duro Nigeria."

da sauri Abba ya ce "To..to...to ba damuwa turo..turo mana."
Abba ya juyo yana duban Baba cike da murnar samun mafita ya ce
"Yaya kaji ko Usman zai bada aron kud'in."
cikin murna mara misaltuwa Baba ya washe baki yana fad'in
"Kai masha Allah Allah yayi albarka Usman kai madallah ai to mutashi muje bankin sai ya turo a can." kuma tab'e baki
S.Man ya yi kana ya kashe wayar sa dan duk abin da yake fad'a yana ji..
cikin hanzari suka mike suka tafi banki, a can S.MAN yaturo musu kud'in direct bankin.
ranar Baba yasamu yayi bacci mai dad'i dan tun da banki suka sashi gaba baya iya bacci mai nisa...

SEEDRAH ce kwance tana manne da waya a kunnen ta suna waya da K'amal sai murmushi take sake wa tare da juyi a kan gado.
Suhailat da ta shigo yanzu ta zuba mata ido tare da rike hab'a tana fad'in
"Ikon Allah wacce take cewa a na damin ta da surutu yana hanata bacci idan ana waya itace manne da waya a kunne?, to nima kada a hanani bacci dan nima bacci zanyi."
tayi maganar tana zama bakin gado.
dariya SEEDRAH ta yi ta ce
"Kai Aunty Suhailat ke dai kiyi baccin ki bazan dame ki ba."
daga cikin wayar K'amal da ke jin su yasaki dariya tare da fad'in
"Ah to a she haka kike fad'a musu itama ta rama kenan, Aunty Suhailat koreta taje waje."
murmushi ta yi me sauti ta ce "Sai na kashe wayata tun da a sanyin nan kake ce a kore ni naje waje."
murya ya d'an rage dan yasan halin SEEDRAH sarai zata iya kashe wayar ta barsa cikin bege da tunanin ta.
ya ce "Sorry Baby a d'aki ma sanyin nan bai barka ba na isa a kora min ke waje,
kin gan ni nan lullub'e da bargo amma sanyi nake ji ke bakya jin sanyin nan?."
"Ina ji mana nima a rufe nake yanzu."
numfashi yad'an ja tare da kuma rage muryar sa ya ce
"Alhajina yayi tafi zai dawo jibi gata zai zo yasami Baba ayi-ayi magana dan gaskiya wannan sanyin yana bukatar ainahin bargo ne, idan kina cikin jikina bazanji sanyin ba kema haka."
da sauri ta kifa fuskarta jikin pillow cike da jin kunyar maganar tasa.
murmushi ya yi ya ce "Bakice komai ba."
dad'a cusa fuskarta tayi batare da ta ce komai ba.
sanin bazata ce koman ba ya ce "Yaushe zaki fara zuwa makarantar?."
ta ce "Ranar monday."
ya ce "Ni dai in da za'a bi tanawa da an aje batun makarantar nan tukun ayi maganar auren mu dan bana son batun makarantar ya saida maganar auren nan,idan aka kawo min ke ni da kai na zan rika kai kaya ta makaranta, dan Allah kiyi wani abu yanzu kam hakuri na yafara karewa ina bukatar ki kusa da ni."
a hankali ta ce

"To ni me zanyi a kai?."
ya ce "Ki aje batun makarantar tukun idan akayi auren sai ki fara zuwa."
ta ce "Ina son makarantar nan fa kuma ai shi bazai hana komai ba."
ya ce "To shi kenan amma fa ki sani idan ki kazo sai kinyi wata uku kafin ki koma makaranta dan sai na ci angwanci na sosai."
hirar su suka cigaba da yi, har Halimatu itama ta shigo kwanciya ta haye karifar tana fad'in
"Mun shige su SEEDRAH sabon shiga har yanzu wayan kike kanyi?."
dariya ta mata ta juya musu baya suka cigaba da hirarsu...

Yau Monday hakan kuwa yayi dai-dai da ranar da SEEDRAH zata fara zuwa makaranta, da ke tasa ranta a tafiyar ko baccin asuba bata koma ba, gudun ma kada ta kwanta baccin ta mai nauyin nan yasata makara.
tana gama shiri ta fito daga d'akin su ta nufi d'akin Mama.
tasha lipton da biredi tayiwa Mama sallama ta fita.
parlour'n Baba ta shiga da sallama yana zaune yana kallon labaren safiya a TV. ta sunkuya ta gaishe shi tare da fad'in
"Baba nagama shiri zan shiga makaranta."
ya ce "To madallah Allah ya taimaka ya bada sa'a a kula sosai."
ya zaro d'ari biyar a aljuhunsa wan da dashi kad'ai ya kwana ya mika mata ya ce tayi kud'in mota. ta karb'a tare da yin godiya ta fita.
ta isa Kasu, open university, poly d.s Kaduna state.
taji dad'in makarantar ba kad'an ba,har kawa tayi yau wata wacce tayi ta shige mata duk da ita SEEDRAH bata wani saki jiki da ita ba, samari kuwa sunyi ta kawo hari dan SEEDRAH Allah ya hore mata farinjini ga tsarin zubin hallitta.
da misalin karfe 2 da rabi tsaye take a bakin get d'in makarantar, tana tunanin ta yadda zatayi ta koma gida dan d'ari biyar d'in da Baba ya bata saura d'ari da hamsin ne ga wani masifaffen yunwan da take ji.
dan tun lipton d'in da ta sha da safe shine a cikin ta har yanzu.
idonta ta lumshe tare da d'an matse shi jin yunwan nadad'a fisgarta.
a hankali ta bud'e idanunta jin magana kusa da ita. ta sauke idanunta kan wata motar dake gaban ta, matashi ne zaune cikin motar ya leko ta jikin windon motar yana fad'in
"Ya ne 'yanmata tsayuwa a rana ba irin taku bace wannan tsadedden surar sassanyan inuwa da ac ne ya kama ta dashi,taya abun da baka saba da shi ba lokaci guda ka ce zaka yi shi, shi yasa kike rufe ido baki saba da rana ba, in babu damuwa shigo na sauke ki gida."
kai ta kawar gefe a takaice ta ce "Nagode."
taja kafafun ta tamasa can gefe.
hon taji a bayanta taki juyowa zaton ta saurayin nan ne, jin an kuma dan na mata hon yasata juyowa a fusace dan ya gama cikata ga yunwa ga shi bata sami abun hawa ba ga kud'in hannun nata ma ba lallai bane ya kaita sai dai in taje gida ta nima cuko, cikin masifa ta bud'i baki zatayi magana sai ganin K'amal tayi yana kuma kokarin dannan mata hon d'in.
baki ta turo gaba tare da kwab'e fuska cikin muryar shagwab'a had'e da yunwa ga kuma gajiya ta ce
"Da ma kai ne? Allah na d'auka wani ne."

dariya ya yi ya ce "Wai a ina kika aje wayar ki nake ta kira baki d'aga ba? shine tafiya makarantar babu sanarwa sai da naji gida ake fad'a min."
kai ta langwab'ar gefe ta ce
"Ayya wayar ma mancewa da ita a gida nayi."
"Sabo da ana sauri ayi azo makaranta ko? ni gashi yau d'aya ma har naga kin rame min, zo mu tafi."
gyarawa tayi ta haye mashin d'in ta na fad'in
"Rama kuma? na dai san ina jin yunwa."
ido ya waro ya ce "Haka ake yi a haka zakiyi karatun babu tsayuwa cin abinci babu zuwa da abincin makaranta?, to ni gaskiya ban yarda ki rika wahalar min da kanki ba."
baki ta washe ta ce "Zuwa da abinci sai kace 'yar Naziri."
ya ce "To ai kusan haka ne nifa ina tunanin ma tsalle kikayi a Secondary dan 'yar kamar kin nan baici a ce har kin gama
Secondary ba."
baki ta murgud'a ta ce "To ko sau d'aya ban tab'a sallaken ajiba tun ina da shekaru uku nake zuwa makaranta sai kayi lissafi."
dariya ya yi hango yanda ta murgud'a masa baki ta cikin mirro ya ce
"Oh haka ne fa shekarun zasu iya kaiwa 16 ke nan."
hararar wasa had'e da murmushi tayi masa
tana fad'in "To nafi haka."
dariya ya yi ya ce "Da d'aya ba in ma kin kai 17 d'in ke nan."
ko da suka iso gida lura da yanda take nannarkewa yasan tana jin yunwar sosai ya ce ta shiga gida zai dawo da daddare..
tana shiga a parlour'n Mama ta wurga jakarta ta fito sakar gida da sauri.
nan ta tadda mutan gidan kowa ya nad'e hannu gaishe su tayi kana ta nufi kitchen da sauri tana fad'in
"Ko sallah bazan iya ba sai naci abinci."
Mama ta ce "Idan kika samu abincin ki kawo mana muma zamu ci."
turus tayi tana kallon Mama fuska a marairaice ta ce
"Mama ba'ayi abincin bane?."
kai Mama ta kawar Umma ce tayi magana
"SEEDRAH duk muma yunwan muke ji har yanzu jiran Baban ku muke babu ko kwayar hatsin da za'a girka a gidan nan."
ji tayi yunwar da take ji gaba d'aya ya d'auke jiki a sanyaye ta dawo da baya.
ido ta zubawa kannen ta Walida da Walid da suke rab'e jikin Umma ga dukkan alamu wutar yunwa ce ke azalzalarsu.
da hannu ta kirasu suka mike tayi d'akin Mama suka bi bayan ta, jakar ta ta d'auka ta ciro d'ari da hamsin canjin da ta dawo da shi ta mika musu ta ce
"Kuje ku shago ku siyo garin kwaki kuzo ku sha."
ai ko da gudu yaran sukayi waje..

Zubewa tayi saman kujera tare da sauke numfashi, yayin data lula duniyar tunani.
lallai Allah ya jarafce su jarafta mafi girma, wai yau gidan su ne a ka tashi babu abincin da za'a

ci.
wan da a da sukafi karfin komai sai gashi dare d'aya Allah yayi wa mahaifin su kariyar arziki.
numfashi taja tare da saukewa a fili ta furta "Allah kakawo mana mafita."
daga cikin gida tajiyo sallama jin muryar mai sallamar yasa ta mikewa tafita, ganin babbar yayan su ce Hajara yasata fad'ad'a fuskarta da murmushi.
Hajara itace babba duka a gidan itace 'yar farin Umma sai Suhailt da Halimatu, sai Walida da Walid sukuma tagwaye ne shekarunsu 6 kenan.
Mama kuma 'ya d'aya Allah ya azirta ta da shi wato SEEDRAH ta dad'e kafin ta same ta daga kanta kuma bata sake haihuwa ba.
Suhailat da Halimatu duk sun girmewa SEEDRAH shekarun Suhailat 25 Halimatu kuma 23 har yanzu Allah bai kawo musu mijin aure ba suna dai kan tab'a boko.
SEEDRAH kuma shekarun ta 17 ne yanzu.
babu laifi family'n suna zaman lafiya sai dai d'an abunda ba'a rasa ba.
wannan kenan...

"Oyoyo Aunty Hajara." cewar SEEDRAH tana rungume ta.
murmushi Hajara tayi itama tana fad'in oyoyo. a sakar gida in da su Umma suke zaune ta zauna suka fara gaisawa, Halimatu da Suhailat suka fito bayan sun gaishe ta suka zauna aka cigaba da hira.
hankalin Hajara yayi matukar tashi jin yau babu kwayar abincin da za'a girka a gidan nasu.
ga Baba tun da ya fita bai waiwayo gidan ba bare a sa ran samun wani abun daga gare shi.
'yan kud'ad'en cikin jakarta ta curo naira dubu biyar a ka siya shinkafa aka kuma yi cefane nan 'yammatan gidan suka d'aura girki, shi suka ci har dare.
har dare Hajara ta kai a gidan kafin ta koma gida, ta shiga tunanin ta yanda zatayi ta taimakawa mahaifan nata gashi mijin ta ba wani me karfi bane.
d'an abincin da ya ajiye musu ta d'an sassakura ta aika da shi gida, sukuma sukarika manaje idan akayi abincin rana baza'ayi na dare ba.
Baba kam dai yana zaune dan bashi da hanyar da zai nimo suci, abun da Hajara ta kalato da kuma wan da Abba ya d'an aiko musu da shi shi suke amfani da shi.
nan fa karatun SEDDRAH ya fara tangad'i dan kud'in abun hawan da zata hau taje makarantar ma aiki ne.
wani sa'in ta kira K'amal yazo ya kaita ida an tashi yaje ya d'auko ta, wani sa'in kuma taji nauyin kiransa haka zata zauna a gida.
dan dole su Mama suka mike kowa ta nimi sana'ar yi a gida domin rufawa kansu asiri.
a cikin wannan matsatsin da suke ne Abba ya bawa Baba naira dubu d'ari biyar ya ce yafara wata sana'ar in da zai samu yarika ciyar da iyalen sa...

Bayan wani lokaci ranar wata juma'a dawowar SEEDRAH daga makaranta kenan, ta tadda Mama kwance numfashin ta sai sama da kasa yake.
hankali tashe tayi kanta tashiga girgiza ta tana fad'in
"Mama ciwon ki ne sannu bakisha maganin ki ba?, bari na kawo miki kisha."
da kyar Mama ta iya bud'e baki ta ce

"Maganin sun kare." hankali tashe SEEDRAH tayi waje tana fad'in
"Bari naje na fad'awa Baba."
ko da taje d'akin shi baya nan sai yanzu ta tuna shigowar ta bata ga motar sa bama a cikin get yafita kasuwa kenan.
a rikice ta dawo d'akin, ganin halin da mahaifiyar ta take dad'a shiga yakuma birkitata.
tsawon shekaru 17 kenan take fama da mugun ciwon hawan jini tun bayan haihuwar SEEDRAH.
cikin bedroom ta shige da sauri ta shiga dube-dube a kasan pillow ta sami kud'i ta had'a kan 'yan canji duka naira dubu d'aya, takardan maganin Mama ta d'auka da sauri had'e da sassarfa tayi waje tana fad'in
"Sannu Mama yanzu zan kawo miki maganin kisha."

Tafiya take ko kallon gaban ta batayi, burin ta kawai ta ganta gaban shagon magani.
gashi shagunan maganin unguwar su duk kanana ne basa sai da irin maganin Mama, dole sai ta tafi har babban titi.
kamar zata tashi sama haka take sharar sauri,har ta iso daf da babban titi tana kokarin sallakawa.
hon d'in da ya karad'e kunnuwan ta ne ya dawo da ita cikin nutsuwar ta, ta d'ago kanta da sauri.
sai lokacin ta lura da gosulon daya cike titin had'e da hayaniyar mutane.
gefe guda kuwa daga can gaban titin sautin kid'a ne mai had'e da taken Nigeria ke tashi, tsakiyar titin kuwa matasa ne had'e da motoci tam kan titin, matasan sai rawa da hele suke.
ko wannen su rike da tutar Nigeria.
idanunta ne ya sauka kan wata mota dake tsakiyar motocin matasa na zazzaune a kan motar ko wannen su na sanye da riga kalar tambarin tutar Nigeri yayin da suka sanya wani dake rike da kofin kwallo na zinari a tsakiya, ya d'aga kofin sama.
daga gefe kuwa polisawa ne suke ta faman bud'e gosulo d'in...

Kai ta saka da sauri da zummar fasa cikin mutanen ta wuce dan sai ta ketare titi kafin ta sami shagon magani.
cikin tsawa taji ance mata
"Ke ina zakije a nan, ki tsaya sai mai k'asa ya wuce kafin ki wuce!."
da sauri ta juyo in da maganar ke fita sai taga daga cikin matasan da suke zazzaune kan motar nan ne wani yayi maganar.
daga cikin su wani ya kuma yi mata hannu alamar ta koma da baya.
wani irin kallo ta wasa musu mai cike da kunar rai tuno yanda ta baro mahaifiyar ta cikin mawuyacin hali,cikin dakewar zuciya ta wasa musu harara dukansu kana ta ce
"Me k'asa a she shi ya halitto k'asar ma, bai san darajar uwa bace tana can kwance cikin mawuyacin hali, sabo da baku da imani da tausayi."
da sauri ta saka kai dan gani take tsayuwar ta a gun ma b'ata lokaci ne...........!

Mommyn Twins ce

🌺 *ƘARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna ƘARSASHI kada ku manta kafin zuwan ƘARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 ƘARSADHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciyar masoya salon labarin na daban ne. ko dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa ƘARSASHI! ƘARSASHI!! ƘARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08034690734_

*______________________________________*

*🌈 🇰 AINUWA 🇼 RITER'S✍🏼*
*🅰 SSOCIATION🤝🏻*

```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*______________________________________*

🅿️7

Kokarin kuma dakatar da ita sukayi, wan da yake sakiyar su rike da kofin kwallo na zinari ya dakatar da su ta hanyar d'aga musu hannu alamar su rabu da ita.
da sauri tarika fasawa cikin tarin jama'ar nan ta sallake titi.
wani shago
dake nan ketaren titin ta shiga, sai dai babu kowa cikin shagon.
waige-waige ta shiga yi tana duba mai shagon amma baya ciki ko yaran shagon ma basa nan.
can ta hango shi tsaye ta waje yana aikin d'aukar mutanen nan a waya. cikin hanzari ta zo in da yake ta ce
"Malam kazo ka bani magani kabar gurin sana'ar ka kazo kallon wad'an can marasa aikin yi d'innan."
ido ya waro ya ce "Ke sune marasa aikin yi d'in?, to wlh a kansu sai na iya kulle shagonan muje mu cashe a babban filin taro, da daddare karfe takwas ma duk wan da yazo shagon nan ba sami na zaiyi ba muna can muna murnar nasarar da d'an Nigeria kuma d'an jahata Kaduna ya buga kwallon duniya ya ciyowa kasar mu Nigeria a kwallon duniya baki d'aya,
to bari kiji wannan taron da za'ayi gomna da shugaban kasa ne suka shirya, to ki dai na yi musu kallon marasa aikin yi."
baki ta tab'e dan ita bata masan meye ma'anar wani kwallo ba dan ita gani ma take masu buga kwallo marasa aikin yi ne kuma wahalallu,suje suyi ta gudu duk su had'a zufa wani ma har ya karye, in ba rashin aikin yi ba meye wannan.
ta ce "Ni dai muje ka bani magani ciwon Mamana ya tashi daga nan sai ka tafi gurin taron in kaje ka kwana a gun."
k'arb'ar takardar maganin da kud'in yayi, ya shiga shagon ya d'auko mata ko da ya kirga kud'in ya dube ta ya ce
"Ya naga dubu d'aya? maganin dubu uku da d'ari biyar."
```

fuska ta marairaice ta ce
"Dan Allah kayi hakuri ka bani maganin zan kawo maka cikon idan Baban mu ya dawo yanzu baya nan ne kuma wlh bata jin dad'i sosai."
ta karashe maganar kamar zata zubda kwalla.
kasan cewar ya santa dan kusan a nan shagon nasa suke siyan maganin duk san da ya kare, ya ce to taje anjima takawo masa cukon. ta karb'a tare da yi masa godiya ta fita ta juya gida da sauri.
ta can bayan motocin  da har yanzu suke cike kan titin ta wuce.

Tana isa gida ta sami Mama har lokacin a kwance, ruwa ta d'ibo ta b'are maganin ta zauna gefen ta tad'an tallafo kanta tasaka mata maganin a baki tare da ruwan ta sha.
cikin kankanin lokaci bacci ya d'auke ta.
numfashi SEEDRAH ta sauke tana kallon fuskar Mama da take bacci,
kwallan daya ciko idanunta ne suka zubo yayin da ta fara zancen zuci
"Allah sarki uwata a sanadin haihuwa ta kika samo wannan ciwon gashi har yau kina fama da shi in sha Allah kamar yanda kika samo sa a ta sanadiyya ta zaki warke a sanadiyya ta da yardar Allah."
ta mike tashiga kimsa musu d'akin da yau Mama bata sami da mar gyara shi ba sabo da ciwon ta...
Mama ta jima tana baccin sai wajen bayan la'asar kafin ta farka, zuwa lokacin kam alhmdllh taji d'an karfin jikinta.
ko da Baba ya dawo SEEDRAH taje ta amso sauran cikiton kud'in mai magani har da dubu d'ayan Mama da ta d'auka kasan pillon ta tamaida mata kana ta wuce ta kaima mai magani cikon kud'in sa...

Washegari ranar asabar tun da safe su Suhailt ke ta shiri, ansha wanka an d'au kwalliya, Halimatu na tsaye gaban mirro sai faman feshe jiki da turare take.
SEEDRAH kam na kwance tana ta sharar baccin ta.
Suhailat ce ta matso bakin gadon tashiga bubbugata, mika tayi had'e da salati tayi juyi nata kokarin kuma komawa baccin ta.
Suhailat ta kuma bubbugata da karfi tana fad'in
"Wai nikam ke bakya gajiya da bacci ne wai duk surutun da za a yi ta yi a kanki idan kina bacci bakya ji ne?
yanzu fa karfe 11 har da rabi amma wai mutum na bacci wai bai gaji ba."
cikin magagin bacci yayin da idanun ta suke rufe ta ce
"To ni me zan miki Aunty Suhailat Allah ni baccin bai ishe ni ba."
ganin tana kuma kokarin komawa baccin duk uban bugun da tayi ta mata ta ce
"To da ma ke bacci na isan ki ne dalla tashi ko bazakije gidan Abba'n bane?."
tuni SEEDRAH kam ta koma baccin ta bata ma san abun da take fad'a ba.
Halimatu dake gyara gyalen data yafa ta ce
"Da ma kin rabu da ita dan ba jin ki take ba, in ba d'aukarta zakiyi ki tsunbulata cikin ruwan Fridge me sanyi ba, a duniyar nan bantab'a ganin mutum me mugun nauyin bacci irin na

yarinyar nan ba."
fita sukayi suka rabu da ita, ita ko batama san sunayi ba.
SEEDRAH tana da nauyin bacci sosai sai aci a sud'e tana gurin tana aikin bacci batama san me ake ba, sanin nauyin baccin ta yasa duk ranar makaranta bata yarda ta koma bacci da asuba.
ai kuwa bata farka ba sai wajajen karfe 12 da rabi.
bayi ta fad'a tayi burosh tare da wanka ta d'auro al'wala dan lokacin anfara kiraye-kirayen sallar azaha.
sai da ta gabatar da salla kafin ta shirya cikin riga da siket na atamfa, ita ba wata ma'abociyar fente fuska da kulliya ba ce, pauda da man lips kad'ai ta shafa sai turare da ta bi jikin ta da shi, amma tayi kyau sosai abinka da me kyau.
d'akin Mama ta tafi ta same ta zaune a kan sallaya, zama tayi gefen ta ta ce
"Mama ya jiki?."
"Naji sauki SEEDRAH." ta ce "Allah ya kara miki lafiya."
Mama ta amsa da amin, kana ta mike taje ta had'a ruwan zafi da lipton ta yanko biredi ta dawo kusa da Mama ta zauna tana sha suna d'an tab'a hira..
da karfe biyu SEEDRAH tayi shirin islamiyya sai wajen karfe biyar da rabi ta dawo gidan.

Sai yamma su Suhailat suka dawo SEEDRAH na zaune a d'akin su tana duba littattafan ta suka shigo,
Halimatu ta zube bakin gado Suhailat kuma ta wuce bayi.
SEEDRAH ta dubi Halimatu ta ce
"Aunty Halimatu ina kuka fito ne?."
da mamaki ta ce "Au bakima san in da mukaje ba?."
Suhailat da ta fito daga bayi ta ce
"Ina kuwa zata sani mutum kamar bugagge idan ya fara bacci,
ke da nayi ta tashin ki kitashi munje gidan Abba mu karb'o tsaraba kika ki tashi."
littafin hannun ta ta rufe ta ce
"Karb'o tsaraba kuma wa yayi tafiya ya dawo?."
murmushi Suhailat tayi tare da fad'in
"Ya S.MAN ne ya dawo gashi ma bamu had'u ba duk zaman da mukayi a gidan yana can abokan sa sun had'a masa shagali na musamnan."
Halimatu ta ce "Wlh ni na masu naga yanda ya koma naji ance yakara kyau  ya canza gaba d'aya."
ido SEEDRAH ta bisu da shi sai yanzu ta fahimci wanda suke nufin wato Usman babban d'an Abba mazaunin kasar Spain, tana dai jin sunan sa amma sam bata san shi ba dan tun tana 'yar karama yabar kasar nan, kuma ba wani zuwa yake ba, da girman ta dai zata iya tunawa sau d'aya ta sami labarin ya zo lokacin ma bata Kaduna taje Zariya wajen kakarta mahaifiyar Mama.
maganar Suhailat ce ya katse mata tunani jin tana fad'i
"Ai wlh sai ma kin ganshi ranar dana je gidan Abba na samu suna video call da Ummi ke kin gansa kuwa hmm abun ba'a cewa komai, girman sa ya karu daya ciwo wa Nigeria kwallo."
SEEDRAH kam da ido ta bisu jin yadda suka dage suna ta zuzuta shi, baki ta tab'e dan ita bata ma sanshi ba bare ya dame ta.
wayar ta dake tsuwa ta d'auka ganin Kamal ne ke kiran nata ta saki wani lallausan murmushi

kana ta mike tayi waje, ta barsu nan suna cigaba da hiran S.MAN...

Washegari da safe su Halimatu suka kuma shirin zuwa gidan Abba, yau kam SEEDRAH bata koma bacci ba dan yau tun kan gari yayi haske ta kwashi wankin ta da na Mama tayi.
ko da suka gama shirin duban ta Suhailat tayi ta ce
"Ki tashi muje ko baccin naki zaki soma?."
mikewa tayi taje ta d'au gyalenta kasancewar a shirye take dan tana gama wankin ta yi wanka ta shirya cikin doguwar rigar les, ta yafa gyalen a kanta suka fito.
sai da ta shiga d'akin Mama ta fad'a mata in da zasu kafin ta fito.
suna fita suka tari a napep suka nufi gidan Abba.
suna isa Suhailat ta biya mai a dai-dai ta suka shige gidan, da sallama suka shiga parlour'n Ummi da Yusrah dake zau cikin parlour'n suka amsa musu.
suka karaso ciki tare da gaishe da Ummi, Ummi ta ce
"A'a tun baku zauna ba ku zauna mana."
suka zauna suna mai ci gaba da gaishe ta.
ta amsa cikin sakin fuska tana tambayar su ya iyayen nasu, sukace suna gaishe ta.
Yusrah ta gaida su Suhailat dan sune gaba da ita, mike wa tayi ta zo
kusa da SEEDRAH ta zauna tare da buga cinyarta ta ce
"Na gai da yayu na ke bazaki gaishe ni bane?."
hararar ta SEEDRAH tayi ta ce "Kin raina ni fa a kan ni d'in ban girme ki bane."
baki Yusrah ta rike ta ce "Ko kunya bakiji ba, ke d'in ce kika girme ni? amma yarinyar nan kin rainani."
murmushi Ummi ta bisu da shi a ko da yaushe idan suka had'u burin kowaccen su dai ta ce itace gaba da 'yar'uwar ta,
SEEDRAH da Yusrah sa'anni ne sakanin su baifi tazaran watanni ba.

Suhailat da tun shigowar su parlour'n ta kafe katon hoton S.Man dake like jikin bangon parlour'n, yana sanye da kayan kwallo yad'an sunkuyo yana dafe da kwallo yayin da ya d'aura kafar sa d'aya kan kwallon.
ainihin kyansa da suffarsa na zaratan maza ya bayyano sosai cikin hoton S
Man Handsome ne na karshe.
sosai ta shagalta da kallon hoton da take jin sa har cikin jinin jikin ta,
Suhailat
tana mugun son S.Man hakan kuwa yana daga cikin abin da ya hanata fidda gwani tayi aure.
a b'angaren Halimatu ma kuwa haka abun yake sai dai ita takan iya b'oye son da take masan amma acan kasan ranta soyayarsa ce zaune cikin sa, takan b'oye ne sabo da 'yar'uwan ta da take bayyana son da ita take masa a ko ina wan da shi baima san sunayi ba.
ganin kallon hoton nasa bazai wadatar da ita ba sai ta d'an muskuta tare da duban Yusrah da suke hira da SEEDRAH ta ce
"Yusrah Ya S.Man fa Allah dai yasa yana gida yau muyi masa sannu da hanya."
Ummi ta ce
"Ai kuwa yau idan da baku same shi ba zan ce ku huta abinku da jigilen hanya, yana nan amma

ina ga bacci yake bai tashi ba dan jiya sai wajen 1 na dare ya shigo gidan nan."
murmushi Suhailat tayi tare da fad'in
"Yana huta gajiya kenan ya kamata kam ya huta."
ji tayi kamar ta tashi taje d'akinsa ta iske shi can.
magana ta somayi a kasan ranta
"Tausa ya kamace ka tun daren jiya zuwa yau ka huta da kyau."
murmushi ta sake a fili.

SEEDRAH kuwa hirar su suke kan lokacin da sukayi candy d'in su, suka shiga kallon hotunan Graduating d'in su a wayar Yusrah
dan Secondary school d'aya sukayi.
Yusrah ce ta kece da dari ganin wani hoton su da SEEDRAH ta zazzaro manyan idanunta ta ce
"Dan Allah dubi ido kina kallon me hoto kamar kin ga dodo."
SEEDRAH ta ce "Amma dai me hoton nan ya cuceni dubi yan da yamin da ido,ko ma dai wayar ki ce badaga gunsa bane."
cikin muryar dariya Yusrah ta ce
"Wlh kada kima wayata sharri ke kika zazzare idanunki kamar baki tab'a d'aukar hoto ba, ai akwai asalin hoton da aka wanke yana nan a d'aki na zo ki gani zaki san ba wayata ke sharri ba."
suka mike suna dariya suka shige d'akin Yusrah.
nan ta d'ebo musu hotunan suna kallo sunayi wa yuna tsiya.
daga can parlour SSEDRAH ta jiyo ring d'in wayar ta da ta bari can parlour, jin sauti na musamman tasan wake kiran nata wato Kamal dan shi kad'ai ta sakawa sautin.
mikewa tayi tana fad'in
"Ina zuwa." tafito parlour'n, kafin ta isa in da wayar take kiran ya yanke.
ta d'au wayar tana kokarin juyawa ta koma d'akin Yusrah tajiyo Ummi da ke waya tana fad'in
"Da dai ka fito kayi break d'in a parlour gashi anzo gaisheka a na jiran ka tun d'azu."
daga cikin wayar S.Man ya ce "Ummi ki bada a kawo min breakfast d'in d'aki kawai idan nagama zan fito ko wanka banyi ba har yanzu gajiyar bata sake ni ba."
Ummi ta ce "To bari a kawo maka."
ta sauke wayar tare da
dakatar da SEEDRAH data d'sura hannu kan handle zata bud'e kofar Yusrah ta ce
"Zo SEEDRAH ki kaiwa yayan ku abin karyawan shi d'aki."
da sauri Suhailat ta ce "Bari na kai masa."
murmushi Ummi tayi tace "A'a barshi ita ta kaimasa ga kannen ku suna guri su sai suyi dad'in girman kenan, zo ki kai masa ga abincin nashi can kan dinning."
yuwayo tayi a sannu ta taka zuwa dinning ta d'au tray d'in da aka shirya masa breakfast d'in ciki, d'an dim tayi tsaye a gurin dan bata san ta ina ne d'akin sa ba, duk zuwan ta da take gidan daga d'akin Yusrah sai na Ummi sai kuma na Abba kawai ta sani.
ganin ta tsaye a gurin yasa Ummi fad'in
"Kai masa mana yan zu wannan sarkin mitar zai fara korafin ba'a kai masa da wuri ba, bi ta kofar kitchen ki kai masa."
a hankali ta nufi kofar kitchen d'in bawai kodun ta san daga nan sai ina zatayi ba.

sai da ta isa kitchen d'in taga kofofi guda biyu d'aya dai tasan store ne d'ayan ne dai bata san ko menaye bane dan SEEDRAH ba mutum bace me shiga lamarin da bai shafeta ba, gashi dai gidan kanin Baban ta ne uwad'aya uba d'aya amma ko da tazo gidan bata fiye shishshige ba abin da yakawo ta kad'ai take yi.
d'aya kofan ta bud'e sai taga ashe hanya ce da zai fiddaka waje ta baya, can ta hangi wani d'an ma dai-dai cin side da tuntuni take masa kallon side d'in bak'i ne.
kofar side d'in ta nufa a hankali tayi knocking d'in sa sau uku kana ta d'an tsaya.
jin shiru ba'ayi magana ba sai ta tura kofar a hankali ta sa kai ciki.
parlour ne d'an ma dai-dai ci me d'auke da kujeru set d'aya sai d'an ma dai-dai cin TV a like a jikin garu-bango, sai fridge a gefe. parlour'n sai tashi da daddad'an kamshi mai garwaye da sanyin ac yake.
sallama ta shigayi amma shiru babu amsa,
hukunci ta yanke wa kanta ta dire masa abincin ana idan yafito ya d'auka, amma sai tayi tunanin ko dai ba nan ne d'akin nasa ba.
har zata juya ta fita sai kuma ta d'an tsaya tare da zubawa kofar bedroom d'aya dake cikin parlour'n a sannu ta taka zuwa bakin kofar, d'an numfashi taja tare da fesarwa kana ta yamutsa fuska jin wani wari-wari kamar warin sigari.
nan ma knocking tayi daga cikin bedroom d'in akace
"Yes." tsayuwa tayi nawasu 'yan sakanni kana ta tura kofar a hankali da sallama tasa kanta cikin d'akin.
sassanyan kamshi mai had'e da kaurin hayakin taba su suka yiwa hancinta maraba.
yana zaune a bakin gado sike da sigari a hannunsa yana d'an zuka a hankali cikin nutsuwa yayin da d'aya hannunsa ke rike da waya yana d'an daddannawa,
gajeren wando ne kad'ai a jikin sa babu ko riga a jikin sa duk tulin sanyi irin na hunturo amma fanka had'e da ac ne ke ai ki cikin d'akin.
har ta karaso ciki bai d'ago ba idanunsa yana kan waya, gefe kan table ta dire tray d'in ba tare da ta kalli in da yake ba, dan tun shigowar ta da idanunta ya sauka kan shi ganin shi zaune kamar tsirara yasata saurin janye idanunta.
tana kokarin mikewa yasoma magana
"Yusrah kice wa Ummi tabaki ruwan zafi na wanka ki kawo min hitan bathroom d'ina ya ki aiki yau."
jin shiru bata amsa ba yasa shi d'ago wa yana fad'in
"Bakiji abun da na fad'a bane."
yayi maganar cikin d'an tsawa, karaf suka had'a ido dai-dai lokacin da ta mike daga tsunkuyen da take.
da mamaki yake kallon ta kamar yanda itama mamakin ne a bangaren ta, tana ta son tuno in da ta tab'a ganin fuskarsa.
a 'yan dakikan ta tuno in da ta tab'a ganin fuskar shekaran jiya da taje siyan magani har wasu ke ce mata ta tsaya mai kasa ya wuce kafin ta wuce.
a b'angaren sa shima a take ya tuno da in da ya tab'a ganin ta duk da hakan ba d'abi'ar sa bane, bai damu da dole sai ya tuno in da ya tab'a sanin ka a karo na biyu a had'uwar ku cikin rayuwar sa ba.
mamakin da yake wace ce ita sannan kuma me yakawo ta cikin d'akin sa.

juyawa tayi a hankali tanufi kofa bayan ta yabi da kallo har ta fice.
gajeren tsaki yaja kana yacigaba da shan sigarin sa.
lambar Ummi ya dannawa kira tana d'agawa ya ce "Ummi abincin fa yunwa fa nake ji."
Ummi da ta zubawa SEEDRAH ido da yanzu shigowar ta parlour'n ta ce
"Abinci kuma? bayan wan da SEEDRAH ta kawo maka."
sai a lokacin idanunsa suka sauka kan table d'in data d'aura breakfast d'in kai, fuska ya had'e ya ce "Wace ce ita? takawo shine bazatayi magana ba."
murmushi Ummi tayi ta ce
"SEEDRAH ce fa baka gane ta bako 'yar Baban ku Musa."
kashe wayan yayi batare da yakuma cewa komai ba.
a parlour'n ta zauna ganin Yusrah ta fito suka cigaba da hirar su.
sai da yashare kusan awa guda da rabi kafin ya shigo parlour'n, cikin shigar fararen kaya da yadin ya amshi jikin sa matuka sai baza kamshe yake yayin da yake gyara d'aura agogon hannunsa.
tun kan ya karaso cikin parlour'n Suhailat ta kafe shi da ido gaba d'aya ta shagalta da kallon sa, yayi masifar yi mata kyau ba kad'an ba, ashe duk yanda take tsara kyan sa cikin zuciyar ta kyan nashi da tsaruwar sa yad'are tunanin ta.
Halimatu ma sosai ta tafi wajen kallon sa.
gai da Ummi yayi ta amsa tare da fad'in
"Tun d'azu suke jiranka ko suma baka gane su bane Halimatu da Suhailat, jiya ma anan suka wuni baka dawo ba shine yau suka kuma dawowa."
da sauri Suhailat cikin yin fari da ido ta ce
"Ina kwana Ya S.Man kazo lafiya ya hanya? muna tayaka murnar nasaran da a ka samu."
batare da ya amsa gaisuwar da Suhailat d'in take masaba ya ce
"Ok 'ya'yan Alhj Musa ko?."
yayi maganar yana nuna Suhailat da Halimatu dan su ya gane su kasan cewar su suna zuwa duk san da yazo Nigeria,kuma kafin yabar kasar ma su da wayon su.
wani irin d'agowa SEEDRAH tayi jin yan da ya ambaci sunan mahaifinsu babu ko girmamawa ciki a matsayin sa na wan mahaifinsa kai tsaye ya kirasa da Alhaji Musa.
wayar sa ce tayi kara ya d'aga tare da nufar kofa batare da ya amsa gaisuwar da Halimatu itama take mika masa ba.
Ummi ta d'aga murya tana fad'in
"Ai da ka tsaya kun gaisa tun fa d'azu kai suke jira."
Picking call d'in yayi ya kai wayar kunnen sa tare da fad'in
"Ummi idan na dawo ma gaisa yanzu wasu ke jirana na."
daga nan yayi waje a binsa.
tsaki SEEDRAH tayi a karan ranta wan da har sai da yafito duk suka juya gare ta.
taji matukar haushin yanda yakira sunan Baba babu ko kara, gashi a na gaishe sa yana wani batsarwa Allah ma yasa ita batama ko kalli in da yake ba bare ta gaida shi har yaki amsawar, da bakin cikin yafi haka, kwafa tayi tare da cigaba da daddanna wayarta da take.
a b'angaren su Suhailat kuwa ko kad'an hakan bai dame su ba musamman ma ita Suhailat d'in da take ji kamar ta tashi tabi bayan sa.
mikewa SEEDRAH tayi ta dube su ta ce

"Mu tafi ko nayi gaba ne? kunsan ina da islamiyya karfe 2 ga azahar ta kusa."
Ummi ta kalleta tana karanto rashin jin dad'in yadda yaron nata yayi musu a gareta, sai tayi murmushi ta ce
"To ai da sauran lokaci yanzu."
murmushin yake SEEDRAH tayi ta ce
"Banyi guga bane zanje na goge Uniform d'ina kafin."
Ummi ta basu dubu biyu ta ce suyi kud'in napep sukayi mata sallama suka tafi.
a hanya SEEDRAH da har lokacin a cike ta ke taja tsaki tare da fad'in
"Amma wannan mutumin d'an rainin wayo ne."
Halimatu ta dube ta tace "Wani mutum kuma?."
ta ce "Wancan S.MAN d'in mana wai dan tsabar rainin wayo sunan Baba fa ya kira wai wani Alhaji Musa, ai ko Baba ba yayan Abba bane zaici albarkacin girma tun da ya haifesa, idan ma bazai iya kiran sa da Baba ba ai yana da yara sai ya kirashi da Baban wane."
tsaki takuma ja tare dayin kwafa ita har cikin ranta taji haushin hakan.
shekeke Suhailat ke kallon ta ta ce
"To meye nawani jin haushi shifa babban yaro ne ko Abba ma wani sa'in Alhaji yake ce masa, to meye dun yacewa Baba Alhaji Musa akan ba sunan sa bane."
Halimatu ta ce "Gane min hanya meye najin haushin ki?,  ai barashin kunya bane dan ya ce haka."
da mamaki SEEDRAH ke kallon su kana ta ce
"Rashin kunya ne mana tun da bazai iya cewa Abba Alhaji Sulai ba, sai dai ya ce Alhajin kawai ashe yasan ma wan da yake yi mawa sabo da shi ya haife sa ko Hmm."
kai ta girgiza.
hararar ta Suhaital tayi ta ce
"Kina da damuwa wlh, kiyi abin da yake gaban ki kawai mu dai bamu ga wani rashin kunyar sa ba ai ba zaginsa yayi ba."
baki ta tab'e had'e da murgud'a shi sannan ta ce
"Na rantse duk san da yakuma kiran Baba da sunan sa, ni sai na tsayar masa, tun da shi dai ba sa'ar sa ba ne tun da Aunty Hajara ma ta girme shi, ya haife shi ya juya."
ta karashe maganar had'e da kuma murgud'a baki.
Halimatu ta ce
"Kina da tsinannen rashin kunya shi d'in bana gaba da ke d'in bane."
shiru tayi bata kuma ce da su komai ba sai  tsakin da take ta ja jefi-jefi har suka isa gida...........?

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna KARSASHI kada ku manta kafin zuwan KARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 KARSADHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciyar masoya salon labarin na daban ne. ko dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa KARSASHI! ƘARSASHI!! KARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08088110090_ ko 08034690723

*________________________________________*

*🌈🇰AINUWA 🇼RITER'S✍🏼*
*🅰SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association
```

*______________________________________*

🅿️8

Da misalin karfe 5 na yamma S.Man ne ya shigo gida ya tadda Abba da Ummi zaune a parlour, da murmushi Ummi ke duban sa har ya zauna kan d'aya daga cikin kujerun parlour.
Ummi ta ce "Sai yan zu Usman?."
cikin yanayin gajiyar daya kwaso ya amsa mata tare da gaida Abba.
Abba ya amsa yana fad'in
"Tun da ka dawo bamu sami zama mun gaisa sosai ba kullum kana hanyar fita."
zaman sa ya gyara tare da soma latsa wayar sa kana ya ce
"Ni ma nagaji da fitar nan mutane sun hanani sakat."
murmushi Abba yafad'ad'a ya ce
"To ai cigaban kenan."
baki ya tab'e bai kuma cewa komai ba yayin da hankalin sa gaba d'aya ke kan abun da yake a waya. Abba da Ummi kuwa suna ta zuba masa zance, lokaci zuwa lokaci yake amsa musu.
zuwa can yasoma magana batare da ya d'ago ba.
"Abba ina bukatar kud'ina kace wa mutumin nan yabani kud'ina."
Abba ya dube shi tare da fad'in
"Wani mutumin kuma Usman?."
ya ce
"Kudi na dana bawa Alhj Musa aro nake so ya maido min dasu ina bukatar su."
Abba ya ce "To-to ai harna sha'afa, anya Yaya Musa ya aje wad'annan kud'ad'en ma kuwa, dan a gaskiya samun sa ya yi kasa sosai ai kasan kud'in ma banki yabiya da su, sai dai bari dai na tuntub'e sa naji ko da d'an wani abu ne yaba da a gurin sa kafin a samu sauran."
da sauri S.Man ya d'ago tare da da fad'in
"Duka kud'ina zai bani bada kad'an-kad'an
ba."
Abba ya ce "To idan kuma baya da shi fa sata zaije ya yi?, bari dai na tuntub'e sa naji in dai babu kam ai dai dole zakayi hakuri."
mikewa ya yi tare da fad'in
"Bazan karb'i kad'an ba duka kud'ina zai bani jibi nake bukatar su."
yana gama fad'a yayi waje.

bayan sa sukabi da kallo, cikin d'aga murya Abba ya ce "Sha-shan cin banza kai,
idan baya da su na ce sata zaije ya yi, ai dole zakayi hakuri sai ya samu yabaka."
Ummi ko kai ta jinjina tasan halin d'an nata sarai tun da taji ya tsaya matsaya d'aya to kuwa bazai tab'a canzawa ba.

S.Man na fita b'angaren sa ya nufa,yana shiga bedroom yajefa wayarsa a kan gado, kana a sannu yashiga rage kayan jikin sa, yarage daga shi sai boxes.
murjajjen surarjikin sa irin na kakkarfan zaratan maza ya bayyana,
ainahin kyau na tsarin kyakkyawan halittar sa yabayyana a fili.
doguwar mika ya yi tare da lankwasa jikin sa gefe da gefe, irin dai yan da 'yan kwallo suke yi,
kana a sannu yanufi kofar bayi yashiga ya sakarwa kansa ruwa, wanka sosai yayi kana yafito.
ya shirya cikin kananun kaya wanda suka amshi jikin sa sosai, yana gama feshe jikin sa da turarukan sa masu dad'in kamshi, yafito parlour d'auke da na'uwar sa,
sosai ya mai da hankalin sa cikin system da yake daddannawa.
wayar sa ya d'aga tare da lalub'o wata lamba.
magana yasoma yi ga dukkan alamu maganar sirri ce dan ni dai banji abin da yake fad'a ba.
sai gani nayi ya mike da laptop d'in yayi waje.

Bayan kwana biyu kamar yan da S.Man ya ce yakuma samin Abba da batun kud'in sa,ya ce yana bukatar su a yau d'in nan.
bayan fitar S.Man daga d'akin Abba Abba yakira Baba bayan sun gaisa Abba ya ce
"Yaya yaron nan ne Usman yadameni da batun kud'in nan nasa tun shekaranjiya har yau ko a d'an kwai wani abu a gurin ka abashi dai-dai a samu sauran."
Baba dake gaban teburin sa na aune-aune wan da sana'ar aune-aune ya koma da d'an kud'in da Abba ya bashi kan yaja jari dan yasami yanda zai rika ciyar da iyalansa.
tun da yafara sana'ar nan baya wani ganin ci gaba madadin yasami riba sai fad'uwa, a duk san da ya auno hatsi dan ya siyar dakyar uwar kud'in sa yake fita maganar riba kam dai babu ita, bai kuma fasa sana'ar ba dan yana sa ran watarana zai samu.
damuwa ce sosai ta bayyana kan fuskar Baba a wannan lokacin a halin da yake ciki yanzu ina zai sami naira miliyan 30 ko miliyan d'aya bashi da su bare miliyon 30.
cikin damuwa Baba ya ce
"Wlh Sulaiman kud'in dai basu samu ba, kabashi hakuri yad'an karamin lokaci zan nima insha Allahu zan bashi kasuwan ne yanzu sai a hankali."
Abba ya ce "To bari na sanar masa Allah yarufa asiri."

Da misalin karfe 8 na dare S.Man yashigo parlour'n Ummi suna zaune ita da Yusrah.
guri ya samu ya zauna kan d'aya daga cikin kujerun parlour'n, Ummi ta dubesa da murmushi tare da amsa gaisuwar da yake yi mata.
Yusrah ta dube shi tana fad'in
"Barka da dare Bro."
ido ya zuba mata yana mai jingina bayan sa da jikin kujera ya ce
"Bar wannan gaisuwar je ki kawo min abinci yunwa nake ji."
baki ta turo gaba dan ita bata so tayi gaisuwa a ki amsa mata, shi kuma baya wasa da cikinsa

yanzu idan ta b'ata lokaci bata d'auko masa abincin ba sai ya iya sab'a mata.
ta mike tanufi dinning tana magana kasa-kasa
"Wai ka gaida mutum yaki ammsawa ni bazan ma kara gaishe ka ba."
ta zubo masa abincin a plt ta kawo masa, tana aje abincin ya cafko kunnen ta yamurd'a.
hannu ta kai da sauri ta rike hannunsa tare da fad'in
"Wayyo Allah Ya S.Man kunne na zai tsinke."
dad'a murd'e kunnen yayi kana
ya ce "Tsinke shi dama zanyi me kike fad'a?."
murmushi Ummi tayi ta ce "Ai dai kasan bazai wuce rashin amsa mata gaisuwar da bakayi ba kasan ta ai."
sakin kunnen ya yi tare da dungurin ta ya ce
"Wuce ki bar nan sai aka ce dole sai an amsa miki gaisuwar."
da gudu tayi hanyar d'akinta tana matse ido da shafa kunnen ta daya murd'e mata.

Ummi ta gyara zama tare da duban sa da kyau yana cin abincin sa cikin kwanciyar hankali.
ta ce
"Usman me zaisa bazaka kara hakuri har Yaya Musa yasami kud'in nan yabaka ba, tun da bawai baka da kud'i bane a hannun ka, na tabbata kud'in da ka bashi kana da irin su sau ba adadi, me zai sa ka damu da sai ya mayar maka da su yanzu ka kara hakuri har ya samu mana."
a hankali ya had'iye abincin daya kai bakin sa kana ya ce
"To ai bazai samu ba ko nan da shekara nawa ne."
Ummi ta ce "To ai abun da nake so ka gane kenan kayi masa hakuri har ya samu."
"Ya sai da gidan sa kawai ya biya ni tun da bashida wata kaddarar bayan ita, ai na fad'a musu duk san da na shigo Nigeria zai dawo min da kud'i na, Ummi kiyi shiru kada ki kara cewa komai game da maganar nan dan sai ya biya ni gobe goben nan dan ina da abun da zanyi da su."
ganin Ummi tana kokarin kuma jefo wata maganar yad'au plt d'in abincin sa yayi hanyar side d'in sa...

Washegari da misalin karfe 2 na rana motar S.Man ne yashigo gidan Baba. yana dai-dai ta parking yafito yana mai karewa gidan kallo,
a sannu ya jingina da jikin motar tare da hard'e hannunsa a kirji yana d'an kad'a kafarsa d'aya daya sarkafe su guri guda.
hannu yasaka cikin aljuhun wandon sa yazaro wata sigari babba irin na rurawannan had'e da makunnin sa.
ya kunna kana asannu yakai bakin sa yashiga zuko sa ya na buso hayakin, cikin nutsuwa.
sai da yasha tabar natsawon mintuna biyar kana ya jefar da ragowar kasa, yasa kasan had'ad'd'en takalmin kafarsa ya murkushe.

A sannu ya mike daga jinginen da yake yasoma tafiya yanufi kofar da zai sada ka da cikin gidan sannan ya tsaya batare da ya karasa bakin kofar ba.
tsayuwar sa ya gyra da kyau tare da bud'e baki yashiga kwad'awa Baba kira, batare da yin sallama ba.

Kamar daga sama su Mama dake zaune a tsakar gida suka jiyo kiran da S.Man yake kwad'awa Baba.
Mama ta ce "Waye kenan da irin wannan kiran mafarautar haka, babu ko sallama."
Umma ta ce
"Wlh kuwa wannan ai sai ya tsinkewa mutun gaba da irin wannan kira."
Suhailat da Halimatu na zaune ko waccen su na daddanna waya.
SEEDRAH na gefe tana wankin kayan Mama.
wani irin d'ago wa tayi jin yakuma fad'in
"Alhj Musa!".
a kufule ta mike tare da fad'in
"Wai wani irin d'an rainin wayo ne wannan daga jin wannan murya dai bana abokin Baba bane sai dai in ko aiko sa akayi ya kira sa, sai ya rika yi masa irin wannan kira kajimin rainin wayo da rashin tarbiya."
taja mayafinta dake kan igiya tanufi kofar gida tana cigaba da mita.
Suhailat ta mike zumbur tana fad'in
"Wannan muryar kamar na S.Man kada dai kuma shine kije kiyi masa rashin kunya."
bata saurare ta ba tayi waje ita ma ta bi bayan ta.

Tsabar jin haushi idanunta ya rufe tun kan ta kara fita tashiga fad'in
"Ka koma a koya maka tarbiyya ta yadda ake kiran babba, kai idan akaje gidan ku ana kiran sunan Baban ka haka zakaji dad'i ne?."
ido ya tsurawa kofar cike da mamakin son ganin wata isasshiyar ce, tana sako kafarta waje Baba na sako nashi.
dan tun kiran farko da ya yi masa kasan cewar yana zaune cikin parlour'n sa ne ya mike ya fito bakin kofa dan tabbatarwa kansa da gaske shi d'in ake kira.
jin kiran da gaske ne da sauri yariga Suhailat bin bayan SEEDRAH.
da mamaki yake kallon S.Man dayake tsaye yana bin SEEDRAH da mugun kallo.
Baba ya maida kallonsa gare ta sannan ya ce
"Shiga gida SEEDRAH."
sai da ta wasa masa wani irin kallo daga sama har kasa sannan ta murgud'a masa baki cike da tsiwa had'e da jin haushin sa ta yadda ya ke raina Baba wan mahaifinsa, tayi kwafa tare da juyawa ta koma ciki.
Suhaita tun da taga shine har wani b'ari jikin ta yake,ta washe baki tana fad'in
"Kamar na sani kuwa na ce wannan muryar Ya S.Man ne ashe dai kai ne anwuni lafiya ya gida."
kallo d'aya yayi mata ya d'auke kai, batare da ya amsa gaisuwar da take mika masa ba.
itako ko a jikin ta bai dame ta ba da rashin kulatan da yayi, sai dad'a fad'ad'a annurin fuskarta take.
Baba ya ce itama ta koma ciki har ta kule ciki tana waigen sa.

Baba ya dube sa ya ce "Usman barka da zuwa shine zaka tsaya daga waje ai da ka shiga ciki, bismillah mushiga daga ciki."
girman idanunsa S.Man ya rage tare da fad'in

"No sauri nake kud'ina nazo karb'a d'auko min su na wuce sauri nake"
Baba ya ce "A ai munyi magana da Sulai bai fad'a maka ba, ka kara hakuri inata kan kokarin neman kud'in kenan nasamu na had'a maka kud'in dan Allah ka kara hakuri."
fuska ya d'aure tamau kana yashiga kad'a makullin motar da ke rike a hannunsa sannan ya ce "Bazan jira har sai an nima a bani ba yanzu nake bukatar su, nan da kwana uku zan dawo ka adana min kud'ina."
yana gama fad'a ya juya yashige matarsa yabar gidan.
Baba yabi bayan motar da kallo kana jiki a sanyaye ya koma ciki.

S.Man na barin gidan gidan sa dake New G.R.A ya nufa, gida ne mai girman gaske ginin zamani tsarin ginin turawa yatsaru iya tsaruwa.
ya bada kwangilar gina gidan tun yana kasar Spain, anjima da gina gidan anzuba kayan more rayuwa babu abun da babu.
ankule gidan babu kowa cikin ta amma da ma'aikatan da suke zuwa gyaran gidan duk bayan wata 1, shiyasa idan kaga gidan bazaka tab'a cewa babu mai rayuwa cikin sa ba.
kasancewar shi bawani zuwa Nigeria yake ba ko da yazo ma baya kwana a gidan sai dai yazo d'an fisha ya tafi, wani lokaci kuma yakan zo da abonsa suyi hira.
koda yazo gidan bai wani jima ba yafita ya dawo gida a kitchen ya tadda Ummi tana aiki.
sannu da aiki yayi mata kana yayi kokarin wucewa.
Ummi ta dakatar da shi da fad'in
"Wai yau ina kaje ne Usman baka ko tsaya kaci abincin rana ba?."
hannunsa ya d'ago tare da duban tsadadden agogon da ke d'aure a hannunsa yaga karfe 3:30pm ya ce
"Gidan Alhj Musa naje daga gun nawuce gida na."
yayi maganar naya wuceta yabi ta kofar dake cikin kitchin d'in ya nufi side d'in sa.
da mamaki Ummi tabi bayansa da kallo, dan tasan maganar kud'in sa ne kawai zai kaisa gidan Baba, dan haka siddan baya zuwa gidan idan yazo kasar nan.
kai ta girgiza a fili ta furta
"Allah shi kyauta."

A b'angaren Baba kuwa jiki a sanyaye ya koma gida Mama da Umma har suna rige-rigen tambayar sa dalilin daya sa S.Man d'in tsayuwa a kofa ya na yi masa irin kiran da yayi masa batare da sallama ba.
Baba yagirgiza kai cike da damuwa ya ce
"Kunsan a zamanin da muke yanzu mai nima baya fushi haka za idan ana binka dole ka jure wulakanci,kud'i yake bina shine yazo karb'a."
nan Baba yashiga yi musu bayanin yanda a kayi yabashi aron kud'i yabiya bashin banki, dan dama basu san ya amshi bashin banki ba basu kuma san da bashin bankin duka aka kwashe a accoun d'in sa da akayi masa sata ba .
su Mama sun jinjina batun kwarai da gaske tare da tausayawa mijin nasu, sai dai sukayi ta karfafa sa tare da yi masa fatan samin bud'in Allah yabiya sa kud'in sa,
duk da kuwa yawan kud'in da samun su zai iya d'au lokaci mai tsawo musamman a yanzu da suke cikin halin rashi.

SEEDRAH da ta gama wankin da take tana shanya kayan taja tsaki wan da a zuciyarta  tayi bata sammaci fitowarsa ba,
tayi kwafa tare da kad'a harshen ta yabada sauti.
dukkaninsu suka juyo gare ta Halimatu ta ce
"Ke kuma da waye kk tsaki?."
ta ce
"Da wancan S.Man d'in mana yanzu dan yana bin Baba kud'i sai ya zo ya na yi masa irin wannan kira, ai ko wan da bai sansa ba bazai yi masa irin haka ba bare kuma Baba."
kai Baba ya girgiza ya wuce d'akin sa.
Umma ta ce "Ai kuwa bai kyauta ba, dama rayuwa cikin turawa mene ne."
SEEDRAH ko kunkuni ta cigaba da yi kasa-kasa.
"To ai sai kuma kiyi shiru haka dan ke rashin kunya baya baki wuya yayanki ne dai ba kece gaba da shi ba ko sai kin zage sa kihuta."
Suhailat ta fad'a tana aika mata  harara.
baki SEEDARH ta murgud'a sannan ta ce
"Shikuma yanzu da yazo yabo yayi ai ba rashin kunya wa nagaba da shi ba."
ta juya tawuce  d'aki.
Suhailat tabita da harara...

Tana shiga ta tadda wayarta na ring jin sauti na musamman dake tashi cikin wayar yasa ta sakin murmushi dan sanin mai kiran nata, ta isa in da wayar yake ta d'auka tare da niman guri ta zauna bakin gado, kana tayi picking na call d'in ta kai kunnenta tare dayin sallama.
daga cikin wayar Kamal ya ce........!

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci  na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna ƘARSASHI kada ku manta kafin zuwan ƘARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗  ƘARSADHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciya salon labarin na daban ne. ku dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa ƘARSASHI! ƘARSASHI!! ƘARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08034690723_

*_________________________________________*

 *🌈 K AINUWA W RITER'S✍🏼*
* A SSOCIATION🤝🏻*
 ```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*_________________________________________*
 ```

"Albishirin ki." murmushi mai sauti tayi sannan ta ce
"Goro." a b'angaren Kamal shima murmushin yake zubawa da kaji shi zakasan yana cikin farinciki sosai.
ya ce "An bani ke yau alhajin mu yake fad'a min yazo gurin Baba neman izini tun d'azu nake kiran ki nabaki daddad'an albishir d'in nan bakya d'aga wayar."
cikin shaukin kauna da soyayya ta ce
"Wayar tana d'aki ne ni kuma ina waje ina yiwa Mama wanki, lallai ka kawo albishir mai girma zan kuwa baka tukuicin ka yanzu."
ta karashe maganar tana y'ar dariya
ya ce "To ina jira ina jin ki bani tukuici na."
zaman ta ta gyara a sannu ta mai da bayanta ta kwanta jikin pillo,
 cikin murya mai zaki da narka zuciyar masoya ta ce
"Rufa idanunka."
a b'angaren Kamal d'in shima zaune yake kan katifar sa a cikin d'akin sa, yana rungume da pillo a kirjin sa.
a sannu ya maida idanunsa ya lumshe yayin da sautin muryarta mai zaki ke rasa cikin kwakwalwarsa, sonta da kaunarta suna tsarga jini da jijiyarsa.
"Uhm ina jiran tukuici na."
yayi maganar yana dad'a lumshe idanunsa ya dad'a rungume pillon ya cusa shi cikin kirjinsa sosai.
a hankali cikin wani irin sauti mai dad'i da zaki ta ce
"I love you!."
ajiyar zuciya mai sauti yasake tare da fad'in
"Godiya mara adadi hakika kin bani tukuici mai girma wannan tukuicin yafiye min kyautar gida da mota har da karin mata ko da indiya ce."
fuska ta kwab'e ta ce "Me ye na sako wata mace cikin zancen."
dariya yy cikin tsigar zolaya ya ce
"To ke da za ayi miki kishiya bayan aure da shekara zaki hana zancen wata mace."
d'ip ta kashe wayar tare da jefar da shi gefe ta mike tana fad'in
"Ka auro uku rana d'aya."
ta shige bayin Mama, wanka tayi ta fito tatafi d'akin su ta shirya cikin riga da siket na atamfa kalar ja.
 tayi kyau sosai cikin shigar duk da batayi wa fuskarta kwalliya ba dan ita ba ma'abociya penti wa fuska bace,
mai da pauda da manbaki sune kad'ai kayan kwalliyar ta.
waje tayi jin Mama tana kwad'a mata kira.
wayar ta Mama ta mika mata tana fad'in

"Karb'i tun d'azu ake ta kira."
tun kan Mama ta rufe baki wani yaro ya shigo yana fad'in
"Wai SEEDRAH tazo inji wani a waje."
karb'ar wayar tayi daga hannun Mama tana duba mai kiran nata
murmushi tayi ganin kiran Kamal yacika wayar, tasan za'a yi haka ko yanzu ma da akazo kiranta tana da tabbacin shine yazo.

D'aki ta koma tad'au mayafin ta tafita,
a tsaye ta iske shi a kofar gida tacikin get.
baki ta turo tatsaya daga can d'an nesa da shi ta hard'e hannayenta a kirji ta kawar da fuskarta daga kallon shi.
murmushi ya sake me sauti ya tako gabanta ya tsaya yad'an tsunkuyo tare da loko fuskarta.
fuskanta ta kuma juyawa gefe tare da kuma turo baki gaba.
fuska ya marairaice kamar karamin yaro yakai hannu yarike kunnuwansa ya narke murya kalan tausayi ya ce
"A yafewa bawan Allah afuwa yake nima bazai kara ba."
baki ta murgud'a tare da kad'a kwayar idanunta ta ce
"Ka koma kaje ka sami 'yar india."
dariya ya tuntsure da shi sosai ita ko ta juya da sauri zata koma gida.
da sauri ya sha gabanta yakuma kai hannu yarike kunnuwan sa ya ce
"Yi hakuri mana rikicacciyata ai ko matan duniyar nan gaba d'aya zasu taro babu wacce ta isheni kallo bare saurare, ayafewa bawan Allah, bazai sake sako wata cikin zance ba daga yau."
baki ta murgud'a ta ce
"Oho ba ni inaruwa na ma."
dariya yy cikin zolaya yaleko fuskarta ya ce
"Ashe haka ake kishi na?."  kwayar idanunta ta kad'a sannan ta ce "Waya fad'a maka."
murmushi yy ya ce "Gashi nan ina gani."
baki ta murgud'a ta ce "To ba haka bane."
dariya yayi yana mai jin shaukin tsiwarta da sonsa da yake hangowa tattare da ita.
nan suka shiga hirarsu cikin so da kaunar junansu, zuwa can sukayi sallama ta koma gida...

S.Man ne yafito cikin shigar manyan kaya, yayi matukar kyau cikin shigar, kasan cewar shi bai cika saka jamfa ba yafi mu'amala da kananun kaya. idan kagansa da manyan kaya to yazo Nigeria ne ranar juma'a ko halartar d'aurin aure sai ya saka manyan kaya.
cikin  d'an sauri yake tafiya yakara so cikin parlour.
Ummi tadube sa tana fad'in
"Inazuwa da sauri haka Usman? yanzu nake shirin nimanka muyi magana."
hannunsa ya d'ago tare da duban tsadedden
agogon dake d'aure a hannunsa kana ya ce
"Zanje d'aurin auren wani abokina ne a Abuja sauri nake Ummi bayan sallar juma'a za'a d'aura,

idan na dawo sai muyi maganar."
"To Allah ya tsare adawo lafiya."
"Amen." yafad'a yana fita daga parlour'n...
da misalin karfe 12 na dare S.Man ya dawo, ganin dare yayi bai wuce gidan Abba ba.
gidan sa yawuce.
yana isa ya yi hon maigadin dake gadin gidan duk da babu kowa cikin gidan da akwai mai gadin gidan, yabud'e masa get ya kusa hancin motarsa ciki.
A gajiye ya fito daga cikin motar yana amsa gaisuwar da maigadi ke miko masa ya wuce cikin gidan.
direct d'akin sa dake sama ya wuce, yazuba wayoyin sa saman bedside yarage kayan jikinsa ya fad'a bathroom.
minti 20 ya d'auka cikin bayin yafito d'aure da towel a kugunsa,
ya isa gaban wardrobe yazaro wata tattausar rigar bacci mai mad'aurin igiya had'e da boxes ya saka.
ya haye lafiyayyen gadon sa dake a gyare tsaf sai baza kamshi yake, yarage wutan d'akin yayi addu'a ya kwanta babu jimawa bacci yayi gaba da shi.

Washegari yana dawowa daga sallar asuba can gefen parluorn kasa ya isa in da na'u'rorin motsa jiki suke.
bai sakaita ga motsa jikin da yake ba,
sai da yashafi tsawon awa uku.
yazube kan wata kujera dake gurin yana maida numfashi tare da share gumin dake sauko masa da karamar towel yayin da d'aya hanunsa ke rike da gorar ruwa yana sha.
wayar sa ya d'aga ya lalub'o number Ummi, tana d'agawa ya ce
"Ummi yunwa kisa a kawo min abinci yanzu ina gida na."
yana gama fad'a ya kashe wayar.
mikewa yayi yahaura sama, bathroom ya shiga yayi wanka kana yafito d'aure da towel a kugunsa yana tsane ruwan jikin sa da wata tattausan farar karamar towel.
yashirya cikin riga singlet da wando iya guiwa, sai tashi da daddad'an kamshi yake.
ya haye gado.
kwance yake a kan gadon yayin da waya ke rike a hannunsa yana d'an daddannawa.
hannunsa yakai saman cikinsa ya shafa.
number Ummi ya kuma dannawa kira
"Ummi har yanzu ba a kawo min abincin ba."
"Kasan dai sakanin nan da gidan ka akwai nisa Yusrah tana hanya tafita bada jimawa ba zata iso."

Yana kashe wayar bada jimawaba Yusrah ta iso.
ko da yagama breakfast kwanciya yayi, sai wajen azahar ya farka. wanka ya kuma kana ya shirya cikin kananun kaya, ya d'au makullin motarsa ya fita.
a masallacin dake jikin gidansa yayi salla kana yad'au motarsa yanufi unguwar rimi gidan Baba.

ko da ya isa gidan yana dai-dai ta parking a farfajiyar gidan ya fito ya jingina da jikin motar yayin

da ya hard'e hannayensa a kirji.
murya ya d'aga yashiga fad'in
"Alhj Musa Alhj Musa!."

a can cikin gidan kuwa SEEDRAH data fito daga d'akin Mama zataje kichin, rike da tray da shingafar da zataje dafawa ciki.
cak tatsaya jin kiran da akewa Baba, ko ba a fad'a ba tasan S.Man ne da irin wannan rashin darajar.
da sauri ta dire tray'n shinkafar kasa ta nufi waje cikin sauri tana fad'in
"Idan ba a ja masa layi ba zaiga kamar ko tsoronsa a ke ji, ai ba akan Baba kad'ai aka fara cin bashi ba gwamnati ma tana ci."
ta karashe maganar da take acikin ranta dai-dai lokacin da take karaso wa inda yake.
kugu ta rike tana yi masa wani irin kallon sama da kasa.
cikin murgud'a baki cike da tsiwa ta ce
"Rashin daraja nagaba ne ko karancin tarbiyya? har idan zakazo kacigaba da yiwa Baba kiran dirar mikiya batare da girmamawa ba kai ma baza a girmamaka ba, sannan kasani mu musulmai ne mun iya amsa sallama,
kud'in ka kuma kaje duk san da Baba ya samu zai baka yanzu bashi da su."

Wani irin kallo mai had'e da zalrar mamaki yake bin yarinyar da shi, ransa yayi mugun b'aci.
wannan yarinyar da bata wuci sa'ar Yusrah ba itace ta tsaya a gaban sa take gaya masa bakaken kalaman da babu wan da ya tab'a tsayuwa gaba da gaba ya fad'a masa.
da sauri ya kai yannu cikin aljuhun wandon sa ya zalo sigari had'e da  makunnensa, makunnin nasa kad'ai abin kallo ne dan ba irin na kasar mu bace haka ma sigarin irin na kasashen turai d'in nan ce,
 yasaka tabar a bakin sa kana yakunna sigarin.
ya zuko hayakin sigarin tare da huro hayakem waje, da sauri-sauri yake zuko hayaken tare da huro shi,
sumar kansa ya shiga shafawa da d'aya hannunsa.
sai juya gefe da gefen sa yake, yama rasa me zaiyi wa yarinyar nan.
 ji yayi kamar ya b'ab'b'allata ya zubar da ita a gurin.
da sauri ta kawar da kanta tare da toshe hancin ta tana yamusa fuska cikin yin kasa da murya ta ce
"A she dai d'an shaye-shaye ne haba dole mana."

Zaro sigarin ya yi a bakin sa muraran kake iya hango matsanan ciyar b'acin ransa kan fuskarsa kana ya ce
"Zan nuna miki halin d'an shaye-shaye kuwa!."
kafad'a ta d'aga kana ta juya cikin sauri dan ta d'an razana da jin kalaman sa da kuma yanda taga yarikid'e yakoma mata na mijin zaki.
cike da karfin hali da dakiyar zuciya take fad'in
"Koma meye kayi Allah na tare da ni."
tayi cikin gida da sauri.

Shiko wurgi da sigarin hannunsa yayi yashiga motarsa yajata da mugun gudu yabar gidan.
gidan Abba ya nufa.
yana isa direct side d'in sa ya wuce batare da yabi ta cikin parlour'n Ummi ba.
yana shiga bedroom yad'au System d'in sa ya zauna bakin gado ya kunna kana yashiga dube-dube aciki.
yad'au tsawon mintuna 15 yana sarrafa na'uwar kana ya rufe ya tura gefe.
d'an kishin gid'a yayi a kan gadon kana ya d'au wayarsa ya daddanna ya kai kunnensa.
magana ya soma wan da ni bana jiyo abin da yake fad'a, daga bisani ya kashe wayar.
ya mike yashiga tarkasa abubuwan da yake bukata kana yad'au laptop d'in yayi waje.
ta sashin Ummi yabi a parlour ya taddata,
ya zauna tare da gaishe ta.
ta amsa tana fad'in
"Dama ka shigo ne?."
"Ban jima da shigowa ba yanzu zan koma dan nayi ba'i."
"Abinci fa da dai ka tsaya ka ci kada ka tafi ka soma kiran a kawo maka."
mikewa tsaye yayi yana fad'in
"Bani abincin natafi da shi sauri nake."
Ummi ta mike ta nufi kichin tazubo masa abinci cikin kula ta sakashi cikin basket had'e da plt da cukali, sai kwalin lemo da gorar ruwa had'e da cup ta fito ta samu har yayi waje.
Yusrah ta kira ta bata basket d'in ta kai masa cikin mota, ta bud'e sit d'in baya ta aje basket d'in ciki.
tana rufe murfin motar ya ja motar da sauri yabar gidan..

Bayan kwana biyu

Yau da wuri SEEDRAH tagama aikin ta kasancewar yau asabar ne tana gida.
daren jiya Kamal yayi mata alkawarin kaita gidan kawarta Naseeba.
karfe sha d'aya tagama shiri tafita rike da waya a kunnenta tana fad'in
"Gani fitowa."
d'akin Mama ta shiga tayi mata sallama dan tun ajiyan ta fad'a mata zataje gidan Naseeba, ta ce mata kada ta kai dare ta dawo da wuri.
Kamal natsaye a bakin get takaraso in da yake tare da hararar sa cikin tura baki ta ce
"Wannan kallon fa?."
numfashi ya sauke tare da kyakkyafta idanunsa da tun fitowarta yakafe ta da su ya ce
"Baby kinyi kyau fa kamar na kwana ina kallon ki."
'yar karamar dariya tayi ta ce
"Kwana a tsaye ko a kwance."
"Duk yanda kike so zaki shigo hanu ai zakiyi bayani."
fuska ta b'ata tare da turo baki ta ce
"Banson haka fa ni banja da tsawo ba."

dariya ya yi kana ya d'an kwanto mata da mashin d'in ya ce
"Hau muje nima ban warware zargen ba."

Suna tafe suna hirarsu cikin so da kauna har suka isa gidan su Naseeba, a kofar gidan ya faka mashin d'in sa yana gaba tana biye da shi suka shige gidan da sallama.
Maman Zeey tana sakar gida tana d'an aikace-aikace, ta amsa sallamar tana fad'in
"A a yau ankawo min surukar tawa ce da kanka ba sai tazo abiyo ta ba."
murmushi tayi cike da jin kunya tayi kasa da kai.
"Ina yini Maman Zeey ya gida."
ta fad'a tana d'an murmushi da wasa da bakin gyalen ta.
Kamal kuwa dariya yayi tare da shafa gefen fuskarsa ya ce
"Maman Zeey kuyi kuje ku d'auko min ita dan Allah nifa hakuri na yafara karewa."
ido SEEDRAH ta waro cike da mamaki mai had'e da jin kunya tana aika masa da harara ta gefen ido.
shiko gira ya d'aga mata.
dariya Maman Zeey tayi ta ce "Allah ya shirya Kamal zamu d'auko maka ita."
da sauri SEEDRAH ta d'aga kafa zata bar gurin.
Zeey data fito daga cikin d'aki da sauri cikin muryar dariya ta ce
"Tsaya-tsaya-tsaya, yauwa tun da kinzo yau zamuyi gwajin girki naji irin girkinki,
Allah in baiyi dad'i ba daga yau Ya Kamal ka daina yimin gorin girki ehe."
dariya tayi tawuce sashin Naseeba, Kamal yabi bayan ta yana fad'in
"Yarinya asalin girki ta iya ke dai kishirya zuwa gidan mu kwad'ayi."

Ihun murna Naseeba ta sake ganin SEEDRAH ta rungume ta tana fad'in
oyoyo.
SEEDRAH ta janye jikin ta tana fad'in
"Ke kada kije ki matse mana baby irin wannan runguma haka."
"Ai murnan ganin kine."
Nasiba ta fad'a tana dariya.
"So take ta janyo mana asara kibi a hankali fa."
cewar Kamal yana karasowa ciki
Mukhtar yafito suka tafa da abokin nasa, duk suka shige ciki.
a parlour suka ya da zangon su.
nan da nan Naseeba ta cike su da kayan ciye-ciye suna ci su hira.
SEEDRAH ta dubi d'an karamin cikin Naseeba daya fara tasowa ta ce
"Mace fa zaki haifa mana dan so nake nakoyi kitso a kanta."
"Yauwa fad'a masa nimafa mace nake so wai shi namiji."
Mukhtar ya ce
"To dai son kai za a gwada mana, Kamal ko kai ma kana bayan su ne."
kallon kasa-kasa Kamal yabi SEEDRAH da shi kana ya ce
"Namiji muke so ita shugaban 'yan maganan ma ta shirya rainon maza biyu."
baki SEEDRAH ta murgud'a masa ta ce
"Kabaryi da ni."

dariya Mukhtar yayi ya ce
"Kayi kokari abokina."

Hira sosai suke cike da zolayar juna, ko da aka kira sallar azahar Mukhtar da Kamal suka tafi masallaci, basu dawo gidan ba sai da akayi sallan la'asar.
nan SEEDRAH ta ce zata koma gida Mama ta ce kada takai dare, kuma tana so ta shiga gidan Nabeela. tayi musu sallama
Kamal ya d'auke ta sukayi gidan Nabeela daga nan ya mai da ta gida...

Zaune Baba yake a d'aki yana huta gajiyar daya kwaso a kasuwa, kira yashigo wayar sa.
ganin mai kiran nasa yasashi shiga damuwa, jiki ba kwari yad'aga kiran.
daga cikin wayar S.Man ya ce.........!

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)

_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci  na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna KARSASHI kada ku manta kafin zuwan ƘARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗  KARSASHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciya salon labarin na daban ne. ku dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa KARSASHI! ƘARSASHI!! KARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08088110090 ko 08034690723_

*______________________________________*

*🌈🇰AINUWA 🇼RITER'S✍🏼*
*🇦SSOCIATION🤝🏼*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*______________________________________*

page 10

"Nazo gidan ka ji ina fata an fad'a maka, bazan kuma zuwa na uku nayi zuwan banaza ba, ka
```

tabbatar da ka ajemin kud'ad'ena dan yau babu afuwa cikin zuwa ta."
yana gama fad'in haka ya kashe wayar.
Baba ko numfashi ya sauke yana jinjina kai .
Mama dake zaune gefen sa idanunta akan sa ganin yadda ya zaro wayar jiki a sanyaye yana juya wayar cikin matsanan ciyar damuwa ta ce
"Usman ne ko?."
kai yagyad'a mata alamar Eh. kana ya ce
"Bansan ta hanyar da zanbi na iya samo masa kud'insa ba sati guda nayi ina zuwa kasuwa da iya karfi na nake gudanar da kasuwan cinnan amma yar yau ban had'a ribar da ta kai naira dubu d'ari ba,
ina da tabbacin koda shekara zanyi bazan iya samun naira miliyon 30 ba."

Numfashi yaja kana ya ci gaba
"Idan ba gidan nan zan d'aga na siyar ba to bansan ta inda zanbi na samo masa kud'in sa ba, kud'i yana da wuyar sha'ani kud'i ke sa karami ya raina babba, d'an d'an'uwana yake gaya min maganganun da suka fito daga bakin sa, wan da ko shi Sulaiman d'in bazai iya duban tsabar idona ya gayamin kwatankwacin sa ba."
"Yanzu sai da gidan za'ayi."
Mama ta fad'a cike da damuwa.
"Baza a sai da gidan ba, idan aka sai da ina zamu je, idan kuma gidan haya zamu koma a wanna lokaci da haya tayi tsada ga shekara yanzu babu wuyan ta zago, y'an kud'in da nake juyawa bazasu wadacemu abiya haya sannan aciyar da kai ba."
kai Mama ta jinjina cike da tausayin halin da suka tsinci kansu ciki..
Wunin ranar Baba yayi ta zuba idon ganin da me S.MAN zaizo yau kuma,
amma har dare bai zoba, a daren ranar yakira Abba ya ce yaroka masa S.MAN d'in yakara masa hakuri.
ko da Abba yakira S.MAN da batun kin dawowa gidan Abba yayi, yayi zaman sa a gidan sa.

Bayan kwana biyar har lokacin Baba na zuba idon ganin S.Man shiru sai dai shi S.Man d'in ma baya kasar yatafi kasar spain sakamakon kiran gaggawar da yasamu kan buga wani wasan da zasuyi.
watan S.Man guda da tafiya kenan
zuwa lokacin sosai Baba ya dage da niman kud'i duk da yasan kasuwan cin da yake yi in shekara goma zaiyi bazai sami ribar da zai kai kud'in da yake bin sa ba, sai dai yasan hanyar Allah tana da yawa.
in yaso sai ya bud'a masa a cikin rabin shekara yasami kud'in sa ya basa.
ya sanyawa ransa haka sai dai ina, jiya kamar yau wata guda bai ajiye kud'in da yakai dubu d'ari ba...

Da sauri SEEDRAH ta fito daga d'akin Mama cikin shigar tafiya school tayiwa Mama sallama tayi waje, da d'an sauri take tafiya dan ta d'an makara sai da ta haura can bakin titi kafin ta sami abin hawa.

Yau Baba na gida bai fita kasuwa da wuri ba har wajen karfe shad'aya da rabi,  yafito daga d'akinsa, su Mama suna yi masa a Allah bada sa'a.
yana fitowa farfajiyar gida tsayuwa yayi da d'inbin mamaki ganin S.Man da wasu mutane ga dukkan alamu shigowarsu kenan.
da kaga mutanen zakasan hukuma ne su dan ga alamun hakan a tattare da su.
Baba ya karaso in da suke jiki a sanyaye yana fad'in
"Usman kaine tafe sannunku fa yaushe ka dawo kasar?."
hannu S.Man yad'aga masa batare da ya amsa gaisuwar had'e da tambayar da yake masa ba.
kana ya dubi mutanen dake tare da su ya ce
"Shine wannan kusashi yanzu ya fita a gidannan nakulle shi."
cikin matsanan ciyar tashin hankali Baba ya ce
"Haba Usman dan Allah dan Annabi kayi hakuri idan kafitar damu a gidan nan ina zamu koma, ka kara hakuri ina ta kokarin nima maka kud'in ka ko yanzu ma gurin niman zanje."
"Kuzauna a titi ma bai shafeni ba, yau zakabar gidan nan sannan kasani idan har nasiyar da shi yagaza kud'in da nake binka dole zakayi min ciko, kana b'ata mana lokaci dukkanin mu muna da abin yi kusashi ya miko min takardun gida, idan kuma ka hana yanzu ni me iya sawa ne a buga min wasu."
hukumar dake tafe da shi su suka ce
"Shiga ka d'auko takardun gidan sannan ka sa mutanen ciki sufito had'e da kayan ku."
hannu Baba ya had'a bibbiyu yashiga rokon su da magiya kan suyi masa hakuri su barshi a gidan sa, amma me kamar dad'a ingiza S.Man ake yana kwararowa Baba rashin mutunci sinki-sinki.

Hayaniyar da su Mama sukaji ne yasasu fitowa ganin abunda ke faruwa hankali tashe suma suka shiga basu hakuri.
Suhailat da Halimatu sunyi jungum-jungum yayin da idanunsu ke kan S.Man...

SEEDRAH da ke tafi kan abin hawa zuwa makaranta har sunyi nisa ta tuna bata d'au wani littafin ta mai muhimmanci ba, da sauri ta ce wa mai abin hawan
ya juya da ita tayi mantuwa zata kara masa kud'i.
suna isa kofar gida ta rika jiyo hayaniya da sauri ta sallami mai abin hawan ta shige gida cikin sauri har tana had'awa da sassarfa.
turus ta ja ta tsaya daga bakin get tana kallon kowa d'aya bayan d'aya.
can ta hango Mama da Umma da Baba suna ta zuba magiya kamar zasu zuba guiwowin su a kasa.
S.Man na jingine da jikin motarsa ya hard'e hannayen sa akirji yana girgiza kafa cike da rashin daraja, wad'an nan mutanen dayazo da su kuma suna cewa su Baba suyi suje su fara fitowa da kayan su.
Baba ya matsa gaban S.MAN cikin magiya da roko ya ce
"Usman ni fa wan mahaifinka ne kada ka mance da Sulaiman da ni uwa d'aya uba d'aya, ko wani kagani zai yi min irin wannan tozarcin bazaka kyale ba sai kuma gashi kaine da kanka

kake kokarin tozartani, haba Usman ka farka daga baccin da kake mana."
hannu S.MAN ya d'aga masa kana ya ce
"Dangantakar ka sakanin kai da mahaifina ne ba da ni ba, idan kai yayansa ne bai zama kai yayana bane so shine d'an'uwan ka bani ba, nifa a kan kud'i komai ma zan iya musamman wanda na tara da gumi na, idan baza ku iya fitar da kayan ba yanzu nabiya afitar dasu!!."

"Wace doka ce tabada damar fitar da wanda ake bi bashi a gidan sa kai tsaye rana asaka batare da bincike da yanke hukuncin wad'an da suka dace ba!!."

Maganar SEEDRAH suka sinkayo cike da amon sauti mai nuna zallar tafasar zuciya had'e da raurin d'iya mace.
tattausar muryar ta mai zaki dake fitar da sauti cikin nuna zallar b'acin rai da takaicin tozarcin da ta taras akeyiwa mahaifinta, tashiga d'aga kafarta tana dumfaro inda suke ya yin da tashiga nuna S.MAN
da hukumar dake tafe da su da hannu tacigaba da fad'in
"Babu dokar da ta ce haka, dan haka baku da ikon da zakuce lallai sai ya fita a gidan sa ya baku a bakin kud'in da ake binsa,
kuje kuyi sammacin sa a kotu idan kotu ta kirasa zai amsa kiranta dan acan ake zartar da hukuncin daya dace, daga nan fa duk kud'in da yake samu a sati ko wata ko shekara aciki za'a rika cirewa ana baka har bashin ka ya kare, baka da ikon da zaka zo da wasu kace sai yabar gidan sa, babu in da zamuje muna nan,
idan kud'in ka kake so kaje ka kai karan Baba kotu!."
ta karashe maganar da nuna S.MAN da yatsa had'e da murgud'a masa baki.

Tun da tafara maganar ya kafe ta da ido ganin kokari da karfin halin yarinyar.
cikin tsawa d'aya daga cikin d'ansandan da akazo da su ya ce
"Ke hukuma ne zakija dasu yanzu zakiji ki a cikin cell."
Mama ce tayi saurin ruko hannun SEEDRAH ta jata tana fad'in
"Ke SEEDRAH hukuma ne fa zo ki shiga ciki."
"Mama dan hukuma ne sai ayi shiru a kyale gaskiya bayan ga gaskiya ana gani a fili, tun da su ba mala'ikun zare rai bane kibari a fad'a musu.."
da sauri Mama ta rufe bakin ta bata bari ta karasa ba,
S.MAN yabi bayan ta da kallo har suka b'acewa ganin sa.
da sauri yazura hannunsa cikin aljuhun wandon sa yana kokari zaro sigari sai kuma ya bari, yakai hannu ya shafo sumar kansa tare da furzar da iska daga cikin bakin sa.
sai da Mama ta kaita har cikin bedroom d'in ta sannan ta sake ta ta kuma ce ta zauna anan kada ta fito.
kuka SEEDRAH ta fashe da shi takifa kanta jikin pilo tana mai jin d'aci cikin ranta da mugun tsanar S.MAN

Can waje kuwa har lokacin su Baba suna ta kan faman magiya da roko,
S.MAN ya dubi d'aya daga cikin d'ansandan dake kusa da shi kana ya yi masa magana kasa-kasa.

kai d'ansandan ya gyad'a kana ya dubi 'yan'uwan sa ya ce
"Kuzo muje."
suka shige mota shima ya shiga yaja suka fice a gidan.
godiya wa Allah su Umma sukayi ganin sun tafi batare da sun ce komai ba.
jiki bakwari sukaja kafafunsu suka koma ciki.
Baba na shiga d'aki lambar Abba yakira sai yaji wayarsa a kashe ya ma gama mancewa da Abba'n yatafi wani kasuwanci shida abokinsa a Japan.
Mama tashigo d'aki ta sami SEEDRAH zaune a bakin gado tagama kukan ta share hawaye ta turo baki gaba.
ta dube ta tana fad'in
"Su Usman d'in sun tafi ma wata kila ya hakura ne, yakamata ki tashi ki koma makaranta me ma yadawo dake ne ma?."
kwanciya ta gyara kan gadon Mama ta ce
"Sai kuma gobe yanzu kam."
Mama ta ce "Allah ya kyauta."
tayi waje.
A b'angaren Baba ma kasuwan da bai fita ba kenan ranar dan gabad'aya jikin sa yagama mutuwa.

Da misalin karfe 8 na dare S.Man ne zaune cikin parlour'n sa dan yanzu yadawo zaman gidan sa. in ka gansa gidan Abba to yaje gaishesu ne.
d'agowa yayi daga kallon System daya mai da hankalinsa sosai yake aikin latsashi,
sai dai fuskarsa sam babu walwala.
d'an shiru yayi da alama dai nazari yake rufe System d'in yayi ya mike da d'an sauri ya zari makullin motar sa dake kan table d'in gaban sa yafita da d'an sauri.

Baba da ya fito daga masallaci sallar isha yazo zai shiga gida yaga mota tsaye a kofar gida.
ganin wan da yake tsaye jikin motar yasashi karasowa in da yake jiki a sanyaye, yana tunanin da wani abun kuma yazo yanzu.
S.Man yagyara tsayuwar sa da kyau kana ya dubi Baba da duk jikin sa yagama sanyi yana zaman jiran jin ta bakin sa ya d'an karkata kai kana ya ce
"Ina bukatar 'yar aiki da zata rika kula min da tsaftar gidana da girki zan rika biya duk wata, idan kaso sai arika cirewa daga cikin bashin da nake bin ka."
tun kan ya karasa Baba ya ce
"To-to-to bawata matsala ai ga yarannan in kyauta kake so ma sai surika zuwa suna yi maka ai bawata damuwa ai, ina dai shike nan abunda kazo da shi gobe sai suje su fara."
baki ya tab'e ya ce
"Ba gayya nake so ba mutum d'aya ma ya isa."
Baba yawashe baki da jin dai ba maganar kud'i ko gida bane dai yazo da shi cikin kuma washe baki ya ce
"Au to shike nan ai tun da Suhailat itace babba sai ta rika zuwa."
katse shi ya yi da fad'in
"Ba ita ba d'ayar...........!

Mommyn Twins ce

🌺 *ƘARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna ƘARSASHI kada ku manta kafin zuwan ƘARSASHI HAMDAH ya
zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 ƘARSASHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciya salon labarin na daban ne. ku dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa ƘARSASHI! ƘARSASHI!! ƘARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08088110090 ko 08034690723_

*___________________________________________*

*🌈 K AINUWA W RITER'S✍🏼*
* A SSOCIATION🤝🏼*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏼

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*___________________________________________*

page 11

Baba ya ce "Ohoo Halimatu? ai ko gobe sai ta fara zuwa."
d'an shiru S.MAN ya yi alamun nazari, Baba ya juya zai shige gida yana fad'in
"In Allah ya yarda gobe da sassafe zata fara zuwa ai ba wata matsala kannen ka ne ai kana da iko da su, idan akwai wani aikin ma nan gaba sai su tafi duka da Suhailat d'in dun su gudanar da aikin da sauri, bawata damuwa ai gobe zata fara zuwa."
"Ba ita ba, sannan kuma bana bukatar zuwa a matsayin dangi na amatsayin 'yar aiki nake bukata, kuma ba wacce zata rika zuwa tana dawowa ba sabo da kowani lokaci zan iya bukatar a gudanar min da wani abin, idan zuwa zatayi tarika dawowa lokacin da na bukaci wani abu bata nan fa?."

Tsayuwa Baba ya yi tare da juyowa ya ce
"To-to wa ke nan SEEDRAH kake fad'a?."
d'an shiru ya sake yi yana juya sunan cikin ransa yana son tuna sunan da yaji Ummi ta kirata da shi randa yafara ganin ta a gidan su takai masa abinci.
kai ya gyad'a masa duk da baya da tabbacin sunan nata kenan dan baisan sunan ta ba bai
```

kuma tuna sunan da yaji Ummin ta fad'a ba.
Baba ya ce "To ba matsala shikenan bari na shiga ciki muyi magana."
Baba ya shiga ciki da sauri dan baya so ya tsaya har ta kaisu ga zancen kud'i ko gida.
aransa kuwa yana tunanin ta yadda za'ayi SEEDRAH taje ta zauna a gidan sa bayan tana tafiya makaranta, kawar da tunanin ya yi da ayyana daga can d'in saita rika zuwa koma ta aje karatun.
dan shi yanzu yana jin duk abunda S.MAN ya ke bukata zai masa har idan zai sarara masa kan maganar kud'i da gidan sa.

Direct d'akin Mama Baba ya shige ya taddata zaune kan sallaya tana jan jarbi, yazauna bakin gado.
ta d'ago ta dube shi tana fad'in
"Barka da dare Alhj." ya ce "Yauwa."
kana ya muskuta da kyau ya gyara zaman sa sannan ya ce
"Usman ne yazo yanzu ina ga ma ya tafi."
kirji Mama ta buga a d'an razane ta ce
"Allah dai yasa ba da hukuma yakuma zuwaba,
yau idan yad'aga mu a gidan nan ina zamuje."
"Ba da kowa yazo ba, zuwansa na yanzu ya bambamta da zuwansa na ko yaushe,
yanzu yazo ne niman wacce zata rika yi masa aiki a gidan sa yakuma ce wai SEEDRAH ya ke so taje tarika yi masa aikin."
ido Mama ta waro tare da kuma dafe kirji ta ce
"Meyasa sai gidan nan ne zai zo niman 'yar aiki meyasa kuma yazab'i SEEDRAH ita ce zatayi masa aikin, Alhj ina jin tsowa nasan SEEDRAH ma bazata amince ba tun da ga su Halimatu d'aya daga cikin su kawai tarika zuwa tana yi masa aikin."
Baba ya riko hannunta ya ce
"Haba meye kuma najin tsoro ai godewa Allah yakamata ma muyi tun da har ya tako kafa yazo niman wani abu a gurin mu ko tanan zamusan yad'an hakura zaiyi mana jinkiri zuwa musamu kud'in sa mu basa, zai kuma hakura yabarmu a gidan mu, har Allah ya kawo lokacin da zamu samu kud'in sa murabu da shi,
kuma ma ya ce zai rika biyan kud'in aikin, sannan kuma kud'in albashin acikin kud'in da yake bina zai rika cirewa ai kin ga dai za'a d'an rage wani abin,
kuma nima sai da na ce masa gasu Halimatu ya ce basu yake bukata suyi masa aiki ba ita SEEDRAH yake bukata."
"Alhj to karatun ta fah sai dai tarika zuwa da farar safiya ta dawo ta tafi makaranta ke nan."
hannuta Baba yakuma damkewa ya ce
"Nima nayi tunanin hakan amma ya ce zama zatayi acan gidan nasa, ai inaga babu wata matsala in yaso daga can d'in sai ta rika tafiya makarantar."
"Amma Alhj.."
katse ta ya yi da afad'in
"Hakan ne kad'ai mafita kituna fa idan mukace zamuyi masa musu to fa babu makawa sai munbar gidan nan,
dan Allah kada kikuma cewa komai ki kirawo SEEDRAH kiyi mata maganar ta shirya idan Allah yakaimu gobe zan kaita gidan nasa."

Numfashi Mama tasauke kana ta gyad'a masa kai jiki a sanyaye, Baba ya mike ya fita, yana fita Mama ta daga waya ta kirawo lambar SEEDRAH.
SEEDRAH dake kwance a d'akin su manne da waya a kunne suna waya da Kamal, ganin kiran Mama yasa ta cewa Kamal d'in ya kashe bari taje kiran Mama, ta mike ta nufi d'akin Mama.
Mama na ganin ta tamike daga kan sallayan da take zaune ta koma bakin gado.
"Zo zauna nan." Mama tafad'a tana nuna mata gefe da ita.
SEEDRAH ta karaso ta zauna kusa da ita
Mama ta dube ta da kyau kana ta ce
"Yayan ku Usman yazo."
SEEDRAH ta ce "Waye kuma Yaya Usman Mama?."
"Usman d'in Abba'n ku Sulaiman S.MAN fa."
baki SEEDRAH ta tab'e ta ce
"Usman dai ko S.MAN d'in babu wani Yaya mutumin da baya ganin darajar Baba mezai sa shima a daraja shi, yakuma zuwa ciwa Baban mutunci ne?."
kai Mama ta girgiza  kana ta ce
"Ki shirya kayanki gobe Baba ku zai kaiki gidansa zaki je ki d'an rika kula masa da gida ne."
wani irin waro ido SEEDRAH tayi tare da d'an zabura tanuna  kanta ta ce
"Ni nine zanje gidan sa kula masa da gida?!."
sai kuma ta shiga girgiza kai tana fad'in
"Mama kinsan me kike fad'a kuwa tayama hakan zata kasance, ina bazai yuwuba babu in da zani, wato ta nan ya b'ullo, wata kofar wulakanta Baba ke nan ya samo ko, to wlh bazai tab'a yuwuwa ba ni kam babu in da zani."
ganin yanda ta birkice gaba d'aya tana kokari mike wa Mama ta ruko ta tana fad'in
"Ke SEEDRAH ki nutsu ki saurare ni kiji, bijirewa hakan tamkar kuma rura wutar da akeson mutuwa fetur ne,
a daren nan yazo yasami Baban ku da batun,
ya ce yanason kije kirika yi masa aiki a gidan sa sannan kuma zai rika biyan albashi wan da acikin kud'in da yake bin Baban ku za a rika zarewa."
hannunta Mama ta dad'a rikewa da kyau kana taci gaba
"SEEDRAH mutuncin Baban ku da kike son karewa tanan ne zakibi domin dad'a  kare masa mutunci da kimarsa,
har idan kika bijirewa hakan tamkar kin dad'a bada kofar da Usman zaizo yarika ciwa Baban ku mutunci ne daga karshe kuma ya karb'e gidan nan,
 mu bazama yawon gidan haya haka zamuyi ta tsugune tashe,
kisawa ranki neman kud'i zakije domin ki kare mutuncin mahaifinki, ai wannan wata kofa ce muma da muka samu ta in da zamuyi aiki a karkashin sa sannan kuma musamu mubiya wani abu daga cikin bashin da yake binmu,
ko kin fi so yaci gaba da zuwa yana tozarta mahaifin kine iye SEEDRAH?."

Tuni hawaye yashiga sauka a idanun ta. bakinciki da takaici sune suka sata zubda kwalla wai ita ce zata je gidan wani amatsayin 'yar aiki wanin ma S.MAN mutumin da tafi tsana a rayuwarta.

Allah kad'ai yasan manufar sa na son ta kasance 'yar aikin gidan sa,
tama rigada da tasan wani tozarcin yake shiryawa Baba.
kai ta girgiza tace
"Bazai yuwu ba bazan tab'a zuwa karkashin sa nayi aiki ba,
ko da ace kuwa shi yafi kowa kud'i a duniya bazan je gidan sa a matsayin 'yar aiki ba, idan aiki kuke so nayi to dan Allah Mama ga gidajen masu kud'i da yawa ku turani can narikayi musu wanke-wanke da shara da wanki kai harma da girki,
murika tara kud'in ana rage masa bashin sa."
"SEEDRAH kina tunanin albashin da za a rika biyanki a wani gida dan kina wanke-wanke da shara zai bada wani kwakkwarar gudumawa ne wajen biyan bashin da Usman ke bin Baban ku,
kinsan kuwa nawa yake binsa to ko albashin gwamnati kika fara karb'a sai kin b'ata tsawon lokaci mai nisa kafin yakai adadin kud'in da yake binsa,
to amma tun da shi yace da kansa zai rika cirewa cikin kud'in da yake binsa shike nan wata kila wata rangwami ya yi niyyar yi masa,na samun saukin biyan bashin da yake binsa."

Duk yan da Mama taso SEEDRAH ta amince sam taki, dan acewarta dataje tayi aiki a gidan S.MAN gara taje tayi sharan titi.
kwana biyu a na abu guda,
Baba Mama Umma kullum sai sun tasata gaba. su Halimatu kuwa cewa sukayi tun da taki amincewa su zasu je, musamman Suhaital da wutar kaunar S.MAN ke balbalar ta har kayan ta ta had'a ta ce zata tafi gidan nasa,
Baba ne ya hanata dan bai mance da wacce S.Man d'in ya ce ita zata je aikin ba.

a daren ranar kwana na biyun kiran S.MAN yashigo wayar Baba,
yana d'agawa ya sinkayo muryarsa yana fad'in
"Tun da ka kasa sata tazo to ni bazan kasa zuwa karb'ar gidana ba, duba takardun gidan ka gani anya suna tare da kai kuwa."
yana gama fad'in haka ya kashe wayar.
da sauri Baba ya mike yaje in da takardun gidan suke adane, wani irin bugawa kirjinsa yayi lokacin da yaga basa gurin.
bincike yashiga yi cikin d'akin ta ko ta ina amma babu su babu alamun su.
ya fito daga d'akin sa yanufi d'akin Mama har yana cin karo.
SEEDRAH dake cikin d'akin tana kad'ewa Mama gado zata kwanta ta mike da sauri ganin yanda yashigo d'akin.
Mama ma mikewar tayi tana tambayar sa lafiya.
Baba ya ce "Ina kuwa lafiya Usman ne yakirani yanzu, na tabbata har idan gobe yasa kafarsa a gidan nan to tabbas munbar gidan nan kenan dan kuwa ina da tabbacin takardun gidan nan suna hannunsa dan basa in da na ajiye su, bansan ta yadda akayi suka shiga hannunsa ba, maganarsa ya tabbatar min da suna hannunsa."
Maganar Mama taji ta na fad'in
"Shike nan SEEDRAH tun da bazakibi maganar mu ba abin da yafi tozarci da cin mutunci Usman zaici gaba da zuwa yana mana tun da haka kika zab'a."

da sauri tashiga girgiza kai tana fad'in
"Zanyi zanyi aikin zanje gidansa nayi aiki a matsayin 'yar aiki dan na kare kima da mutuncin mahaifi na, zanyi."
takuma fad'a tana sakin bedsheet d'in da take shinfid'awa ta fita da sauri zuwa d'akin su.

Wardrobe ta bud'e gefen da kayanta yake ciki ta janyo wani akwati wanda shima nata ne tashiga ciro kaya tana karawa cikin na akwatin cikin sauri, yayin da takejin zuciyar ta ya bushe tangaras ta sawa ranta zataje tayi aiki tukuru dan ta tseratar da mahaifinta daga tozarcin S.MAN bama shi ba har wanin sa.
Suhailat dake zaune tana kallon yadda take  tura kaya cikin akwatin, ta yamusa fuska tare da fad'in
"Tun da ke bakya bukatar zuwa basai abar masu bukata suje ba kamar S.MAN zai bukaci aje masa aiki wai kiki zuwa, nifa ko gidan nasa yace nakoma gaba d'aya narika bautatawa gidan ko bazai biyani ba wlh da gudu zanje ganin sa ma kad'ai yabiya kud'in aikin da zan masa."
bata kula ta ba sai aikin tura kayan ta take cikin akwati tana gamawa tarufe ta d'au mayafin ta taja akwatin tayi waje.

A tsakar gida taga su Baba da Mama Umma duk a tsastsaye,
ta dubi Baba ta ce
"Baba na shirya ka kaini."
Baba ya dubi agogon wayarsa ya ce
"Goma da rabi ina ga kamar dare ya yi mubari sai gobe da safe."
kai kawai ta gyad'a taja akwatin zuwa d'akin Mama ranar a d'akin ta kwana.
washegari da sassafe Baba ya d'auketa a mota da kayanta suka d'au hanyar gidan S.Man.
suna isa ya yi hon maigadi ya wangale masa get yashiga ya faka a gefe, SEEDRAH ta fito Baba ya fito tare da ciro mata akwatin ta.
bin gidan tayi da ido wan da tsaruwan sa yakai tsaruwa,
"Ga gida har gida amma babu mutum."
tayi maganar a kasan ranta tare da yamusa fuska a fili tana kuma murgud'a baki, kamar S.Man d'in ne a gaban ta.

Maigadi yakaraso inda suke da sauri suka gaisa da Baba kana ita ma ta gaida shi.
maigadi ya ce
"Oga bai tashiba tukun amma yasanar min da zuwan ku dan haka zaku iya shiga daga ciki, ke ce 'yar aikin ko?."
ya nuna SEEDRAH
Baba ya ce "Eh.eh.. itace eh itace."
kai SEEDRAH tajinjina wato ma tun kan tazo yagama yad'ata wai itace yau ake cewa 'yar aiki.
Baba ya ce
"A'a ita ce zata shiga ni zan koma daga nan tun da yana bacci, maza shiga ciki SEEDRAH, ni zan wuce kasuwa."
kai ta gyad'a maigadi yad'au akwatinta yana gaba tana biye da shi, Baba kuma yaja motar sa ya yi gaba.

Tsintar kanta tayi cikin wani dankararren parlour mai kyau da tsaruwa,
maigadi ya aje mata akwatin ta cikin parlour'n ya na fad'in
"Ki zauna ki jira fitowar Oga."
kai ta gyad'a tana zama kan d'aya daga cikin dankararrun kujerun parlour'n kana maigadi yayi waje yana jawo kofar parlour'n.
a hankali tashiga bin cikin parlour'n da ido sosai parlour'n yatafi da ita matuka ta shagalta da kallonsa.
tana nan zaune tana zuba idon ganin fitowar sa amma shiru, tashafi tsawon awanni biyu zaune amma babu alamarsa.
tsaki takuma ja akaro na sau ba adadi a fili ta furta
"D'an rainin hankali sai kace wani mai sarauta da sai an wani zaman jiran fitowarsa."
kwafa tayi tare da kad'a harshe yabada sauti.
zuwa yanzu ta gaji da zama sai ta gyara kan doguwar kujerar da ta ke kai tad'an kishingid'a.
tana nan zaune harta fara jin kiraye-kirayen sallar azahar, ta mike tare da sakin doguwar hamma had'e da mika tare da yin salati, gajiya junwa duk suke tare da ita.
waige-waige tashiga yi tana niman ta in da bayin parlour'n yake taje tayi al'wala.
can idanunta ya sauka kan wata kofa dake gefe shi kad'ai, ta nufi kofar dan shi take tunanin zai iya kasancewa toilet.
a hankali ta murd'a handle ta tura kuwa taga toilet d'in ne, tsaf-tsaf yake babu datti sai kamshin turaren toilet mai dad'i yake, tashiga tayi al'wala tafito.
akwatin ta tabud'e zaciro hijabi kana ta rufe, ta zare d'ankwalin kanta ta shinfid'a ta gabatar da sallar a kai.
ko da ta idar jingina tayi dajikin  kujera tana tasbihi a hankali da 'yan yatsun ta.
idanunta ne yasauka kan kwalin sigari dake kan kujerar da take jingine da shi,
cikin jin kyamar abin ta mike tana yamusa fuska ta d'aga waya da gyalenta dake kusa da shi ta ajesu can gefe.
tad'au rimut d'in t.v da tagani a gun tashiga ture kwalin tabar cikin jin kyama ga yan da take ture abin zaka san bam bata kaunar hannunta ya tab'a shi,
ko da ya fad'o kasa kusa da kafarta tayi d'an tsalle ta masa gefe.
kana ta mika hannunta dake rike da rimut d'in ta tura shi kasan kujera.
aje rimut d'in tayi tare da rike kugu ta sauke numfashi kamar wacce tayi wani babban aiki.
"Mttsss." taja dogon tsaki kana ta koma ta zauna.
zaman ta baifi da minti 5 ba tajiyo taku daga matattakalar bene
a sannu ta waigo da dubanta izuwa gurin.
yana sanye da jallabiya kalar ruwan madara yayi kyau sosai cikin rigar.
da d'an sauri yake saukowa yana kuma duba tsadadden agogon dake d'aure a hannunsa.
yanda yake sauka dasauri cikin zafin nama irin na zaratan maza, lallausar gashin kansa daya sha gyara da wani  d'an a don aski irin na 'yan kwallo iska ke kad'ashi yal-yal.
cikin hanzari yakarasa sauka daga step's d'in jin ana fad'in sahuu daga masallacin da ake jiyo sautinsa rangad'au a cikin gidan.
yanufi kofa batare da ya kalli cikin parlour'n ba bare yama san da wata halitta agurin.
SEEDARAH ko baki bud'e tabi bayan sa da kallo cikin takaici tafurta

"Rainin hankali nashafe tsawon lokaci zaune a nan ina zaman jiransa sannan yafiyo ya yi tafiyar sa,wato ma nacigaba da zaman jiran nasa kenan, ai wlh bai isa ba idan ban d'au jakata nayi gaba abina ba."
d'an shiru tayi tana tuna tofa idan ta tafi tafiyar nata zai shafi Baba, da tunanin nan takuma gyara zaman jiransa.

S.MAN bai shigo gidan ba sai wajen karfe 2 na rana, tana nan zaune cikin parlour'n ya turo kofa ya shigo.
a sannu yatako izuwa cikin parlour'n
ya zauna kan kujerar dake fuskantar ta,
kafarsa d'aya ya d'aga ya d'aura kan d'aya.
yayin da ya maida bayan sa jikin kujerar yashiga kad'a kafar a hankali.
kana ya d'au rimut ya kunna t.v tare da mai da idanunsa kan t.v
SEEDRAH ta cika har wuya kiris ya rage ta fashe ganin rainin hankalin nasa nason yin yawa yaganta sarai bawai bai gantaba amma yayi buris da ita kamar baisan da wata halitta agurin ba.
kwafa tayi a fili tad'an ja guntun tsaki kana ta ce
"Kafad'i abin da za'ayi maka idan kuma babu na tattara nayi gaba abina."
yatsa ya d'aura kan bakin sa ya ce
"Shiiiiit ni zan yi magana ba ke ba dan nan fadata ce........"!

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci  na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna ƘARSASHI kada ku manta kafin zuwan ƘARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗  ƘARSASHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciya salon labarin na daban ne. ku dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa ƘARSASHI! ƘARSASHI!! ƘARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08088110090 ko 08034690723_

*________________________________________*

*🌈🇰 AINUWA 🇼RITER'S✍🏼*
*🅰 SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*________________________________________*
```

Zaman sa ya gyara tare da kuma maida idanunsa kan t.v yana cigaba da karkad'a kafa.
SEEDRAH ko kallon shekeke tabisa da shi tare da yamutsa fuska.
sai da ya d'au tsawon mintuna 20 zaune batare da ya kuma cewa komai ba ya yin da idanunsa kuma ke kan t.v har lokacin.
kamar an zamure sa ya sauko da kafarsa saman lallausar carpet d'in dake malale tsakiyar parlour'n, yazamo bakin kujerar da yake kai yashiga nunata da yatsa sannan yasoma magana cikin kakkausar murya

"Tun da nake babu wani wan da yatab'a tsayuwa a gabana yana fad'a min son ransa a kaina sai ke da bakifi cikin kokali ba,
ko uban naki bai isa ya tsaya gabana ya yi gigin gayamin bakar magana ba,
shiyasa nasashi da kansa yakawo min ke domin nakoya miki tarbiyya dan naga karancin sa atare da ke,
me ma kika ce?, d'an shaye-shaye ko!."
yafad'a cikin tsawa da har sai da ta d'an zabura ta matsa baya.
hannu yacigaba da nunata da shi ya yin da yakad'a yatsun sa suka bada sauti
"Zan nuna miki halin d'an shaye-shaye sai na kunttatawa rayuwar ki sai kinyi danasanin kasantuwar ki a yanzu,
sannan ki sawa ranki bakima sanni ba babu wata alaka sakani na da ke, ke kawai 'yar aiki ce a gidan nan."

Tarazana da jin kalaman sa sai dai sam bata bari ya fahimci hakan ba, tayi kokarin kawar da tsoronta ta hanyar tattaro jarumtarta had'e da tsiwar ta ta shimfid'a su kan fuskarta.
Kafad'a ta d'aga alamun ko oho
kana ta wasa masa wani kallo sannan ta ce
"Kada kayi gigin aibanta mahaifina a gabana dan ko wuka aka kawo sa kan wuyata bazai bani tsoro na lamunce cinmutunci wa mahaifina ba,
tarbiyya kuwa nasame sa dai-dai gwargwado sai dai godiyar Allah shiyasa ma nake tafe da albarka ta,
yaushe tarbiyyar ta ishe ka da zaka bani,
kaima bawata tarbiyyar bace gare ka,
 da kana da ita da bazaka rika aikata irin abubuwan da kake aikatawa ba,
sannan kuma ni dama ban sankaba idan dama dawata alaka na dangantaka sakanin mu kajima da warwareta tun ranar da na fahimci rashin darajawarka ga mahaifina, babu wata alaka sakanin mu kai da ni da duk wad'an da mukafito uba d'aya kamar bare ne wad'an da ke tafe a kan titi, kaga babu wata alaka sakanin su,
gidan nan kuwa nazo ne amtsayin 'yar aiki zanyi aiki tukuru domin dawo da kimar mahaifina, zan yi aiki a karkashin ka ta hanyar biyana albashi karike kud'in da kake bin Baba."

Wani irin murmushin takaici ya sake a zafafe ya mike tsaye ya d'aga kafa zaiyi ball da ita, sai kuma ya fasa, ya tsunkuyo tare da shako wuyarta da karfi, har sai da idanunta suka firfito,sannan yasoma magana cikin huci

"Zan azabtar da ke ta yadda idan nayi magana baki isa ki amsa min ba!,
a karamin tunanin ki kina sammanin ko shekara goma zakiyi kina min aiki zai fanshe kud'in da nake bin Alhj Musa ne,
million 30 nake binsa ba dubu talatin ba!!."

D'an sassauta shakar da yayi mata ya yi ganin yanda take ta fafutukar neman numfashi, kana yazare hannunsa a wuyanta tare da angizata tagaru da jikin kujera.

SEEDRAH kuwa da gab'aya ta d'auke wuta tayi saurin dafe wuyanta inda take ji kamar ba a jikin ta yake ba dan tsananin azaba, ta janyo numfashi dakyar tana mai da shi.

Cikin muryar fushi sosai ya ce
"Sai na rage miki numfashi duk ran da kika kuma tsayuwa a gabana kina fad'a min maganganun da suka fito daga karamin kwakwalwar ki!."
ya juya da sauri yanayin yadda yake taku kad'ai zai tabbatar maka da fusatar sa afili dan hatta cikin parlour'n amsa sautin takunsa yake, dip-dip-dip! haka yake tafiya kamar namijin zaki cike da KARSASHI!.
can gefe cikin parlour'n in da
na'urorin motsa jikin sa suke ya nufa,
cike da zafin nama yashiga wujijjiga jikinsa bisa na'urar yad'au tsawon mintuna 30 kafin ya sakaita motsa jikinsa ya sauka.
fridge dake zaune gefe a gurin ya bud'e ya d'au gorar ruwa mai sanyi, kan kujerar silve da suke jere a gurin ya zauna yabud'e gorar tare da d'aura shi kan lips d'in sa.
saida ya shanye ruwan duka kafin ya d'ago gorar tare da yin wurgi da shi cikin parlour'n.
numfashi yashiga maidawa a hankali yayin da yake share gumin da yake tsatsafo masa da wata karamar towel,
ya zaro sigari a aljuhunsa ya kunna yashiga zuka da d'an sauri-sauri.

A razane SEEDRAH ta d'ago jin fad'uwar abu dan har lokacin tana cikin tsoro, bakin nan nata ya mutu musurus sai zazzare ido take, dan har lokacin bata dawo hayyacin ta daga shakar da yayi mata ba.

yad'au tsawon mintuna 10 zaune sai a lokacin yaji zuciyarsa ya d'an sanyaya.
ya mike a sannu ya jefar da ragowar sigarin hannunsa saman wani table dake gurin, kana ya tako cikin parlour'n,
ya zauna kan kujerar da d'azu ya tashi.
kasa tayi da idanunta,
shiko murmushi mai sauti ya yi tare da shafa d'an karamin gemun sa irin wan da 'yan kwallo suke bare,
"Gargad'in ya shigeki kenan bakiga komai ba ma tukun."
ya yi maganar idanunsa a kanta.
lumshe idanunta tayi tare da kuma bud'e su a lokaci guda tad'an tauni gefen lips d'in ta.
magana ya soma ya yin da idanunsa ke kanta

"Gargad'i game da aikin gidan nan ina mai tabbatar miki da duk randa nasami wata kusku ranar zaki fuskanci fushi na,
kaf fad'in gidan nan daga sama har kasa kama daga cikin kowani bedroom's da bathroom's zuwa parlourn sama da kasa zaki rika gyara shi akowata safiya da maraice, girki safe rana dare,
wankin kaya, sharar farfajiyar waje baiwa fulawa ruwa wankin mota, sune aikin ki,
sannan kuma da karfe 11 nake tashi daga bacci kuma ina tashi nake bukatar abin da zansa wa cikina, kada ki kuskura lokacin ya wuce batare da kin tana da min abinci na ba,
sannan kuma brekfast a sama nakeyi sauran lokutan cin abinci kuma a kasa,
da karfe 11 nan kuma ki tabbatar da kinzo kin gyara min d'aki zuwa bathroom d'ina kafin gyaran kawani bedroom's,
idan kika kuskura aka sami matsala aduk cikin abun da na lissafa mikin nan to ina mai tabbatar miki
Alhj Musa shi zai fuskanci matsala!,
karfe 11 kin gama komai ko minti 1 kika kara a kai to kiyi kuka da kanki."

Shiru tayi tana nanata ayyukan daya lissafo mata a ranta, sai kace tazamo jaka to ma taya zatayi ta iya duk wad'an nan ayyukan daga asuba zuwa karfe 11,har da aikin da yakamata mazane suyi duk dasu zatayi.
kai ta jinjina zatayi bauta ko dun ta tseratar da mahaifinta daga tozarcin S.MAN.

Maganar sa tajiyo yana fad'in
"Da nayi niyyar can waje kusa da d'akin karnuka zaki zauna kirika shigowa kina aikin,to amma kinci albarkacin zan iya bukatar abinci cikin dare dan haka ga d'aki can kishiga kizauna ciki."
ya nuna d'aya daga cikin d'akunan cikin parlour'n.
kwayar idanunta ta juya izuwa kofar d'akin da yake nuna mata kana ta dawo da kallon ta a kansa sannan ta ce
"Nawa ne albashin aiki na?."
"Me yasa sai kin sani."
"Ko aikin gwamnati kaje nima ka samu ana sanar maka da iya albashin da za a rika baka, ka d'auka hakanne,
zan fara lissafi daga kan yau da zanfara aiki, nakuma san adadin hakkina da za a rika cirewa cikin bashin da kake bin Babana."
ido ya bita da shi wato bakin ta dai bazai tab'a mutuwa ba. ya ce
"Idan kika masa da tambaya amsar ga Alhj Musa zai isa, tashi ki b'ace min da gani, ki kai jakarki ciki kifito da shirin fara aiki."
bata kuma magana ba jin ya sanyo Baba cikin maganar tasan ba mutunci gareshi ba sai ya iya zuwa yaci mutuncin Baba.
ta mike a hankali taja akwatinta tanufi kofar d'akin daya nuna mata.
ta tura kofar a hankali takusa kanta ciki, a hankali tashiga takowa cikin d'akin yayin da take bin d'akin da kallo.
d'aki ne babba komai na bukata yana ciki,
kama daga lafiyayyen gado babba da wardrobe wan da yacike b'arin bango guda, a gaban

gadon wata kujera ce ta alfarma t.v manne jikin garu-bango yana fuskantar gado ga fridge a gefe bedside da ramb'asheshen mirro, da dai sauran su.
kayan d'akin duk irin na kasar waje tsaruwar sa yakai tsaruwa,
sai dai d'akin yad'anyi kura alamar dai babu mai rayuwa cikin sa.
a hankali ta isa ta aje akwatin ta kana ta cire mayafin kanta.
nan ta shiga kad'e d'akin ta gyara shi tsaf ta goge ko ina, kana ta sauya zanin gado data gansu jere cikin wardrobe dan na kan gadon shima yayi kura.
ta d'auki wan da ta ciren ta shiga bathroom dan ta wanke, nan ta tadda washing machine ciki, shima kansa bathroom d'in abin kallo ne dan kuwa yasha kayan alatu kamar ba band'aki ba.
da washing meshing d'in tayi amfani wajen wanke bedsheet d'in,
takuma yi amfani wajen busar da shi da goge shi, kana ta wanke bayin tsaf, sannan tayi wanka tare da d'auro al'wala ta fito.
tana fita ana kiran sallar la'asar tagabatar.
ko da ta idar akwatinta ta bud'e ta ciro kayayyakin ta tashirya su cikin wardrobe dan tagama sawa ranta zatayi zaman aikin da zata fanshi mahaifinta duk wuya duk rintsi.
tana saka akwatin cikin wardrobe taji ana bugun kofa sai kuma muryarsa data jiyo ya na fad'in
"Ba kwanciya yakawo ki gidan nan ba maza ki fito."
tsaki ta ja ta ce
"Sai kace kwanciya akace masa nayi."

Ko da ta fito parlour baya nan ciki, nan ta shiga tunanin ta in da zata fara.
nan ta talub'o kichin ta shiga
tasoma kiciniyar d'aura girki cikin awannin da basu fi uku ba ta shirya lafiyayyen girki, kan kace me gaba d'aya gidan yakaure da kamshin daddad'an girkin ta.

S.MAN da tun fitar sa bai dawo ba sai daf magriba yana sanya kafarsa cikin parlour yashaki wani daddad'an kamshi ba shiri ya lumshe idanunsa yana mai dad'a shakar kamshin.

SEEDRAH nagama gyara kichin d'in ta tarkaso kulolin data shirya abincin ciki tafito.
jin karar bud'e kofa yasashi bud'e idanunsa tazo tawuce ta gaban sa zata ta nufi dinning. ya ce
"Ke-ke-ke tsaya waya baki ikon girka abin da kikaga dama batare da kin tambaye ni ba, me ma kika girkan tukun?.
cigaba da tafiyar tayi batare da ta tsaya ba ta ce
"Idan kazo ci zaka gani ai."
ta haura dinnig ta aje tray'n data jero kulolon ciki, gani ya dumfarota da sauri yana fad'in
"Ke ni kike cewa haka?." da sauri ta sauko daga kan dinning d'in ganin yana ta kokarin zuwa inda take yana kokarin cafko ta aiko da sauri cikin had'awa da gudu tashige d'aki ta mai da kofa ta rufe.
numfashi ta sauke tana fad'in
"D'an rainin hankali kabar kakuma sa hannu a jikina."

Shiko bayanta yabi da kallo tare da yin kwafa ya haura dinning, in da kamshin girkin ke ta fisgarsa.

kular farko ya bud'e wani kamshi ne yabigi hancinsa babu shiri ya lumshe idanunsa ya yin da yaji yunwar cikin sa yad'a karuwa.
had'edden jalof ne dayaji busasshen kifi da nama da kayan ganye sai fidda sihirtaccen kamshi yake.
d'aya kular ya bud'e ferfesun kaza ce dataji kayan d'and'ano dana kamshi, tanuna luguf.
sai kofi mai d'an girma mai d'auke da kunun aya mai sanyi a ciki.
da d'an sauri ya zauna dan ba shakka yunwar cikin sa ta motsa.
sosai yaci abincin cikin matukar jin dad'in sa, yana ci yana tsiyayar kunun ayar nan yana korawa da shi.
sai da yacika cikin sa tam sannan ya mike yad'au kular ferfesun kazar had'e da kofin kunun aya ya haura sama da shi..

SEEDRAH kuwa bata kuma fitowa ba sai wajen karfe goma na dare nan ma sai da ta tabbatar da babu motsin sa cikin parlour'n.
ta wuce kitchin ta zubo abinci ta koma d'aki.
tana gama cin abincin kiran Kamal ya shigo wayarta ta haye gado suka shiga soyawan su...

Washegari tana idar da sallar asuba ta fito
can gurin motsa jikinsa ta hangosa yana ta faman gudu bisa na'ura.
hararar bayan sa tayi a fili ta furta
"D'an wahala kamar wanda akasa dole Allah ubangiji yasa ka fad'i ka karya kafa da kugu, ko idan kazo d'aga wancan katon karfen yafad'o ma a kirji."
takarashe maganar da jan guntun tsaki had'e da murgud'a baki kamar yana gaban ta.
ta shige tafara aiki.
gyaran parlourn kasa ta fara zuwa cikin bedroom's d'in cikin parlour'n kana ta wuce kitchin tashiga kiciniyar had'a brekfast.
tana kammalawa tashirya masa nasa kan tray, da sauri ta nufo waje ganin lokaci nata tafiya.
ko da ta fito daga kitchin baya gurin motsa jikin, da sauri tashiga haurawa kan steps har ta kai karshe, kana ta bud'e kofar dazai sadata da parlour'n sama da sallama ta shige ciki.
cak ta ja ta tsaya bakin kofar.........!

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna KARSASHI kada ku manta kafin zuwan KARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 KARSASHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciya salon labarin na daban ne. ku dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa KARSASHI! ƘARSASHI!! KARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08088110090 ko 08034690723_

*______________________________________*

*🌈🇰AINUWA 🇼RITER'S✍🏼*
*🇦SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association
```

*___________________________________*

page 13

Ganin tsaruwan parlour'n mai kamada aljannar duniya shi yasata jan burki a bakin kofar.
idanunta ya sauka kan katon hoton sa da ke manne jikin garun parlour'n yana sanye cikin kayan kwallo, a tsakiyar filin kwallo ya d'aga kafarsa zaiyi shot da ball aka d'aukesa a hoton, yayi matukar kyau sosai.
idanunta ta janye daga kallon hoton nasa da kuma tsararren parlour'n nasa.
sai kuma ta d'an batsar tana tambayar kanta to ma ina wani abun burgewa a wannan gida da mai gidan yakansace mutum mara d'a a.
taja gajeren tsaki kana tasoma takowa izuwa cikin parlour'n.
ta isa ta aje tray d'in saman table d'in sakiyar parlour'n.
nan tasha d'ammara da gyalenta ta shiga gyara parlour'n.
cikin mintuna kalilan ta tsaftace shi tas duk da dama dai bawani datti yayi ba.
tana gama gyaran parlour'n tad'ago ta na kallon kofofin bedroom's guda hud'u dake d'auke cikin parlour'n tana tunanin ta in da zata fara,
idanunta ne yatsaya kan d'aya daga cikin kofofin
wanda dizainin d'in kofar ma daban ne.
anyi rubutu ajikin kofar wan da ga dukkan alamu ba mannashi akayi ba da shi aka kera kofar.
ido tad'an tsurawa kofar tana son gane abinda aka rubuta duk da da manyan harufa akayi rubutun sai dai d'aya cikin d'aya akayisu,
kuma da yanayin kwalliya idan ma ba ka luraba zakayi zaton kwalliya ce kawai.
bata kaiga tantace ma'anar rubutun da take ji da wuya ma ta iya gane abin da ake nufi a ka bud'o kofar.
waya na sakale a kunnensa yana magana, sanye yake da singilet da 3qrt ya karaso cikin parlour'n, lokacin da yake sauke wayar a kunnen sa.
zama ya yi kan kujerar dake kusa da table d'in data d'aura kayan brekfast.
batare da ya kalli inda take ba ya ce
"Tsayuwa kalle kalle kikazo yi ko aiki?,
ai babu hutu cikin rayuwar ki acikin gidan nan, ko hutun sama da minti 10 bana kaunar naga kinyi sa a cikin gidan nan,
wuce yanzu kije ki gyara min bedroom da bathroom sannan ki wanke min kayana ki goge."

wucewa tayi cikin d'akin da ta ga yafito daga cikinsa batare da tace komai ba, duk yanda idanunta keta son janta izuwa kallon katafaren makwancin nasa zuciyarta kuwa yaki bada damar hakan.
duk abin da yace tayi shi tayi kafin ta fito a d'akin.
yana nan zaune in da ta barshi yagama yin brekfast d'in.
tana kokarin barin parlour'n tajiyo muryarsa yana fad'in
"Kin gama duka aikin?."
kamar bazata amsa shi ba sai kuma ta gyad'a masa kai.
"Baki da baki ne? da bazaki amsa min da bakin ki ba."
yafad'a yana jefinta da mugun kallo.
"Idan haka ka d'auka to hakan ne, ka tambaya kuma na baka amsa ai ba sai na amsa da baki na ba, amsa magana da baki baya daga cikin jadawalin aikina, sannan kuma duk abin da ka lissafo na aikina na gama ko a kwai abin da ya yi saura ne."
ta karashe maganar tana d'aga hanci sama cike da tsiwa.
da d'an mamakin jin zata iya kuma tsayuwa gaban sa yana fad'a tana fad'a dan zaton sa gargad'insa na jiya daya shakota ya shige ta, sai yaga akasin haka.
idanunta tarmazai take jera masa zance.
afusace ya mike yana fad'in
"Kin gama kike cewa kin wanke mota da zubawa fulawa ruwa da gyarashi."
ta ce "Ban iya ba sai dai ka fad'o wasu aikin a madadin su."

"Su zakiyi idan kuma ba haka ba zan kira Alhj Musa nan yazo ya yi,tun da ya iya cin bashi dole ya iya aiki ma."
"Ka iya bakinka ka dai na jefin mahaifina da miyagun kalamai zan iya jure komai amma ban da cin mutunci wa mahaifina, ai bashi hanji ne yana cikin kowa,
yafi karfin yazo ya yi aiki a karkashin ka tun ya haifa gani nan a gabanka yawuce tozarci."
ta karashe maganar da murgud'a masa baki tare da binsa da kallon sama da kasa.
batayi aune ba sai ganin sa tayi a gabanta, baiyi wata-wata ba yakai mata bugu a bakin ta da bayan hannu.
da sauri ta dafe bakin cikin jin azabar zafi.
ya ce "Fasa shi zanyi sai na fasa bakin ki aduk san da nake magana kina mayar min,
wuce maza yanzu kije ki wanke motar sannan ki gyara fulawar ki zuba musu ruwa yanzun nan ko na kirawo sa yazo yayi!."

Baya ta shiga ja yayin da ta d'ago hannuta data kai baki tana kallon d'an guntun jinin daya fito a gefen bakin ta.
shiko komawa yayi ya zauna yana fad'in
"Yanzu karfe 11 saura minti 25 mintuna 25 ne kad'ai suka rage miki, ki tabbatar da kin gama komai kafin cikar mintuna 25."

Kuma duban d'an guntun jinin dake hannunta tayi kana ta dube sa sannan ta ce
"Ba a haifowa katon gardi jaka ba wlh Allah ya'isa mugu wlh kasake kuskuran kai hannunka jikina sai kayi dana sani."

a fusace ya mike ganin haka yasata zurawa da gudu tana had'a steps tasauka a guje tayi cikin d'aki ta murza key.
a jikin kofar takasa kunnenta jin dai shiru bai biyo ta ba tabud'e kofar asulale tayi waje.

Tsayuwa tayi a farfajiyar gidan tana karewa fulawowin da sukayiwa gidan kawanya kallo,
wai su zata zubawa ruwa sannan ta gyara
"To ma taya?." tayi wa kanta tambayar, ga kuma motoci can guda uku cikin parking lot
wai duk ita zata had'a ta wanke su.
kugu ta rike saita kalli motocin takuma kalli flaw's d'in.
sai kuma a sannu tashiga takowa zuwa in da ta hangi tiyo da irin abin da ake rage tsawon fulawa da shi, ta d'au abin tashiga yanke kan flaw's d'in nan sai da ta kusa cire rabin na gurin, kana ta yi gaba shima sai da ta cire ganye jiki tas..
mai gadi dake zaune can bakin get yahango abin da take da gudu ya taho yana rabka uban salati da fad'in
"La-la-la waya saki wannan aikin wace b'arna kike yi haka, kin san kuwa daga ina oga yataho da wannan fulawar? tun daga kasar turai ya taho da su, shine zakiyi musu aski irin haka waya fad'a miki haka akeyi."
ta ce
"Oho ba bashi ya ce a gyara ba."

S.MAN dake sama yajiyo salatin da maigadi yake rabkawa ta windo ya leko ya hango su,
ido ya waro kan b'arnar data tabka masa cikin d'aga murya ya ce
"Ke!."
maigadi yad'aga kai sama yana fad'in
"Oga basai ma ka sauko ba
amma dai tayi b'arna wanna ganyen turai d'in tasha tsinka yo ko kwad'o zakiyi da shi ai iya kaci."
ganin ya rufe glaas d'in windon tasan saukowa zaiyi ai da gudu tayi ciki, tana shiga parlour shikuma yana step d'in farko na sama yana kokarin sauka.
kafin ya sauko tuni tayi cikin d'aki ta murza key.
kofar yashiga bubbugawa da karfi yana fad'in
"Ki bud'e kofar nan!.
ta ce " Wlh bazan bud'e ba bazan bud'e kayi min bugun uban wani ba, ni ba 'yar ka bace kajira ka haifa tukun ka buga."
bugun kofar yake yana cigaba da fad'in
"Na rantse idan kika shigo hanuna sai na ɓaɓɓalla ki na taraki anan."
"Ai wlh baka isa ba zakaga gatana kuwa, aiki ka sani kuma nayi maka baka da bakin wata magana."
naushin kofar yayi da kafa kana ya juya yabar jikin kofar.
SEEDRAH ko ido ta zazzare dan ta gama zaton kofar ta b'alle dan ba naushin wasa yayi wa kofar ba.
jin shiru bai kuma wata motsi ba sai ta koma bakin gado ta zauna tana mai da numfashi da fad'in

"Haka kawai dukan da bazaka iya ramawa ba,
ai wlh da baka fito bama da kaf saina yanke fulawan nan nazubar da su, ba aiki kace ba."

(AFWAN NASAMI KORAFI GA WASUN KU SUN CE SU BASUSAN MEYE GARU BA KUMA DUK LITTATTAFAI NA DA KALMAR NAKE YAWAN AMFANI TO YA ZANYI TUN DA HAUSAN GARIN DA NAKE KENAN KUMA NA SABA AMMA ZANYI KOKARI  ZAN RIKA RUBUTO MUKU IN DA ZAKU FAHIMTA. GARU BANGO KENAN KO KATANGA SHIMA DUK GARU NE KURIKE SUNAN DAN BAZANYI MUKU ALKAWARI A KODA YAUSHE ZAN RIKA SAKO MUKU BANGO BA KU DAI RIKE SUNAN SA GARU KAWAI DAN YA KAMA BAKI NA)

Ranar SEEDRAH wasan b'uya tashiga yi da S.MAN ko ai ki take idan taji motsin sa saita gudu d'aki ta kulle kanta ciki
a haka suka kwana.
washegari kuwa data fito ta hango sa yana gurin motsa jiki, sai ta fasa gyaran parlour'n ta sulale tayi kichin sai da ta kulle kofar kichin d'in kafin ta soma aikin.
ko da ta gama ta bud'e kofar a hankali ta leko kanta can ta kuma hango sa yana ta uban gudu bisa na'ura, cikin sand'a ta fito a hankali tahaura sama.
tana aje kayan brekfast d'in ta shiga gyaran parlour'n da sauri-sauri tana kammalawa ta shige bedroom nan da nan tagama ta fito da sauri tanufi kofar da zata sauko kasa.
wani irin wawan burki taja sakamakon ganin sa ya sako kai  zai shigo.
tad'an tsorata da had'uwar da batayi zato ba sai kuma ta wayence ta had'e fuska ta masa gefe ta bashi hanya dan ya wuce.
hannuta ya cafko da karfi ya murd'e hannun.
tasaki uban kara tare da fad'in
"Wayyo Allah na wayyo hannuna ya karyamin hannu."
takuma sakin wani kara jin yanda yake cigaba da murd'e hannun wane zai karya shi.
ido ya zubawa fuskarta batare da ya saketa ba burin sa kawai yaga hawaye cikin idanunta, duk ihun da take d'in nan kuwa babu d'igon hawaye a idanunta.
sulalewa kasa tayi yabita batare da ya saki hannun nata ba yasaka guiwansa d'aya a kasa yana mai cigaba da mud'e hannun nata.
cike da jin azaba tafashe da kuka cikin muryar kuka da tuni hawaye yashiga zubowa  idonta ta ce
"Wayyo Allah na wayyo hannuna wayyo Mama ya b'allamin hannu, wlh idanka karya ni kaima sai an karya ka."
sakin hannun nata yayi kana ya mike tsaye tare da karkad'e hannunsa ya dube ta da kyau kana ya ce
"Da ma burina naga hawaye a cikin wad'an nan marasa kunyar idanun naki, duk san da kika kuma yi min b'arna acikin gidan nan sai na sauya miki kamanni."
yajuya ya shige d'aki ya yafito rike da key d'in mota yafice ya bar gidan.
da kyar ta iya mikewa ta sauko kasa, a parlour'n kasa ta zauna bata iya shiga d'aki ba tana tallafe da hanunta datake ji kamar baya amfani.

tajima sosai zaune a gurin sai da taji hannun yad'an rage mata zugi kana ta mike ta shiga d'aki.
kwanciya tayi a kan gado ta d'aura hannun kan pilo.
wasu zafafan hawaye ne zuka zubo mata takai hannunta mai lafiyar ta share haushi da tsanar S.MAN cike fal cikin zuciyarta
"Lallai wan nan zai iya kashe mutum dan babu imani atare da shi."
tayi maganar a kasan ranta, tana nan kwance a haka har baccin wahala ya d'auke ta.

Ko da S.MAN yafita gidansu ya je, suna zaune a parlour gaba d'aya hankalin Ummi na gare sa.
ta d'an numfasa kana ta ce
"Amma Usaman meyasa ka zab'i ajiye 'yar aiki a gidanka akan mata?, madadin kayi aure ka ajiye mata agidan sai ka d'auko wata 'yar aiki, duk da ita d'in 'yar uwar ka ce amma ai itama nan bada jimawa ba zata iya yin aurenta,
shikenan sai dai karika d'auko 'yan aiki bazakayi aure ka ajiye mata cikin gidan ka ba."
"Bana da lokacin ajiye mace yanzu duba da abun da nasa gaba, Ummi bazai yuwu ma nayi aure yanzu ba har sai na nutsu guri guda."
"Usman harsai yaushe ke nan girmafa kake 'yan kwallo nawani suke da mata kuma suna tafiya ko wani kasashe, kayi aure zanfi samin kwanciyar hankali ni ma naga jikokina."
"Allah yakawo lokaci."
yafad'a yana mikewa, wai shi da baya da ko budurwa ma ake masa wani zancen aure, dan shi dai har yanzu baiga mace cikin matan da suke bibiyarsa ba.
ya yi wa Ummi sallama ya tafi...

SEEDRAH da bacci kamar kasa har wajen karfe 2 na rana bata farka ba.
S.MAN da yanzu dawowan sa daga masallaci ya yada zangonsa a parlour'n kasa,
ya zauna tsawon wasu 'yan mintuna yana daddana waya daga bisani ya aje wayar kana yakai hannu yashafi cikin sa daya fara jin yunwa. bin parlour'n yayi da ido baiga alamar wata kula na abinci a gurin ba,
ya maida dubansa can kan dinning shima babu komai.
d'an shiru yayi yana tuna tun zaman sa a nan baiji motsin ta ba ko a kichin ne, sai ya mike ya nufi kichin d'in ya leka baiga kowa ciki ba, babu kuma alamun an d'aura girki.
juyawa yayi yanufi d'akin da take yatura kofar, can ya hangota kwance kan gado tana ta sharar baccin ta.
daga bakin kofa in da yake tsaye ya ce
"Ke bacci ne yakawo ki gidan nan wa kika ajiye da zai miki girkin."
nauyin bacci irin na SEEDRAH batama san yana yi ba,
shiko ganin kamar tana jinsa tayi burus da shi ne yacigaba da magana a hatsale amma har lokacin bata ko matsa ba.
a hatsale ya tako bakin gadon yana cigaba da fad'in
"Ke wai ni sa'an ki ne ina magana kina kwance zaki tashine kosai na sauya miki kamanni a nan!."
yayi maganar cikin d'aga murya sosai kuma cikin tsawa.

sai a lokacin tad'an motsa tare da yin mika ta juya kai tare da cigaba da baccin ta dan ita bata ma san yana yi ba.
cikin matukar jin haushi yarasa ma me zai mata sai ya juya yaje in da fridge yake ya bud'e yaciro gorar ruwa mai sanyi har wani turiri yake tsabar sanyi, ya dawo bakin gadon kana yabud'e marfin gorar ya saiti dai-dai fuskarta yashiga tuttud'a mata ruwan.
a gigice ta farka tare da kwalla kara ta mike zaune tana ware ido a kansa dan ba karamin firgita tayi ba.
shiko ragowar ruwan yakarasa sheka mata a wuya ya gangara cikin kirjinta, kuma zabura tayi tamike ta saka guiwawinta saman katifa tana fad'in
"Wayyo Allah sanyi me namaka Allah bazan yafe ba."
ya ce "Idan da baki tashi ba d'aukar ki zanyi nasakaki cikin fridge d'in na kulle ki ciki, ke har kina da wani ikon yin bacci ne a gidan nan, idan na sake ganin ki kin kwanta kina bacci kamar mushe sai na sauya miki kamanni,
tukun na ma ina abincin rana?."
baki ta turo gaba tare da d'an murgud'a shi tana d'an jajjan rigarta da ruwan yasa ya lafe ajikinta sosai, har ana iya hango shatin bakin ababen jirjinta da bata saka musu bra ba, ga kuma wuyan rigar daya d'an zamo.
ya ce
"Zaki tashi kije ki d'aura girkin ne ko ya."
baki takuma turowa tare da sakar masa karamar harara ta ce
"To ka fita mana ba ka fad'a ba zan fito ai."
tayi maganar tana janyo hijabinta dake kan gadon ta rufe jikin ta.
tsaki yaja kana ya juya yafita yana fad'in
"Ki b'ata lokaci ki gani."

Sauka tayi a gadon tana jan tsaki da fad'in
"Mugu azzalumi kuma Allah ya isa."
bayi ta shige
ta tub'e jikakkun kayan tayi wanka tare da d'auro al'wa ta fito,
sai da ta gabatar da sallar azahar kana ta sauya wasu kayan sannan ta fito.
yana zaune a parlour'n rike da sigari yana d'an zuka yayin da idanunsa ke kan t.v
tazo zata wuce shi ta nufi kichin dai-dai lokacin da ya buso hayakin sigari ya ce
"Sai kinyi ra ayi ne ma kafin ki fito, aduk b'ata lokacin da zakiyi a kan wani aiki acikin kud'in aikin ki dan ko wace karya doka sai anyi mata kud'i."
kai ta kawar gefe tare da yamutsa fuska tana kore hayakin sigarin da hannunta kana ta toshe hanci da sauri tabar gurin.
sai da ta shiga kichin kafin ta saki hancin ta tana sauke numfashi, a fili ta furta
"D'an kwaya ma da ban yake."
Ko da ta gama girkin ta d'ibo ta kawo masa sannan ta d'ibi na maigadi ta kai masa kana ta d'ibi wan da zataci tayi d'aki...

Bayan kwana biyu

SEEDRAH ce zaune cikin parlour bayan ta gama duk kanin ayyukan ta tana huta gajiya. wayarta ce tayi kara da jin sautin dake tashi na musamman wan da mutum d'ayane ke da wannan sautin, murmushi ta sake tare da d'aga kiran ta

kara wayar a kunnen ta tare da yin sallama.

a b'angaren Kamal kuwa numfashi mai sauti ya sake tare da amsa sallamar kana ya ce
"Me yasa hakan?."
ido ta d'an lumshe tare da bud'e su lokaci guda takai bayan ta jikin kujera tana mai dad'a manna wayar a kunnen ta sannan ta ce
"Me ya faru?."
ya ce "Gani a kofar gidan ku Mama ta ce min wai kina gidan yayan ku yau kwana nawa ma, amma shine babu ko labari ashe duk wayar da muke da ke ma kina can da ban zo ba da baza ma ki fad'a min ba kenan."
to taya ma zatayi ta iya fad'a masa taje gidan wani aiki akan bashin da ake bin Baban ta, duk da tasan Kamal mutum ne mai fahimta amma ina bazata iya fad'a masa sirrin gidan su ba.
ta ce "Ayya wai dama bamuyi magabar ba ai na d'auka na fad'a maka nazo gidan sa ayya na sha'afa ne to gaba d'aya, ayi min afwa."
ya ce "Da nayi fushi amma yanzu na hakura."
ta ce "To godiya nake."

Nan suka shiga hirar su na kauna da soyayya cikin hirar yake tambayarta
"Wai wani yayan ku ne ma?."
ta ce "S.MAN yaron kanin Baba." ya ce
"Oh S.MAN wannan d'an kwallon ko ai ina matukar son buga wasan sa dan wlh ya iya kwallo sosai dawowan sa ma daya ciyowa Nigeria kwallo ai damu akaje a ka cashe a hall."
hab'a ta rike ta ce "Wai rawa kukayi?."
dariya ya yi kana
ya ce "Shagali ne kawai amma an d'anyi rawan ma, daga nan kuma mukaje muka buga kwallo saboda farin cikin kasarmu tayi gaba."
"Wai dan Allah kaima kana wannan aikin wahalan ne."
"Ke kwallon ne aikin wahala kinsan kwallo kuwa, to duk wanda kika gansa yana kwallo ki girmamashi daga yau ma ki kara girmama S.MAN fiye da da,
dan shi d'in a can saman-sama yake babbane."
baki ta tab'e a ranta ta ce
"Ina abin girmamawa a tare da shi mutumin da baisan darajar mutane ba Allah ya sawaka."
a fili kuwa dariya kawai tayi.
maganarsa ta jiyo yana fad'in
"Ashe ya yi aure ma amma dai auren sirri ya yi dan banji labarin ba ko a kafafen yad'a labarai, kai manyan nan fa yanzu sun dage da auren sirri babu mai sani zasuyi abunsu sululu su shige da matansu ciki,
da gaskiyarsu su killace matansu ba suyi ta nunawa duniya tana gani ba, yafi ai suyi kishin kayansu, kai nimafa irin wannan auren zamuyi dan babu wani bikin da za'ayi daya wuce walima."

d'an shiru tayi tana nazarin maganar tasa, wato shi tunani ya ke S.MAN d'in yana da mata, shi yasa ma tazo gidan nasa,
to ma taya zatayi tace masa bashida mata kuma take zaune a gidan.
maganar sa ta kuma sinkayowa ya na cigaba da fad'in
"Ki gai da Aunty'n namu watarana zaki rako ni na gaida ta idan basu koma ba, amma dai yau zaki koma gida ko?."
kai ta girgiza kamar yana ganin ta sai kuma ta ce
"A'a ba yau ba."
ta fad'a a takaice
"Sai yaushe ko sai zasu koma tukun?."
ta ce "Eh." ido ya waro ya ce
"To gaskiya bazan iya jure rashin ganin kiba tun da bansan yaushe zasu tafi ba zan dai zo narika ganin ki a can d'in, kar kumafa su d'auke min ke sutafi min dake kasar turawan nan ace sai nayi kud'in jirgin d'auko ki."
dariya tayi ta ce "Haba dai sai ka tara kud'in jirgi kenan."
shima dariyar ya yi ya ce
"Da gudu ma kuwa."
jin karar bud'e kofar parlour tasan S.MAN ne ya shigo dan haka tayi saurin cewa Kamal bari tayi wanka anjima zasuyi waya.
ya ce to. sukayi sallama ta sauke wayan dai-dai lokacin da yake karaso wa cikin parlour'n yad'an kalle ta tare da fad'in
"Zan fita yanzu kije ki wanke min mota ki goge yanzun nan."
ya wuce yafara haurawa step's, mikewa tsaye tayi sannan ta ce
"Ban iya ba."
sai da yakai karshen matattakalar sannan ya ce
"Alhj Musa kam dole zai iya dan nasan bashi da kud'in da zai iya kai gura-guran motar sa gurin wanki sai dai idan fashi zai koma so dole shi yake wanke sa da kansa, bare kuma wad'an nan motoci masu tsada wankin su ai bazai bashi wuyaba shi zai zo ya wanke su yanzu."

Cikin d'aga murya ta ce
"Ya ishe ka ka dai na kokarin rika aibanta Babana dan uba baifi uba ba."
cak yaja ya tsaya tare da juyowa kana ya maimaita kalmar "Uba baifi uba ba."
tarar numafshin sa tayi da fad'in
"Kwarai kuwa amma ka sani duk yanda kake son ka kaini bango bazan tab'a iya fad'ar mummunar kalma akan Abba ba, dan har gaba da abadan yana da kima da darajar uba agareni dan abun da ya yi Baba shi ya yi Abba, duk nasan darajar su ba kamar kai d'an kwaya d'an shaye-shaye ba."

Wani irin waro idanu ya yi kan kace me idanun nasa sun sauya kamanni,
b'acin rai fushi tafasar zuciya kake iya hangowa cikin su,
ganin yan da ya d'aga kafa cike da KARSASHI tamkar zai duro daga saman matattakalar izuwa kasa.
ai ko ta d'aga kafa dagudu kafin tace zata shiga d'aki ya iso ta ya samata kafa ta zube kasa.

bin ta yayi kasan tare da shako wuyarta.
wani irin tsoro ne ya baibayeta, idanunta tarufe da karfi dan ji take bazata iya bud'i idanunta a kansaba dan ya koma mata abin tsoro.
cikin fusatacciyar murya mai nuni da zallar tafasar zuciya ya ce
"Ni ni ne d'an kwaya d'an shaye-shaye a ina kika tab'a ganina da kwaya a ina kika gansu!."
yayi maganar cikin tsawa tare zuba mata gigitaccen maruka biyu da sai da suka d'auke mata jin ta na wucen gadi,
yashiga nuna ta da hannu yana fad'in
"Zan sauya miki kamanni sai na b'allaki na taraki anan."
ya angiza ta kanta yagaru da kasa,
ya mike ya haye sama yana huci.
fizgar numfashin ta tayi da kyar ta tattaro ragowar karfin ta ta mike zaune da kyar ta iya mikewa tsaye ta shige d'aki a bakin gado ta zube, sai a lokacin taji wani kuka yazo mata ta fashe da kukan tare da kife fuskarta jikin pilo tashiga rera kukan cike da kuna dad'acin rai.
kamar an zabure ta tamike tsaye tare da share hawayen ta tafito da sauri ta shiga kichin.
in da ta tab'a ganin soson waya taje ta d'auka ta fita ta dasauri ta nufi parking lot.
gindin pampo dake gurin taje takunna ruwa cikin boket d'in data gani a gurin ta d'auko ta kawo sa kusa da motocin,
sai da ta dubi mota mai kyan ciki kana ta d'ibi ruwa a kofi ta wasa masa wannan soson wayar data fito dashi tashiga dirza jikin motar da shi.
ta dage sosai tarika dirzan motar nan gefe da gefen sa gaba d'aya ta goga soson wayar  ta zazzana motar gaba d'aya tayi kaca-kaca da fentin motar.
mikewa tayi tana haki tare da rike kugu, ta girgiza kai tare da ciza baki ta juya da sauri ta bargurin.
tana shiga ta ganshi yasauko cikin sabuwar shiga da d'an sauri yake tafiya ga dukkan alamu dai fita zaiyi.
bin ta da ido yayi ganin duk ta jike ya ce
"Kin wanke motar ne ko ya?."
ta ce "Ah sosai ma kuwa har na gama."
tawuce da sauri ta shige d'aki, bin bayan ta yayi da kallo ganin yan da tayi saurin shiga bedroom, sai kuma ya juya yafice waje..

Tun kan ya karaso parking lot d'in yake hango motar kamar an shafa mata wani abu, da d'an sauri ya karaso gurin, wani irin waro ido yayi kan motar da yake ganin abin mamaki ajikin sa, hannusa ya d'aga ya naushi iska ya kai hannayen sa duka biyu yacusa cikin sumar kansa ya yamutsa.
sai kuma yashiga kai koma a gurin yama rasa me zaiyi.
sai kuma da sauri ya zaro wayar sa tare da lalub'o lambar Baba ya dannan masa kira
Baba ya d'aga da sallama batare da ya amsa sallamar sa ba ya ce
"Kud'in motata naira million 80 kazo ka had'a kabiya...........!

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08088110090 ko 08034690723_

*______________________________________*

*🌈K AINUWA WRITER'S✍🏼*
*A SSOCIATION🤝🏻*

{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*______________________________________*

page 14

Da sauri Baba cikin matukar shiga tashin hankali ya ce "Wata motar kuma?."
S.MAN ya ce "Motar  da 'yarka ta la'anta shi yanzu kud'in motar na fad'a maka kazo yanzu ka biya ni."
ya na gama fad'in haka ya kashe wayar sa.
Baba kuwa cikin matukar tashin hankali yafito a bujajan ganin yan da yafito daga d'akin sa hankali tashe yasa su Mama tambayar sa abun da ke faruwa, bai iya tsayuwa basu amsa ba yayi waje yaja motar sa ya yi new G.R.A gidan S.MAN.

S.MAN kuwa na kashe wayar yajuya da sauri sai huci yake yaje yarika bubbuga kofar SEEDRAH taki bud'ewa yarika buga kofar yana fad'in
"Wlh yau sai na canza miki kamanni ki bud'e kofar nan."
ta ce "Bani bud'iwa kuma ina mai tabbatar maka a duk san da ka sake kuskurin kai hannunka jikina da sunan duka ko shaka wlh karika yin na kud'in ka kenan, kad'an ma ka gani."
naushin kofar yayi dakarfi har sai da ta ja da baya cikin matukar tsoro, dan gani take kofar ma ta b'alle.
cikin fusatacciyar murya ya ce
"Kin jawa wanjan tsohon."
jin shiru bai kuma magana ba yasa ta komawa ta zauna jiki a d'an sanyaye dan tasan gurin Baba yanufa yanazu, Allah ne kad'ai yasan cin mutun cin da zai je ya yi masa.

A b'angaren Baba kuwa cikin mintuna kalilan yakawo shi gidan S.MAN yayi hon maigadi ya bud'e masa get.
yana faka motar da sauri ya fito, can yahangi S.MAN a gurin hutawan shi na musamman a cikin

gidan wan da aka kawata shi tamkar a turai.
yana zaune kan d'aya daga cikin kujerun da suke zagaye da gurin ya d'aura kafarsa d'aya kan d'aya yana d'an girgiza kafar, sigari na rike a hannunsa yana sha, idanunsa kuma suna lumshe.
da sauri Baba ya karaso in da yake yana fad'in
"Usman ina motar take ina kuma ita SEEDRAH?."
Baba yayi maganar cikin nuna tsantsar damuwa.
hayakin sigari ya zuko tare da buso shi kana ya bud'e idonsa d'aya ya kalli Baba da shi cikin kanne ido da rashin daraja ya ce
"Ka taho da kud'ad'en?."
hannu Baba ya rungume jiki a sanyaye.
S.MAN yakuma mai da idonsa ya lumshe yana fad'in
"Au na mance ashe kai fakiri ne, to ni ko fashi zakaje kayi kaje kayi kakawo min kud'ina wan da kaci bashin sa naira million 30 da kuma wacce 'yarka ta la'anta motar million 80."
Baba ya ce
"Dan girman Allah Usman kayi hakuri a ina zan sami wad'an nan kud'ad'en?."
da sauri S.MAN yabud'e idanunsa ya ce "Anya ba kaika sata ba ma kuwa? dubi yadda ta goge min mota ta b'ata shi, kai komai akayi ma da sa hannunka, duba fa dubafa ka gani."
yayi maganar yana nuna parking lot can in da motar take.
Baba ya ce "Haba Usman taya zanyi na sata tayi maka b'arna wlh sam banda masaniya a kan haka, ina SEEDRAH take?."
"Tana ciki kaje ka fito da ita dan wlh yau sai na saita mata tunani."

Da sauri Baba ya shiga ciki yana waigen motar da SEEDRAH ta goge fentin sa kamar zata sake masa wata fentin.
tun daga bakin kofa Baba ke kiran ta har ya shiga ciki.
S.MAN daya biyo bayansa yakaraso yana fad'in
"Can kofar zakaje ka fito da ita in ba hakaba kuma na b'alle kofar ni naje na same ta."
ya nuna masa kofar d'akin da SEEDRAH take ciki.
Baba ya matsa bakin kofar da sauri shiko S.Man ya haura sama.

Tana nan zaune cikin zullumi da tunanin rashin mutuncin da yanzu S.MAN yaje yake kanyiwa Baba tajiyo ana bubbuga kofa.
a d'an firgice ta mike tazo bakin kofar
Baba yakuma bubbuga kofar tare da fad'in
"Ke SEEDRAH bud'e kofar nan hauka kikayi ne wani shashanci ne wannan kin san kuwa barnan tulin dukiyar da kikayi? maza bud'e kifito nan."
jin muryar Baba yasata bud'e kofar tafito tana rarraba ido tare da turo baki.
Baba ya ce "Zonan maza."
yafad'a yana nufar in da kujeru suke ya zauna, ta karaso ta zauna kasan carpet gefe da shi.
Baba ya dube ta hankali tashe ya ce
"Meyasa hakan meyasa zaki sa abu ki goge masa jikin mota kin san kuwa kud'in motar nan SEEDRAH?, ta ina ne zan iya samo kud'in  motar nan SEEDRAH ata ina ne zan iya samo

miliyan 80 ban da kud'in da yake bina iye SEEDRAH, meyasa zakiyi haka."
"Baba ai nace masa ban iya wankin mota ba ya ce sai nayi."
"Tafi can da'alla sai kuma dan baki iya ba sai ki saka abu ki goge motar har sai kin cire fentin jikin sa, yanzu ko kud'in fentin motar ce ma a ina zan samu nabiya sa asake yi masa fenti bare kuma kud'in motar."
baki ta kuma turowa zatayi magana sukajiyo muryarsa yana sauko wa daga matattakalar bene
"Ko da kana da kud'in fentin ma bazan karb'aba sabuwar mota nake bukata."
yakaraso ya zauna kan kujera tare da d'aura kafa d'aya kan d'aya.
Baba yashiga basa hakuri kamar zai zuba guiwowinsa kasa yana had'asa da Allah da manzon sa, shiko sai wani cika yake yana batsewa daga bisani yad'aga wa Baba hanu ya ce yaje amma fa zai neme sa aduk san da bukatar hakan ta taso dan bai hakuraba.
Baba ya tafi yana mai jaddadawa SEEDRAH ta kiyaye kada wata matsala takuma faruwa.

SEEDRAH nakokarin mikewa ta bar parlour'n ya dube ta yama rasa me zaiyi wa yarinyar, yaso yimata dukan da gobe idan akace takuma b'arnata masa wani abun bazatayi ba.
ya ce "Kizauna da shirin ki dan wlh sai nayi miki dukan kud'in motata."
wani kallon sama da kasa ta bisa da shi kana ta ce
"Ni kuma wlh ka kuskura ka tab'a ni sai nayi maka b'arnar da har ka mutu bazaka manta ba, duk ranar da ka sake kuskuran kai hannu jikina sai kayi da na sani, ba wankin mota kace ba' shiyasa nikuma nayi masa wankin da zai dad'e bai yi datti ba ko gobe kakuma sani haka zan yiwa sauran motocin."
ta murgud'a masa baki tayi wucewar ta d'aki.
baki ya bud'e da mamaki yake kallonta harta shige d'aki sai kuma da sauri yabiyo bayanta yana fad'in
"Me zaki yi, me zaki iya yi?."
ta ce "Komai ma idan kuma kana ganin wasa ne to ka gwada."
tayi maganar ne cikin dakiya ganin yadda yake dad'a maso ta, ya mika hannu da zummar cafko ta, ta ja da baya tare da d'aukar plt dake kan mirro ta ce
"Idan ka kuskura ka tab'ani sai na buga maka."
murd'e ta yayi ya kwace plt d'in tare da angizata tagaru da jikin gado.
kana ya ce
"Baki isa ki b'ata min mota kici banza ba,
kinyi abakin abincin da kike ci a cikin gidan nan, dan nasan Alhj Musa bashi da kud'in da zai iya biyana b'arnan da kika min,
daga yau abinci sau d'aya zaki rika ci a gidan nan iya na safe kawai sai kuma wata safiyar, sannan kuma ruwan gidan nan ya haramce ki sai dai idan zaki rika shan nacikin bathroom."
baki ta murgud'a masa ta ce
"Sai me."
ganin yana kokarin kuma maso ta taruga da gudu tayi cikin bayi ta murd'a key..

Bata fitoba sai da ta tabbatar da yatafi, tana fita kiran wata 'yar ajinsu mai suna Firdausi na shigowa wayarta.
bayan sun gaisa Firdausi take cewa

"SEEDRAH kina da labarin gobe za a shiga yajin aiki kuwa?."
ido ta waro ta ce "Dan Allah fa wlh bani da labari."
Firdausi ta ce "Wlh nima d'azu K.B yake fad'a min zuwa yanzu kuwa ai labarin ya baza ko ina."
"Wayyo ban ji labarin ba Allah dai yasa adawo da wuri."
"Amin ya Allah."
nan sukayi sallama..

Tun daga ranar S.MAN bai kuma sa SEEDRAH wankin mota ko baiwa fulawa ruwa da duk sauran ayyukan daya shafi sakar gida ba.
aikin cikin side d'in kawai takeyi,
sannan kuma ya kwashe duk wasu kayan sha dake cikin fridge d'in parlour'n kasa zuwa kichin bedroom d'inta duk ya kaisu sama.
kamar yadda ya ce sau d'aya zata rika cin abinci kuwa hakan akayi duk san da zatayi abincin rana dana dare zama yake a parlour har sai ta gama tana gamawa kuwa zaice ta kai masa sama sannan yakulle kichin d'in yatafi da key d'in.
ganin haka kuwa idan tayi breakfast sai ta zuba da yawa cikin kula shi zatayi ta ci har dare.
a haka har ta shafi tsawon sati uku a gidan.
duk yadda taso zuwa gida yahanata yakuma ce mata idan ta sake ta fita to sai ya cire kud'in fitar cikin albashin ta,
tun da tazo aiki tofa aikin kawai zatayi babu fita.
idan tayi yunkurin fita kuma maigadi yaki bud'e mata kofa ya ce Oga ya ce kada ya barta ta fita.
duk san da tayi waya da Mama takan cewa Mama itafa ta gaji tana so ta zo gida ta ganta yakuma hanata fita.
Mama ta ce tabari kawai takula da aikin ta duk gidan suna nan lafiya.
haka SEEDRAH tayi ta mita wai sai kace tazamo matar kulle sai yarika nuna mata wani busasshen iko, ko shi a su wa oho,
dan tana aiki a gidan sa sai ya zamo ko waje bazata leka ba dan rainin tsintsi ma wai harda gidan su yahanata zuwa.

A B'angaren Kamal kuwa yagaji da zuba idon ganin komawarta gida,
gashi yana son ganin ta duk san da yace mata zai zo, sai ta ce masa yabari tukun.

Kwance take akan gado like da waya a kunnen ta suna waya da Kamal,
cikin hirar tasu yake ce mata
"Nifa yau hakurina yakare ganin kyakkyawar fuskarnan taki kawai nake da bukata."
murmushi tayi tare da fad'in
"Um bagashi kana jin muryata kullum ba."
"Inaa jin murya kad'ai bai wadatar ba ganin ki nake son yi, na dauren na daure dauriyar takasa kai ni ko ina, yau zan zo kawai naganki."
"To ai baka san gidan ba."
tafad'a cike da d'an zullumi da tunanin zuwan nasa, bakomai yasa taki barinsa yazo gidan ba sai dun gujewa wulakancin S.MAN dan tana da tabbacin zai iya wulakanta sa idan yazo dan abune mai sauki a gurin sa.

ya ce
"To tun da abun kauna ta tana ciki me zaisa sai na sani nemo sa kawai zanyi, in ban da abunki gidan jarumin namu ne zai gagare ni sani,
yanzu idan na bukaci hakan za'a kai ni har kofar gidan."
murmushin yake tayi
"Ni dai ka huta kawai bance ka wahalar min da kanka ba, kuma gobe ma zanje gidan Nabeela ta haihu daga gun zan wuce gidan Naseeba can zan wuni."
ya ce "Da gaske."
ta ce "Eh mana." "To shike nan Allah ya kaimu."
nan sukayi sallama.
numfashi ta sauke tana aje wayar a gefen ta, fatan ta kada Allah yasa yazo gidan dan bazata iya jurar ganin tozarcin S.MAN agare shi ba.
mikewa tayi ta nufi kofa dan lokacin d'aura abincin rana yayi.
tana fito wa cak taja ta tsaya nan bakin kofar,
da d'inbin mamaki take dad'a ware idanunta kan S.MAN dake zaune kan kujera wata budurwa na zaune a kan cinyarsa tawani sakalo wuyansa da hannayen ta, takawo fuskarta daf da nashi tana yi masa magana.
shiko hannunsa d'aya ya saka ya tallafo bayan ta ya yin da d'aya hannunnasa kuma ke rike da waya yana daddannawa.
baki bud'e SEEDRAH ta ke kallon su sai kuma tayi saurin janye idanunta tare da yin gyaran murya.

Da sauri budurwar mai suna Teema ta waigo tana bin SEEDRAH da kallon mamakin yadda akayi ta ganta a nan bayan tasan shi kad'ai ne cikin gidan.
SEEDRAH ko tafiya ta soma tazo ta wuce su ta shiga kichin, a ranta take ayyana girman lamarin nasa ashe dai ba iya shaye-shaye ya tsaya ba har da neman mata.

A parlour kuwa kallon tuhuma Teema take yiwa S.MAN mikewa tayi a jikin sa ta zauna gefen sa tare da ruko hanun sa sannan ta ce
"S.MAN wace ce kuma wannan?."
batare da yad'ago daga kallon wayar da yake ba ya ce
"Yar aiki ce." ido Teema ta waro tare da fad'in "Yar aiki, wannan ce 'yar aikin?
haba S.Man kada ka cigaba da rainamin hankali mana, ashe dama kayi aure ne shiyasa dana bukaci nazo kace min baka kasar, yaushe kayi aure S.MAN?."
gabaki d'aya ganin SEEDRAH yasa hankalin Teema mugun tashi tabi ta rikice.
d'an kallon ta yayi kana ya ce
"Na ce miki 'yar aiki ce."
cikin rashin gamsuwa da maganar sa tayi murmushi wan da yafi ihu ciwo, ganin rainin hankalin da yake mata yadubi wannan zankad'ed'iyar yarinyar ya ce wai ita ce 'yar aiki. sai kuma ta girgiza kai tare da fad'in
"Basai ka b'oye min ba ni ban damu da kayi aure ba zan cigaba da jiranka idan ka gama more amarci idan kana bukatar karin wani amarcin zaka iya nima ta, ko yanzu ne ashirye nake."

A cikin kichin kuwa SEEDRAH na d'aura girki tafito, bata kuma kallon in da suke ba tazo zata wuce su tajiyo muryarsa ya na fad'in
"Ke ba kiga bakuwa bace ki kawo mata abun sha."
cak ta ja ta tsaya tare da juyowa da zummar ce masa baya daga cikin jadawalin aikin ta kawowa  karuwa abin sha.
sai kuma ta juya ta hanyar tausar zuciyar ta tahaura sama domin kawo mata, dan duk yakwashe duk wani abin sha ya kaisu sama.
Teema ko baki bud'e take binta da kallo harta haura sama tana ta son ta gaskata wai shin da gaske ne 'yar aiki ce.
sai da takawo drink's d'in yasata ta bud'e ta zuba mata a kofi kafin ta gaskata cewa 'yar aikin ce dai da gaske,
sai dai tana ta shan mamaki ace kamar wannan takasance a 'yar aiki, dan tayi imani har idan da matar sa ce ko auren kiyayya akayi musu dole sai taga kishi a kan idonta a yanda tafito ta samesu d'in nan, bare kuma har taje ta kawo mata abin sha.
ko da SEEDARH ta juya tanufi d'aki bayan ta Teema tabi da kallo har ta shige ciki.
gabaki d'aya tasha jinin jikin ta wai ace wannan ita ce 'yar aiki, ba sai wani yafad'a mata ba tasan SEEDRAH tafita komai da kamai kyau diri da komai ma na tsarin zubin halitta.
wannan itace S.MAN ya aje amatsayin 'yar aiki matarsa kuma to ya zata kasance kenan?.
tayiwa kanta tambayar acikin zuciyar ta, sai yanzu ta samo amsar da yasa yaki aurenta sannan kuma yaki amsar tayin bukatarta na mallaka masa kanta koda bai aure ta ba.

Wace ce Teem?.
Teema d'iya ce ga wani hamshakin d'an siyaya a Nigeria ta jima tana d'awainiya da dakon son S.MAN a zuciyar ta,
saboda tsabar son da take masa duk kasar da zaije buga kwallo sai ta bi jirgi taje ta same sa.
duk yan da taso ta juyo hankalinsa gareta ta garara dan har kanta ta ce zata bashi tasha tub'e kayan ta a gaban sa amma ko kallo bata ishe saba, wasu lokutan yakan tab'a jikin ta sai dai baya wuce gona da iri.
duk da S.Man yarayu cikin turawa baisashi mu'amalar banza da mata ba, ya kanyi iya bakin kokarin sa wajen kame kansa, ba Teema kad'ai ba akwai mata da yawa masu kawo masa kansu baya sauraran su.
wannan kenan...

Ko da SEEDRAH ta kuma fitowa duba girkinta basa cikin parlour'n yanzu, dan haka ta wuce taje tacigaba da aikin ta.

Da yammacin ranar tana zaune cikin d'aki bayan tayi wanka ta shirya cikin riga da siket na atamfa, tana zaune a bakin gado tana d'an daddanna wayar ta, gabaki d'aya kad'aici ya ishe ta kewar Mama da 'yan uwan ta duk sun addabe ta.
a hankali ta d'ago kanta jin an turo kofar

Ganin shine sai ta maida idanunta kan wayar tacigaba da abun da take.
yana tsaye rike da kofar daga nan bakin kofar ya ce
"Wa kika gayyato mun shi gida na?, kefa kawai 'yar aiki ce, baki da ikon da zaki shigomin da wani cikin gidan nan, na ce masa yatafi na aike ki."
da sauri ta d'ago tana duban sa akasan ranta ta ce
"Kamal kazo kenan."
"Kada ki kara gaiyato min wasu 'yan iska cikin gida daga yau."
ya juya yana kokarin fita
da sauri ta ce "Shine zakace masa ka aike ni alhalin ina nan, shi ba d'an iska bane kamilin mutum ne, ko waccan karuwar da tazo ba'a ce mata baka nan ba bare kamilallen mutum."
kofar ya janyo batare da yayi magana ba sakamakon kira data shigo wayar sa.
da sauri ta mike zatayi waje kiran Kamal ya shigo wayar ta, cikin hanzari ta gad'aga
Kamal ya ce
"Yanzun nan nabar kofar gidan Yayan mu nayi rashin sa'ar samunki nayi kuma farin cikin had'uwa da kwarzon mu har sai da muka d'au selfi da shi, dama nazo ne na sanar miki gobe idan Allah ya kaimu zamu d'an yi tafi da Alhajina."
numfashi ta sauke jin dai S.MAN bai gwada masa bakar halin sa ba.
tayi masa fatan isa lafiya nan suka lula duniyar masoya tana like da waya a kunne suna ta zuba love d'in su...

Bayan kwana biyu.

SEEDARH ce kwance cikin d'aki tana kallo a t.v hamma ta yi tare da yin salati, a hankali ta mike ta janyo kular da ta saka abincin breakfast ciki wan da take ajewa tarika ci har dare ta zauna bakin gado ta soma ci.
taci yadda cikin ta zai iya d'auka kana tarufe sauran.
fuska ta yamutsa dan yanzu ruwa kawai take da bukata, dama ruwan pampon kichin take tara cikin kofi ta kawo d'aki tarika sha duk da sam baya kashe mata kishi haka take maneji da shi, gashi kuma gaba d'aya ta mance bata tari ruwan ba lokacin da ta gama girki, gashi ya kulle kichin d'in yatafi da key d'in.
tsaki taja tare da fad'in
"Dole ma in nemo ruwa dan wlh bazan mutu da kishi ba."
tamike da d'an sauri tafita, cikin sauri ta nufi steps dan taji fitarsa d'azu a mota bata kuma ji dawowar sa ba.
tana shiga parlour'n sama in da fridge yake ta nufa ta bud'e, babu ko gorar ruwa aciki drinks ne kad'ai a ciki.
rufe fridge d'in tayi tana fad'in
"Ruwa nake jin kishin sa ba lemo ba."
da sauri ta juya tanufi kofar bedroom d'in sa ta tura kofar a hankali............!

Mommyn Twins ce

🌺 *ƘARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

_

*___________________________________________*

*🌈 🇰 AINUWA 🇼 RITER'S✍🏻*
* 🇦 SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻
```

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*___________________________________*

page 15

Tashiga ciki da sauri ta isa inda fridge yake ta bud'e, cikin hanzari ta d'au babban gorar ruwa har hannunta na b'ari tabud'e shi dan bakarami kishi take ji ba.
sai da ta sha kusan rabin gorar kana ta sauke gorar ta mai da marfinsa tarufe, takuma d'aukar wani babban gorar ruwa sannan ta rufe fridge d'in
tana fad'in
"Zan shaku har dare."
ta juyo tare da d'aga kafarta zata bar d'akin aka turo kofar.
da sauri cikin rawar jiki tayi baya da hanunta tab'oye gorunan ruwan a bayan ta.

Ido S.MAN ya zuba mata ganin ta tsaye cikin d'akin sa cikin yanayin nuna rashin gaskiya, sai kuma yasoma d'aga kafarsa ya tako zuwa gabanta yayin da yake cigaba da binta da kallon tuhuma.
"Me ya kawo ki cikin d'aki na lokacin zuwan aikin ki baiyi ba, sata kika zo min ko?."
ya jefa mata tambayar ya na mai cigaba da tsare ta da ido.
d'an dibirbircewa tayi sai kuma ta saita nutsuwar ta ta ce
"Ni bana sata ban tab'a yi ba bazan kuma faraba da yardar Allah."
tayi maganar had'e da murgud'a baki da d'aga hanci sama cike da tsiwa.
ya ce "To idan ba sata kika zo min ba me kike b'oye shi a bayan ki."
yafad'a tare da miko hannunsa ya cafko hannayen ta da suke b'oye a bayan ta,
ba shiri tasaki gorunan kasa, sabo da yan da ya ruko hannun nata da salon mugunta.
bin gorunan ruwan ya yi da ido kana ya mai da duban sa gare ta ya ce
"Okay satan ruwa kika zo min a d'aki?."
baki ta turo ta ce "Kai nifa ba b'arauniya bace kishin ruwa nake ji dan kuma na d'auki ruwa na sha baizama nayi sata ba,
idan kuma hakan sata ne to kowa ma b'arawo ne tun da kowa yakan iya shan ruwa a duk in da ya gansa, ruwa kuma ai na Allah ne bana d'an mutum ba."
"Idan kuma mutum ya siya da kud'in sa ne ya ajiye wani yad'auka fa shima ba sata bane, to bazaki sha wannan ba akan ba ruwa cikin bathroom d'in d'akin da kike ne, ko da a gidan ku

ruwan gora kike sha, wani samin guri kawai wuce ki bar min nan na daina ganin ki."
yayi maganar tare nuna mata kofa yana yi mata alamar ta fita.
baki ta turo gaba ta ce
"Allah bazan sha ruwan bayi ba ni ko a gidan mu ma bana shan ruwan pampo dan baya kashe min kishi, sauyin rayuwa ce kawai amma muma ruwan gorar muke sha a gidan mu da, yanzu kuma da Allah yaso ganin mu a haka bai hana mu kud'in da zamu siyi ruwan fiyowata ba, ni ban iya shan ruwan pampo ba dan baya kashe min kishi."

Ya ce "Zaki b'ace min da gani ne ko sai na murd'e wannan bakin rashin kunyar, tun da bazaki sha na pampo ba sai ki zauna haka."
fita tayi tana kunkune da fad'in wlh bazata sha na pampon bayi ba kam...

Haka kuma bata sha bathroom ba har sai da tazo girkin dare kafin tasha a kichin ta kuma d'iba ta kai bedroom d'in kwanan ta.
shan ruwan kawai take bawai ko dun yana kashe mata kishi ba,
SEEDRAH ma abociyar shan ruwan dare ce.
duk nauyin baccin ta kishin ruwa na tadata cikin dare.
hakan ne ta kasance da misalin karfe biyun dare kishin ruwa ya tashe ta, ta mike cikin magagin bacci ta isa in ta aje ruwan da tad'ibo a kichin aikuwa garin gigin baccin ta tamika hannu zata d'au kofin ta tureshi ruwan ya kife a kasa.
sai a lokacin ta gama bud'e idanunta da bacci ke cike fal cikinsu.
 tsaki taja cikim muryar bacci ta ce
"Shine ka zube."
sai kuma ta nufi bathroom dan ji take bazata iya bacci idan bata sha ruwa ba.
pampo ta kunna ta kafa kanta tasoma sha babu kakkautawa cikin ta yacika tam sai dai bata fasa jin kishin ba.
 mikewa tayi tana yamutsa fuska dajin yanda lokaci guda taji zuciyar ta na tashi,tasan za ayi hakan dan tana kyankyanin shan ruwan bayi babu in da ta iya ne kawai.
da sauri ra sunkuya kan toilet tashiga sheka amai daya taho mata, sai da ta amaye ruwan data sha duka kana ta mike ta wanke bakinta tana mai da numfashi.
sai da ta gyara in da ta b'ata kafin ta fito.
abakin gado ta zauna tana cigaba da maida numfashi.
wani irin mugun kishin ruwa takeji yin aman da tayi tamkar dad'a kara mata kishi ya yi, zuciyar ta kuwa sai hurewa yake da azabar kishin ruwa.
da kyar ta iya tattaro yawun bakin ta ta had'iye. ta mike da sauri ta d'au hijabin sallarta ta saka tafita a d'akin dan yanda take ji har idan bata sharuwa yanzu ba tana ji kamar bazata wayi garin gobe ba.
direct sama ta haura rike da wayarta tana haska hanya dan duk wutan cikin side d'in a kashe yake.
ko da ta shigo parlour'n sama gurin fridge
ta nufa tabud'e da tunanin ko ya saka ruwa aciki, amma sai taga babu sai drinks d'in ne kawai aciki.

da sauri tashiga waige-waige ko Allah zai sa taga ruwa amma babu ko alamarsa.
numfashi ta fizga da kyar takuma had'iye miyau tare da rumtse idanunta da karfi tana jin yanda zuciyar ta ke dad'a hurewa da ƙishin ruwa.
bud'e idanunta tayi ta sauke su kan kofar bedroom d'in sa idan har tana son tasha ruwa tofa babu makawa dole sai tashiga d'akin sa.
sannan ta rokesa ya sammata.
bata da zab'in da yawuce hakan a hankali tashiga d'aga kafarta har ta tako bakin kofar.

Ta d'aura hannunta jikin handle sai kuma ta tsaya da tunanin har idan taje tarokesa tofa jin kansa zaiyi kamar yafi kowa, sannan kuma yakara kaimi kan wulakantata da yake,
to amma tana jin kishin da bazata iya sarrafa kanta ba dole sai ta sami ruwan da zatasha.
kashe tocin wayar ta tayi kana a hankali ta murd'a handle d'in ta tura kofar a hankali cikin sand'a tasa kai cikin d'akin.
cikin d'akin duhu babu haske ko tafin hannunta bata iya gani.
a hankali tasoma d'aga kafarta duk da bata ganin gaban ta amma takan iya hasko in da fridge yake acikin zuciyarta, tana jin zata iya isa gurin batare da haske ba.
wani irin garuwa tayi da jikin abu da sauri ta dafe goshinta datake sammanin fashewa ma ya yi dan bakaramin azabar zafi taji ba, gaba d'aya jikin ta ya d'au b'ari ga zafi ga tsoro bata kai ga dai-dai ta nutsuwar ta ba taji hannun mutum a kafad'ar ta.
wani uban kara ta sake mai cike da tsananin tsoro tayi baya da sauri takuma garuwa da wani abun, tana kokarin d'ago wayarta ta kunna tsabar b'arin da jikin ta yake wayar ta fad'i kasa, sai kawai takuma sakin wani karar.
"Ke rufamin baki me yakawo ki d'aki na a tsohon daren na me kika ajiye anan kika zo d'auka sata kikazo min?."
taji maganar sa daf da ita, wutar d'akin ya kunna yaci gaba da fad'in

"Alhj Musa ne ya turo ki ki kasheni ko."
kai tashiga girgizawa sai kuma ta ce
"Nifa ruwa zansha ba wani abu yakawo ni ba, ni kuma ba b'arauniya bace ka dai na dangantani da sata, sannan kuma mezaisa Baba yaso kasheka."
"Ke ba magana nace ki jera min ba, bance kije ki sha ruwan bathroom ba d'azu, yanzu ma ki koma kije kisha."
"Allah ni bazan iya shan abin da zai kusa kashe ni ba."
tayi maganar tana janye idanunta daga kansa dan babu komai ajikin sa sai gajeren wando kawai.
ya ce "Oya wuce ki fita in kinje ki mutu."
a hankali ta juya harta kai bakin kofa tajiyo muryarsa yana fad'in
"Zo ki d'auka zan cire kud'in sa acikin kud'in aikin ki dan kin dai na cin abinci kyauta acikin gidan nan, duk wani abun da zakici acikin kud'in aikin ki."
da sauri ta juyo dan sosai take jin kishin ta d'au babban gorar ruwa tafita, a parluor'nsa tasha kusan rabin ruwan kana ta koma d'akin ta sai alokacin ta sami bacci mai dad'i yadda take so..

Washegari kamar kullum tana yin sallar asuba bata yadda ta koma ta kwanta ba sanin kalar

baccin ta ba lallai bane tatashi dawuri.
kichin tatafi tafara d'aura breakfast kafin ta fito can ta hangosa gurin motsa jiki tawuce ta haura sama.
ko da ta gama gyaran saman tasauko shikuma lokacin yahaura sama,
tashiga kichin ta kammala aikin kana ta d'auki nasa breakfast d'in ta kai masa nasa, tadawo kichin d'in ta d'auki nata tashige d'aki tana zama tajiyo sa yana kokarin kulle kichin da sauri ta mike tuno da wayarta ta mance shi  a cikin kichin d'in.
tana fitowa yana zare key da sauri ta karaso in da yake tana fad'in
"Na mance wayata aciki bani key d'in na d'auka."
jefa key'n ya yi cikin aljuhunsa kana ya juya yasoma tafiya yana fad'in
"Sai ki jira idan lokacin bud'e kichin d'in ya yi sai ki d'auka."
da sauri tasha gaban sa tarike kugu ta ce
"A wani dalili wayata ce ina bata wani ba kabani key nad'auki abina."
"Anki badawa idan kina da karfi ki kwata."
hararar sa tayi sama da kasa kana taja tsaki mtttss ta juya.
 hannu ya miko zai cafko ta ai ko ta d'aga kafa tasa gudu nan jigidan jikin ta yafara bada sautin kacau-kacau.
tsayuwa ya yi tare da zubawa bayanta ido yalura duk san da tayi masa tsamin baki zata gudu sai yaji wannan karar ajikin ta.
har ta shige d'aki yana tsaye kana daga bisani yahaura sama..

Yana gama breakfast yazari makullin mota yabar gidan, bai dawo ba sai bayan sallar isha.
SEEDRAH kam yau tasha baccin ta ma'ishi wan da tun da tazo gidan bata samu tayi irinsa ba, kasan cewar key d'in kichin na gurin sa be dai isa yakamata da laifin rashin yin girki ba.
tana zau ne kan sallaya yaturo kofa, tad'ago ta dube sa sai kuma ta kawar da kanta tacigaba da lazumin da take.
 daga bakin kofar ya ce
"Ke ina abinci na?."
batare da ta d'ago ba ta ce
"Kaba da key ne?." key'n ya wurgoshi jikinta ya ce
"Tashi ki dafo min tea yanzunnan ki kawo min."
ya janyo kofar ya fita.
sai da ta gama dukkanin addu'o'in ta kafin ta fita taje ta dafo tea d'in.
ad'an karamin flas tazubo tad'aura shi kan d'an madaidaicin tray had'e da cup tafito ta haura sama..
yana zaune a parlour yana busa hayakinsa,
fuska tashiga yamusawa tana kakkawar da fuskarta gefe,
tazo ta gefen sa ta aje tray'n kan table d'in da ke gefen sa dai-dai lokacin da ya huro hayakin sigarin.
da sauri takai hannu ta toshe hancinta, d'aya hannunta kuma tana kore hayakin da shi tana wani yamusa fuska cikin yanayin da kamar zatayi amai.
tajuya zata bar parlour'n tana mai cigaba da yamutsa fuska cikin kasa da murya sosai ta ce

"Mutum bashida aikin yi sai shaye-shaye da halin y'an kwaya mttss."
taja gajeren tsaki

Maganar da tayi tamkar a kunnensa.
wani irin mikewa ya yi tare da fizgota har sai da ta garo da jikin sa.
bakaramin tsorata tayi da ganin yanayin da ya shiga lokaci guda ba,
ta lura aduk sannda ta ce masa d'an kwaya d'an shaye-shaye irin wannan yanayin fusatar take gani tattare da shi.
sigarin ya kai bakinsa yazuko hayakin daya cika bakin sa kana ya jefar da sigarin kasa sannan ya kuma yanyota jikinsa sosai kana ya tallofo kanta da hannunsa d'aya d'aya hannun kuma ya matse bakinta,
ya d'aura lips d'in sa kan nata yahura mata hayakin sigarin cikin bakinta duka sannan yad'ago kansa yasa hannu ya toshe bakinta.
yadad'a tallafo kanta sosai da sosai.
SEEDRAH ko ido tashiga zazzarewa tana juya kai da fizgar numfashi, yayin da hayakin yashiga kokawa da makoshin ta, tuni idanunta suka kad'a sukayi jajir.
sai da ya tabbatar da tahad'iye hayakin kafin ya sake ta tare da angizata tazube kan kujera.
yabita yashako wuyanta cikin fusatacciyar murya ya ce
"Ni ba d'an shaye-shaye bane ban tab'a shan kwaya ko kayan maye ba, iya sigari nake sha shima nafi shansa alokutan da nake jin b'acin rai, duk san da kika kuma dangantani da d'an kwaya na rantse saina canza miki kamanni wawuya kawai!!."
ya hankad'a ta tagaru da jikin kujera ya mike yana huci yashige bedroom d'in sa.

Itako tari take babu ko kakkautawa tanayi tamkar zata shid'e da kyar ta mike tana cigaba da tarin ta sauka kasa tana shiga d'aki bayi ta wuce tarika kela amai kamar zata amayar da hanjin cikin ta.
da kyar aman ya tsaya ta mike tana mai da numafshi a daddafe ta gyara in da ta b'ata kana tayi wanka ta fito,
tana saka kaya ta haye gado ta kwanta tana
jamasa Allah ya isa a haka bacci ya d'auke ta.

Washegari da kyar ta iya tashi sallar asuba sakamakon wani baccin da ke cike fal idanunta, tamkar batayi bacci da daddare ba.
bayan tayi sallan kwanciya tayi kan sallaya jin yadda bacci ke fizgar idanunta ai kuwa ba b'ata lokaci bacci yatafi da ida.
ba ita tafarka ba sai wajen karfe 10 da rabi.
da sauri ta mike ganin yanda lokaci yatafi har haka, sanin kalar baccin ta shiyasa tun da tazo gidan bata yarda ta kwanta baccin asuba gudun kada ta ketare lokacin aikin daya zana mata saboda kare wulakancin sa ga Baba.
da sauri ta fito numfashi ta sauke ganin sa can gurin motsa jiki.
a ranta ta ce
"Allah ya taimaka shi ma dai makaran ya yi."

waige-waige tashiga yi tama rasa ta ina zata fara sai kawai ta juya da sauri ta haura sama.
cikin hanzari ta shiga gyara parlour'n nan da nan ta gama kasancewar babu wani datti,
da sauri ta shige cikin bedroom d'in sa ta na fad'in
"Allah yasa har na gama kada azzalumin nan ya shigo."
d'an tsayuwa tayi cikin d'akin tana tunanin tafara daga cikin bathroom ne ko daga bedroom, sai kawai ta yanke hukuncin ta fara daga bayi sannan ta fito tagyara d'akin, da sauri ta nufi kofar bathroom ta murd'a handle ta shige ciki ta maida kofar ta rufe kana cikin hanzari ta juyo.

Wani irin waro ido tayi ganin mutum tsaye cikin bayin babu kaya jikin sa yayin da yake ta kokarin wanke kumfar sabulu a fuskansa,
kara ta calla sai kuma da sauri ta kai hannayenta tarufe fuskarta da shi tashiga ja da baya.
da sauri S.MAN ya wanke kumfar fuskarsa kana ya janyo towel ya d'aura a kugun sa,
jin ta garu da jikin kofa ta juya da sauri tana kokarin bud'e kofar sai ji tayi ya danne kofar da hannunsa kana yakuma murza key ya kulle kofar da key.
ido takuma warowa batare da tajuyo ba ta ce
"Allah bansan kana cikiba kuma ai can na hangoka gurin motsa jiki to taya akayi na ganka a nan kuma."
fuska ya d'aure tamau ya ce
"Karya kike kin sani sarai ina ciki shiyasa ma kika shigo, wannan fisararrun idanun naki ga dukkan alamu kinsan maza shiyasa ma kika biyoni bayi yanzu!."
ya yi maganar cikin tsawa har sai da tad'an zabura.
kai tashiga girgiza wa tana fad'in
"Kada kayi min kazafi wlh Allah ban san kana ciki ba a gurin motsa jikinka fa na ganka dan Allah bud'e min kofa na tafi."
"Ai ba ki isa ba tun da kika ganni to yazama dole kema na ganki baki isa kici bulus ba."
ido ta waro ta ce "Me kake nufi?."
ya ce "Tub'e maza yanzun nan!."
baya taja tare da nuna sa da yatsa ta ce
"Kada kace zakayi min rashin d'a'a anan nace maka bansan kana ciki kana wanka ba."
"Okay bazaki tub'e ba to bari ni na tub'e ki."
ya janyota tare da matse ta ajikin sa yana kiciniyar zuge zip d'in rigarta.
tureshi tashiga yi tana kokarin kwatar kanta ganin dagasken sa tub'e mata kaya zaiyi ta ce
"Wlh Allah ka kuskura kacire min kaya sai kayi dana sani kasake ni ka kyaleni."
tuni yayi kasa da zip d'in kana yaruko wuyan rigar yazare shi a jikinta yawurgar kasa, bra'n jikin ta ya bayyana.
da sauri ta sulale kasa tare da had'e kanta da guiwa tana kare jikinta, tana fad'in
"Zakayi dana sanin yimin haka wlh sai kayi nadamar aikata min haka."
wani murmushi ya sake sannan ya sunkuyo gabanta ya ce
"To yaushe ma naraman tukun ai tsaye zaki mike kamar yanda kika shigo kika ganni, oya mike!."
ya karashe maganar da tsawa.
ido ta rumtse da karfi ta ce
"Wlh Allah bazan mike ba sai dai in zaka kasheni."

bata kai ga karasa maganar ba ta had'iye ragowar sakamakon jin yad'aga ta cak yamikar da ita tsaye.
da iya karfin ta tafizge jikin ta tamasa gefe tana kare kirjinta da hannayen ta.
ganin yana matso ta sai tashiga waige-waige da sauri ta masa jikin mirron dake like jikin garun bayin cikin rawar murya ta ce
"Wlh idan ka matso ni sai na cire na buga maka."
hannu ya miko ya fizgota tadawo jikinsa jin yana kokarin jan zanin ta sai kawai ta sulale kasa yabita kana yacibada da kiciniyar kunce zanin yazare sa ajikin ta.
babu shiri tasauke hannayenta datake kare ababen kirjinta ta dafasu a kasa tashiga ja da baya da baya har ta isa jikin garu, zuwa lokacin kam tafara tsorata kwarai da gaske da lamarin sa.
tsoro ne sosai ke bayyane a kan kuskarta sai dai har lokacin bakin ta bai mutu ba tana ta yi masa gargad'i da kashedin tub'e mata kaya.
shiko yana sunkuye idanunsa a kanta, ya yin da zuciyarsa ke wani irin tsalle kamar zai faso kirjin sa ya fito,
ganin cikakkun halittar jikin ta. sai kuma ya girgiza kansa ya ce
"Ina hakan bai wadatar ba ni kwata-kwata babu komai ma ajikina kika ganni."
kafafunta yaruko yajanyo ta tado gaban sa sai kawai yazagaye ta da hannayen sa yasaka hannunsa kan mab'allin bra'n ta yab'alle shi tare da zare shi ajikin ta yayi wurgi da shi.
fararen nonuwan ta wanda suke cike tip-tip da su a tsaye kem kwanin ban sha'awa suka bayyana.
wani uban kara ta sake tana niman mafaka takare jikinta sai dai babu wani kayan ta dake kusa da ita duk ya jefar dasu can gefe, ganin yana kokarin janye jikinsa ta in da zaisamu ya kare mata kallo sai kawai tafad'a jikin nasa ta kankamesa cikin muryar da kuka ke son kwace mata ta ce
"Wlh bazan yafe maka ba sai munyi shari'a da kai sai kayi dana sanin duk abinda kake min, kuma Allah sai ya saka min, mugu kawai ai idan kafi karfina bakafi karfin Allah ba sannan bakafi karfin hukuma ba sai sunbimin kadi na."
wani irin shock yaji yan da ta shige cikin jikin sa ababen kirjin ta suka manne da nasa kirjin har sai da ilahirin jikin sa ya motsa, babu shiri ya rumtse idanunsa da karfi tare da jan numfashi har sai da sautin sa ya bayyana.
wani irin zabura tayi jin hannunsa kan pant d'in ta yazamo shi ta kasan jigidan jikin ta yana kokarin janye shi kasa,
da sauri taciro kanta dake cikin wuyansa  tana kallon fuskarsa da idanunta da hawaye suka cikashi tap sai kwalkiya suke kad'an ya rage su zubo.
sai kuma tashiga girgiza masa kai tare da fad'in
"A'a kada kayi haka a'a kada kamin haka dan Allah kayi hakuri, narantse bansan kana cikin bayin nan ba."
wani murmushin mugunta ya sake jin kalmar hakuri daga bakinta karo na farko a had'uwar su data fara bashi hakuri.
 duk wani wuyan da zai bata abaya bata tab'a bashi hakuri ba.
rirrike pant d'in tayi da karfi jin yana ta dai kokarin rabata da shi.
sai kuma ya saki pant d'in, numfashi ta sauke batayi aune ba taji ya zura hannusa cikin pant d'in ta.

yatsunsa biyu na sakiya yashiga kokarin turasu cikin HQ d'in ta.
wani irin gigitaccen kara ta fasa tare da rirrike damtsen hannunsa tuni jikin ta yad'au b'ari sakamakon wani zafin daya ratsata, hawaye yashiga wanke fuskarta.
shiko kokari kawai yake ya tura yatsun nasa ciki sai dai ko kan yatsun basu sami hanyar shigewa ba.
wani irin zabura tayi ta mike tsaye da iya karfin ta sakamakon kuma tura yatsun da ya yi wan da har yanzu ko  kan yatsun bai samu sun wuce ba.
ta d'au zanin ta a guje tayi bakin kofa tamurza key ta bud'e kofar dagudu tafita sai a cikin d'akin tasami damar d'aura zanin a kirji tayi waje da gudu ta nufi steps.
tana step d'in farko na sauka taga wani na kokarin shigowa parlour'n sama,
gani yanda ta sako kai aguje yasa shi bata hanya da sauri tawuce tana sauka tashige d'aki ta kulle kanta tana maida numfashi sai kuma ta fashe da kuka tazube kan gado...

Da sauri Sagir yashige bedroom d'in S.MAN yana waigen ta, dai-dai lokacin da S.Man yafito daga bayi,
 yana tsane gashin kansa da karamar towel, sai yarfe hannunsa da ya yi kokarin cusa shi cikin HQ d'in ta yake,
 har lokacin sai yarika ji kamar hannun yana cikin HQ d'in nata.
wurgi da towel d'in hannunsa ya yi kana ya had'e hannayen sa duka ya mussuke su yakuma yarfe hannun, tare da kuma tankwashe yatsun suka bada sauti.
ido Sagir ya zuba masa kana ya ce
"S.MAN me kayiwa yarinyar can ne?."
yatsun sa ya tankwashe dayake jin su kamar ana jansu da kurar karfe ya ce
"Nakure mata rashin kunyarta ne."
dariya Sagir ya yi ya ce
"Kai fa d'an iska ne kaga yanda ta firgice kuwa kadafa ka aje yarinyar mutane karika turmushe ta, shiya sa nace maka kabawa Teema dama kawai ka kwashi gara."
"Kai ni fa ba abin da nayi mata, ta ganka a gun motsa jiki tayi zaton nine shine tafad'o min kai a bathroom, rashin kunyarta ya yi yawa bakin ta baya mutuwa shiyasa nakure mata rashin kunyar nata,  kai ni na fad'a maka ina bukatar wani abune da zaka kawo min batun Teema."
kallon hannunsa da yake ta yarfewa Sagir ya yi sai kuma ya yi dariya ya ce
"Me ya sami hannun naka  ko kayi targad'e ne?."
hararar sa ya yi shiko yafice a d'akin yana dariya.
d'aya daga cikin d'akunan cikin parlour'n ya shiga wanda nan ne masaukin sa.

Zama S.MAN ya yi bakin gado har lokacin yana jin hannunsa tamkar yana yawo cikin HQ d'in ta, sai yarika ji kamar ana jan yatsun nasa tamkar kurar karfe.
yarfe hannun yakuma akarona sau ba a dadi ya mike yasoma shiryawa yana yi yana yarfe hannun lokaci zuwa lokaci yakuma ja tsaki...

SEEDRAH kuwa sai da taci kukan ta ma'ishi taja masa Allah ya isa yafi cikin kwando. kana tamike tana ware kafa dan bakaramin zafi kasan ta ke mata ba, tashiga bayi tayi wanka tare da

yin sarki da ruwan zafi tafito tazauna bakin gado.
ji tayi an turo kofa da sauri tad'ago tana duban sa sai kuma tayi saurin janyo hijabin ta tazura a jikin ta dan zanine d'aurin kirji kad'ai a jikin ta.
ya tako cikin d'akin yana isowa in da take ya...........!

Mommin Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

*________________________________________*


*🌈🇰AINUWA 🇼RITER'S✍🏼*
*🅰SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻
```

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*_____________________________________*

page 16

Ya wurga mata bra da rigar ta da ta gudu ta barsu cikin Bathroom d'in sa.
kai ta sunkuyar kasa cike da jin kunya da bakincikin abin da yayi mata.
baki ya tab'e idanunsa a kanta kana ya ce
"Ke ina breakfast d'in?."
cike da haushi mai had'e da tsanar sa ta ce
"Ban girka ba."
a hatsale ya ce "What! wazai je ya girka miki oya tashi kiwuce kije ki girka yanzunnan."
kasa takuma yi da kanta dan har yanzu tsoron sa bai sake ta ba, shiko yaji dad'in ganin tsoron sa daya d'arsa mata a zuciya ya juya ya fita yana fad'in
"2 minutes na baki kifito."

Sai da ta saka kaya kafin ta fito
suna zaune a parlour shi da Sagir,
yana danne-danne a wayar sa, yayin da gaba d'aya Sagir ya maida hankalin sa kan TV yana kallon kwallo ihu Sagir ya sake dai-dai lokacin da jama'ar dake kallon kwallo nacikin TV'n suka saki hele suma,
harda mikewan sa tsaye yana tsalle ya dubi S.MAN yana fad'in
"Kai mutumi na gaskiya kabuga wasa mai kyau anan gurin kai fa na daban ne Allah yayi maka wata baiwa na musamman shi yasa gidajen TV basa gajiya da hasko wasan ka ko da yaushe."
murmushi kawai yayi batare da ya d'ago ya kalli TV'n ko Sagir d'in ba.
dai-dai lokacin da SEEDRAH ta karaso cikin parlour'n tajiyo Sagir yana maganar kallon TV tayi dai-dai lokacin da ake hasko sa a TV turawa 'yan jaridu suna ta magana a kansa na nuna yabawar su a kansa.
baki ta tab'e tawuce su kan ta a kasa.
Sagir yabita da kallo har ta shige kichin kana ya mai da duban sa kan S.MAN ya ce
"Allah baka da kirki kaduba kaga yadda kasa yarinyar nan tazamo kamar mara lafiya dube ta fa abin tausayi."
"Mance da ita wannan ba abin tausayi bace yarinyar sam batada kunya, sa'ar Yusrah ce fa sai

d'an banzan rashin kunya."
dariya Sagir ya yi ya ce
"To ai dama sai a hankali su yanzu sukejin  kansu daga zaran sun fara tasowan nan musammna idan sukayi girman jiki da wuri."
baki ya tab'e batare da yakuma cewa komai ba.
akai-akai yake d'an tankwashe yatsunsa da har lokacin yake jin su kamar suna cikin  HQ d'inta.
dogon tsaki yaja tare da yarfe hannun had'e da kuma tankwashe su,
 jin tamkar dad'a karamasa lamarin ake yana ji kamar ana jan yatsun sa suna lumewa cikin abin nata, gawani d'umin da tun da ya cusa hannunsa ciki har yanzu yake jin yatsun sa suke ma.
ido Sagir ya zuba masa sannan ya ce
"Wai hannun naka ciwo yake yi ne kam?."
"Wata kila ciwon zaiyi."
yabashi amsar a takaice.
dariya Sagir ya yi ya ce
"Mutumi na wai ina ne kasaka hannun naka ne ko ka bige a bathroom ne?."
hararar sa ya yi batare da ya ce komai ba.
shiko Sagir dariya yakuma tuntsirewa da shi..

A kichin kuwa SEEDRAH na gama breakfast d'in ta tarkaso abincin takai dinning  ta koma tad'au nata tazo zata wuce tajiyo muryarsa
"Wa kika ajiye dazai d'auko yakawo nan."
da sauri Sagir ya ce
"Bari kawai na d'auko."
hannu ya d'aga masa kana ya ce tawuce taje ta kawo musu nan.
kanta a kasa taje ta kwaso ta kawo musu kana ta wuce d'aki..

Tun da SEEDRAH tashige d'aki bata kuma fitowa ba har sai da lokacin abincin rana ya yi, nan ma tana gamawa ta koma d'aki. dan dama ita bata fiye zaman parlour ba dan bata iya jurewa wulakancinsa..
washegari
tana cikin jera abincin rana akan dinning S.MAN yashigo parlour'n tun kafin ya karaso ya ce
"Ke me kika girka waya baki ikon girka wani abu batare da kin tambaye ni abin da nake so naci ba, oya kwashe abincin nan kije ki girka min tuwon sakwara miyar kifi yanzun nan."

Ido tad'an waro wai duk uban wahalar girkin nan da ta yi kuma kara wani zatayi, ta ce
"Gaskiya sai dai kuci wannan dan wlh kirjina ciwo yake min bazan iya dakan sakwara ba ayi wani karon."
"Ni kike cewa bazakiyi ba ko Alhj Musa bai isa ya ce min bazaiyi abin da nake so ba bare kuma ke, zaki wuce kije kiyi ko sai na canza miki kamanni  anan."
yayi maganar yana dumfaro in da take cike da zafin nama.
kugu ta rike duk da kuwa bugawan da kirjinta yake. dan har yanzu tsoron sa na nan tare da ita sai dai a yanzu tayi kokarin danne tsoron ta hanyar tattaro tsiwarta dan ta tabbata idan ya iso ta sai ya kai mata hanu.

ta ce "Kada ka sake ka maso ni dan wlh zakayi dana sani,
Baba kuma kai baka isa ka sashi yayi ba tun da ya haifa, sannan karubuta ka ajiye nayi imani sai ka karb'i sakamakon abin da kayi min,
sai nayi maka mugun b'arnar da harka mutu bazaka mance ba."

Wani irin d'aga kafarsa ya yi cike da karsashi sai gashi a gaban ta,
mari ya kai mata cikin hanzari takai hannayenta tarufe fuskarta marin yasauka kan bayan hannunta, abun ka da farar mace nan da nan shatin yatsunsa suka shinfid'u a kan bayan hannunta.
cike da jin rad'ad'i da azabar zafi ta shiga yarfe hannun.
a fusace ya shako ta da karfi yana fad'in
"Duk san da nake fad'a kina mai da min zaki sha wuya, me zaki iya yi."
da gudu Sagir dake biye da shi ya iso ya rike hannunsa ya daddage ya janye shi jikin wuyanta ya na fad'in
"Haba S.MAN kayi hakuri mana tun da tace zatayi wani karon kayi mata hakuri zuwa wani lokacin mana."
SEEDRAH kuwa jin an kwace ta bakin ta bai mutu ba tajuya tayi d'aki tana fad'in
"Na rantse sai na cinnawa gidan nan wuta sai na kona gidan nan gaba d'ayan sa."
S.MAN yad'aga kafa zai bita Sagir ya sha gabansa ya ce
"Dan Allah ka kyaleta."
"Bakaji abin da take fad'a bane kabarni naje na ɓaɓɓalla yarinyar nan natarata a gun."
"Naji fad'a kawai take amma bazata tab'a iya aikatawa ba, yi hakuri mana."
da kyar Sagir ya lallab'a shi yajashi sukayi dinning yazuba masa abinci yatura masa gaban sa Sagir ya gyara zama yashiga cin abincin yana santi.
ya dubi S.MAN da ko loma d'aya bai kai bakin sa ba ya ce
"Ci mana kaji dad'in abincinnan kuwa Allah abincin nan ya yi dad'i sosai fa,
na tabbata ko tuwon sakwarar nan bazai kaishi dad'i ba, gaskiya yarinyar nan ta iya girki."
sai kuma ya tuntsure da dariya ya ce
"Ga tsiwa ga iya girki jurewa tsiwar nata kawai zakayi dan arika yi maka girki mai dad'i irin haka, idan kuma kasako zafi ciki to wataran za ayi maka da zallar ruwa da gishiri."
yakuma tuntsurewa da dariya yana ci gaba da fad'in
"Kai lallai kuwa ranar zaka ci dad'i."
hararar sa S.MAN ya yi kana ya d'ebo abincin da kamshinsa ke dad'a angizo masa yunwarsa ya kai bakin sa yana fad'in
"Za kuma ta ci dukan tsiya ba."
dariya Sagir yakuma a haka sukaci abincin Sagir nata zolayar sa....

Halimatu da Suhailat ne zaune a d'akin Umma mahaifiyarsu, suna cin tuwon gari da ba a surfe ba wacce Aunty Hajara ce ma takowo musu masarar shine suka nika shi sukayi tuwon sa da miyar kuka, wacce bataji wadatacciyar magi da manja ba.
Suhailat data kai loman tuwo bakin ta tahad'iye sa da gyar tana yamutsa fuska.
kwanon tuwun ta tura gaban Halimatu ta ce

"Nakoshi wlh bazan iya ci ba da kyar fa nake iya had'iyewa."
Suhailat ta ce "Nima haka Umma ki bamu kud'i kawai musiyo wani abun muci dan wlh tuwon nan bazai shiga ba, ni tun da nake ma ban tab'a cin irin wannan tuwon ba haba dan Allah."
Umma ta ce "A ina zan sami kud'in na baku sana'ar me nake dani da ku d'in ba duk zaman kawai muke ba,
ke Suhailat bana ce miki kije ki nimi alfarma a can makarantar yara na bayan layin nan kije kirika koyarwa d'an abin da zasu rika baki ai dai zamu d'an rika kashe wasu masalolin,
ke kuma Halimatu ko ba koyarwa ba ko aiki zan sa a tambaya miki koda a gidan makota ne ko dai ya ya ai za'a rufawa juna asiri."
Suhailat ta ce
"Umma ai naje makarantar fa amma ni abinda sukace zasu rika biya ta ce ya kasa min, wai fa dubu biyar a awata duk tulin wahalar koyar da yara ace dubu biyar a wata Allah gara na cigaba da zama agida."
Halimatu kuwa ido ta ware ta ce
"Umma aiki aikifa agidan makota kuma, to duk fad'in unguwer nan akwai gidan daya kai gidannan girma da zubin tsarin masu kud'i, wlh nima gara narika zuwa koyar da yaran idan na dawo daga school, amma ni bazan iya zuwa aiki wani gida ba haba-haba ina bazai ma yuwu ba, ina bazan iya ba wlh."

Baki bud'e Umma take duban su ta ce
"Aikin banza ke kin raina albashin da za a rika baki ke kuma kin fi karfin zuwa aiki gidan wasu, to duk ku fidda miji kuyi aure, kuna zaune gandan-gandan agida duk kun d'are shekaru ashirin duk mun zauna mun mike kafa da ni da ku,
sai abin da Hajara ta d'an kalato ta kawo musamu muci, idan da kuma kunyi auren da duk ba za a had'u a rufawa juna asiri bane, ayi fama da kannen ku ayi fama da ku,
to duk kufito da miji bari Baban naku ya dawo ko motar hawansa yasiyar ayi muku aure koda katifa ce a kaiku, nagaji da ganin ku a gabana muna jera kafad'a,
duk sa'o'in ku daga mai 'ya'ya uku sai mai, hud'u kuma suna can suna kan karatun agidan mazajensu wasu kuma suna aiki,
duk kusanar wa maneman ku sufito."

Kai Halimatu ta takawar gefe tana mara baki ta ce
"Ni kam dai bani da wani tsayayye sai dai ko in Suhailat dan duk cikin samarukana banga mijin aure ba,
har yanzu ban samo mai gida da mota mai d'aukar albashi mai tsoka ba dan bazanyi auren da miji zai ajeni a gidan gado irin na Aunty Hajara ba, yaushe kasamu kaci me kyan ma bare ka bawa wani naka."
Suhailat ta ce
"Ai ni kowa yasan ma Ya S.MAN nake jira, idan har ban same sa ba to nima sai na jira zuwan mai kud'i tukun, Umma da kike cewa wai da katifa za a kaimu sai kace marasa galihu, wlh ba za'ayi wannan abin kunyar da ni ba sai dai Baba yasan yanda zaiyi ya nimo kud'in min kayan d'aki,
dan wlh bazan shiga bakin kawaye ayi ta yi da ni ba."

Umma ta ce "Sai dai kuwa kishiga bakin kawayen, a gidan uwar uban wa zai samo kud'in kina ganin abincin da za a cima nashirin gagara bare kuma wani kayan d'aki, har yaushe zaku cigaba da zaman jiran me kud'i ku fidda mai rufin asiri kawai,
ke Suhailat kun dai-dai ta da S.MAN d'in ne, in dai kun dai-dai ta ai ko shike nan kin ga zairage yiwa Baban ku wani abin ma."
ta ce "Zamu dai-dai tan ai dan ni shi nake so."
Umma ta jinjina kai tana gyara zama tare da fatan 'yar nata tasami S.MAN d'in dan itama tana son abin da 'ya'yan ta suke so, tana fatan susami mazaje masu kud'i dan acewar ta babu wan da yaki gidan hutu musamman ma shi S.MAN yaro da kud'i wan da taurarun sa yake haskawa.

Mama na zaune a d'aki duk kad'aici ya ishe ta, tunanin 'yarta d'aya tilo ya baibaye ta.
zaune take a kan sallaya tana karatun kur'ani dan shi ke d'ebe mata kewa.
bayan ta kai aya shiru tayi tare da yin tagumi tazubawa Al'kur'anin ido a zahiri a bad'ini kuma tunanin rayuwar da d'iyarta take awani guri take.
idan ba kaddara ba me zai sa tatura yarta gidan wani aiki gidan da babu mata ciki,
sai dai tana da yakini kan tarbiyyar data baiwa d'iyarta dakuma addu'ar da take aikamata akullum da ko yaushe.
a hankali ta rufe kur'anin tare da shafa addur'ar data yi, ta mike taje tad'au kofin kunun tsamiya data dama d'azu, wan da acikin d'an kayan abincin da Maman ta da 'yan'uwan ta suka aiko mata dashi ne daga Zariya dan akwanakin nan su suke ciyar da kansu kowa girkin ta take, dan lamarin kasuwancin Baba sai dad'a tab'arb'ancewa yake, kud'in da Abba yabashi yaja jari yanzu ba uwar kud'i ba riba.

abin da hajara da dangin Umma suka kalato shi suke dafawa suci da 'ya'yanta. ita ma Mama ita d'ayan ta take girka nata wan da nata dangin suke turo mata, wan da duk san da zata saka wani abu a bakin ta sai ta tuna da awani hali 'yarta take ciki shin ita ma taci, duk da tasan in da take ba abinci ba abunda yafi abinci ma yafi karfin sa.
amma irin kauna da tausayin uwa a kan d'anta shike sata tunano ta aduk san da zata kai wani abu cikin bakin ta...

A b'angaren Suhailat wanka da gaye sosai tayi dan yau takuduri aniyar tinkarar abin kaunarta wato S.MAN d'akin Mama ta shiga tace ta bata aron kud'i zataje unguwa idan ta dawo zata bata, Mama ta tattara 'yan canjin ta duk ta bata tafita ta sami mai abin hawa tayi gaba.
abakin get d'in gidan S.MAN aka dire ta tabiya mai adai-daita kud'in sa kana ta karaso bakin get d'in tashiga knocking.
maigadi yabud'e karamar kofa tare da leko kansa yana fad'in
"Wane ne?."
Suhailat ta ce
"Ni ce."
"To wace ce ke."
mai gadi yafad'a yana waigen gefe da gefe.
ta ce "Eh baka sanni ba kam ni ce Suhailat kanwar S.MAN ce ni yana ciki ne?."

"Wa ce kanwar tasa ni sam ban gane ba Yusrah kad'ai na sani kanwarsa."
yayi maganar yana kokarin rufe kofar
da sauri cikin hura hanci ta ce
"Sai kuma akace maka itace kad'ai kanwar sa bashi da 'yan uwa, to ni 'yar yayan Baban sa ne Alhj Musa."
maigadi ya ce
"Au to yanzu kikayi bayani to dai oga baya ciki sun fita da abokin sa."
ta ce "SEEDRAH fa tana ciki?."
ya ce "Eh ita tana ciki."
ta ce "To bari na shiga zan jirasa ya dawo."

Ya bud'e mata kofa tashiga tana tafe tana karewa gidan kallo a fili ta ke fad'in
"Duk ranar dana zamo matar gidan nan ko bacci bazan iya ba wannan gida wane aljarnar duniya, S.MAN had'ed'd'en namiji ne shiyasa gidan sa ma yazamo na daban Allah ka mallaka min shi."
da ire-iren wad'an nan maganganun ta isa kofar da zai sadata da ainahin side d'in gidan knocking tayi tare da murd'a handle ta tura kofar tashiga tana rera sallama.
"Wow." tafurta lokacin datayi tozali da tsararren katafaren parlour, wani irin taku take tana juyi cikin parlour'n daya gama tafiya da imanin ta, aduk mafarkin ta nason auren mai kud'i bata tab'a hasasho irin wannan duniyar ba.
sai take jin kanta lallai ita mai sa'a ce a fili ta furta
"Ya S.MAN duniya ce."
hoton sa dake like cikin parlour'n ta isa inda yake tana kare masa kallo wani murmushi ta sake tare da mika hanu tashafo kyakkyawar fuskarsa tana mai cigaba da sakin murmushi.
"USMAN SULAIMAN S.MAN had'ad'd'en namiji babu wani abu ragagge tare da kai."
tawani lumahe ido tana mai cigaba da shafa hoton...

SEEDRAH dake kwance cikin d'aki tajiyo sallama asama jin bata kuma ji ba sai tayi zaton ko kunnen tane kawai yajiyo mata ba dai-dai ba, har ta gyara kwanciyar ta sai kuma ta mike ta fito dan tabbatar wa ganin ta.
can ta hango Suhailat tsaye jikin hoton S.MAN tana ta faman shafawa tana sakin murmushi cike da shauki.
ido ta waro sai kuma tatafi da gudu taje ta rungume ta tana fad'in
"Oyoyo Aunty Suhailat dama ke ce ke sallama."
Suhailat tajuyo tana kare mata kallo daga sama har kasa dafad'in
"Kaji manya ana daga ciki anbaje."
dariya SEEDRAH tayi taruko hannunta ta janyo ta suka zau na
tana fad'in "Nayi matukar farincikin ganinki Aunty Suhailat wlh nayi kewarku sosai ina so naje gida na ganku amma wannan S.MAN d'in ya hana ban isa nafita ko nan da canba yahana maigadi ma yabarni na fita,
yasu Mama da Baba Umma Aunty Halimatu dasu Walida da Walid sai nake ji kamar shekara nayi ban ganku ba."
sosai take nuna tsantsar farincikin ta naganin 'yar uwar tata.

Suhailat ta ce
"Ke dalla dakata ba wannan ba yana ganki haka ban ga kin wani kara jiki ba,me kike jira kina wannan katafaren masarautar da baki aje kiba ba?,
sai dai kin kara haske kam fatar nan ta murje tayi luwai-luwai da ita anji sanyin AC."
"Haba Aunty Suhailat ina tambayar ki gida kina yimin zancen kiba taya ma za ayi nayi kiba ina zaman yiwa wani katon gardi bauta, duk kewar gida da Mamata ya addabe ni."
fuska Suhailat ta yamutsa tare da gyara zaman ta tana dad'a bajewa kan lallausar kujera kana tabi parlour'n da kallo sannan ta mai da duban ta kan SEEDRAH ta ce
"Mene ne a gidan da har zaki rika tunoshi har ya hanaki kwanciyar hankali in banda tarin yunwa da wahala,
ke kin san yanzuma su Umma su suke ciyar da kansu har shi Baban ma su suke d'an sakura masa wani abin yanzu komai yadad'a tab'arb'ancewa,
ki mance da wannan kedai kibaje kafarki cikin wannan daular har ranar da zan shigo gidan nan amatsayin matar Ya S.MAN,
daga ranar zaki 'yantu ki cigaba da zama a matsayin kanwarmu ba 'yar aiki ba,
kin ga kema ko ba komai zaki mori rayuwa."

Wani irin kallo SEEDRAH ke bin Suhailat da shi mai cike da d'inbin tarin mamaki sannan ta ce
"Aunty Suhailat kinsan me kike fad'a kuwa?,
duk talaucin gidan mu yafiye min nan sau dubu ko da za'a rikayin sati ne kafin a d'aura tukunya,
yanzu Aunty Suhailat mutumin da yake wulakanta Baba baisan darajarsa da kimarsa ba shine har kike mararin auren sa,
ina abin so agurin S.MAN wan da baisan darajar mahaifinki ba,
dan Allah Aunty Suhailat ki siya mana mutunci ba kaskanci da tozarci agurin S.MAN ba."
wani kallon shekeke Suhailat tabita da shi kana ta ce
"To me yakeyiwa Baban nifa sam bana ganin wani laifin sa akan kud'insa yake yin komai, kuma a wannan zamanin ko d'an ka da ka haifa acikinka ba lallai bane ya iya biyoka bashin makudan kud'ad'en da S.MAN yake bin Baba,
duk abun da ya faru ai laifin Baba ne in da ya biyasa kud'in sa da duk hakan bazata rika faruwa ba, baisan uzirin saba wata kila yana da bukatar amfani da kud'in sa ne shikuma ya hana sa, yabar masa gidan kawai yasiyar ya rike kud'in sa, ai ana wankan dare dan gobe ne kin ga gobe bazai kara basa bashi ba."
SEEDRAH data gama cika har wuya ta wasa mata harara ta ce
"Amma gaskiya Suhailat bakida cikakken lissafi uban daya haifeki wani can da tarbiyya bata ishe shiba yafi miki shi."
shewa Suhailat tayi har da tafa hanu ta ce
"Au Aunty'n ma an jingine shi a gefe sai Suhailat d'in kawai, to naji ni dai ko ma me zaki ce kan S.MAN bafa zan fahimce ki ba dan ke yarinya ce har yanzu da sauran ki tukun, wai ma dan Allah yafad'a miki ina zaije da yaushe zai dawo dan ni gurin sa nazo ba gurin ki ba."
tsaki SEEDRAH ta ja tamasa a kusa da ita ta koma gefe tana fad'in
"Yanzu kuma amsar a gurin sa zaki samu kijira dawowar sa."
fuska Suhailat ta yamutsa ta ce

"Ke dai bazaki tab'a canza halinki ba da wannan d'an banzan tsiwa da rashin kunyar."
baki ta murgud'a mata ta ce
"In dai a kan gaskiya ce sai dai a shekara ana ce min mara kunya suma masu fad'ar ai ba kunyar ce ta ishe su ba."

Suhailat zatayi magana aka turo kofar parlour Sager na gaba S.MAN nabiye da shi rike da waya a kunnen sa yana magana.
Suhailat na ganin sa ta mike tana wani karairaya tun kan su karaso cikin parlour'n take fad'in
"Sannun ku da dawowa."
Sagir ne ya amsa da yauwa S.MAN kam karasawa ya yi can kan kujera dake gefe ya zauna, har lokacin yana waya.
Sagir ma ya zauna yana fad'in
"Sannunku da gida."
cike da karairaya Suhailat ta zauna tare da gaishe sa ya amsa cikin sakin fuska.
S.MAN sai da yakai tsawon mintuna biyar kafin ya sauke wayar, Suhailat na ganin haka ta suke murya cikin tsigar jan hankali ta ce
"Barka da warhaka Ya S.MAN ya gida ya aiki."
batare da ya d'ago ya dubi in da take ba ya ce
"Lafiya." a takaice.
saikuma yasoma magana
"Ke ina abinci ko sai ance ki kawo ne kafin ki kawo."
sarai SEEDRAH tasan da ita yake tayi masa banza sai ma kokarin mikewa tayi tabar gurin dan bazata iya ganin rashin darajar da Suhailat ke son siya musu ba.
a hatsale ya d'ago dan yasan taji sa rai, ganin haka yasa
Sagir saurin cewa
"SEEDRAH kawo mana abinci munkwaso yunwa bamu tsaya munci abinci a in da mukaje ba."
"Rokon ta kake ko da sisin Alhj musa ne cikin kayan abincin gidan nan."
S.MAN yafad'a yana tsare Sagir da ido
murmushi Sagir ya yi ya ce
"Bata ji abin da ka fad'a bane shi yasa na fad'a mata."
baki ya tab'e.
SEEDRAH kuwa kugu ta rike tana yi masa kallon sama da kasa kana ta ce
"Ka saisaita kalaman ka dan shi d'in ba sa'an yin ka bane uba ne shi daya haifa."
ganin yan da yawani d'ago a fusace da sauri Sagir ya ce
"Dan Allah S.MAN."
bai saurare sa ba ya mike SEEDRAH ko na tsaye bata gudu ba dan zuciyar ta yagama bushewa.
saukar mari taji a kan bakin ta har sai da bakin nata ya fashe gefen lips d'in ta yana tsiyayar da jini.
zai kuma kara mata Sagir ya rike hannunsa ya ce
"Ya isa Haka dan Allah ke SEEDRAH je ki tafi nace."
ganin yan da S.MAN d'in ke huci yakuma ce mata ta tafi.
da sauri ta juya had'e da sassarfa yayin da zuciyar ta ke tafasa duk azabar zugin da bakinta ke

mata ko d'igon hawaye babu a idon ta.
d'aki ta shiga tasoma dube-dube can ta hango wuka data yanka appel d'azu tajanyo wukar tajuyo da sauri da zummar fita taje ta same sa sai ganin sa tayi a bayan ta.
wukar ta d'ago tana fad'in
"Ni ba jakar ka bace ba a kawo maka jaka ba aiki kad'ai aka kawo ni na yi a gidan ka aduk san da kayi kokarin aibanta mahaifi na bazan kyaleka ba ko da hakan zai zamo karshen numfashi na aduniya,
mugu azzalumi."
hannunta yarike yamurd'e ya karb'i wukan,
yatura ta jikin garu yamatse ta tare da shako wuyanta yasaka wukar a wuyan ta,
ya jefa kwayar idanunsa cikin nata kana ya soma magana
"Shi waye Alhj Musan da kika isa ki hana magana a kansa ke har wani uba kike da shi anan!!."

A guje Sagir ya iso in da suke yana fad'in
"Subhanallahi S.MAN meye haka lafiyar ka kuwa."
da sauri yaruko hannunsa dake rike da wukar ya ce
"Ka dai na fa ka bari dan Allah kada ka jawo mana damuwa."
cikin fusatacciyar murya ya ce
"Meye abun damuwa akan kashe wannan yarinyar sai na canza miki kamanni saina illataki mara kunyar banza."
ya gara kanta da jikin garu.
da sauri Sager
ya daddage ya janye hannunsa kana yakukkusa yashiga sakanin su yatura shi gefe yana fad'in
"Dan Allah kayi hakuri ka kyale ta kawo wukar nan."
ya karb'i wukar yajanyo hannunsa yana cigaba da bashi hakuri suka fita a d'akin.
sai a lokacin SEEDRAH ta sulale kasa tare da sakin kukan bakin ciki...

A parlour kuwa Suhailat na ganin fitowar su ta mike tana wani yauki da kaud'i ta iso gaban S.MAN ta narke murya tana fad'in
"Sorry bro kasan yarinya ce har yanzu kuruciya na damin ta,bari na d'auko ma abincin."
hannu ya d'aga mata kana ya juya yanufi step's ya haura sama.
Sagir ya dube ta ya ce
"Je ki bata hakuri kawai bari ni zan ji da shi."
ya wuce ya je dinning ya d'au tray'n data shirya abinci ciki ya haura sama ita kuma Suhailat ta shige d'akin da SEEDRAH ke ciki.
har lokacin tana zaune dirshen a kasa tana tsiyayar da kwalla, Suhailat ta zauna bakin gado ta kalle ta tana fad'in
"To ni ban maga abin da zaisa na baki hakuri ba, rashin kunyar ki yajanyo miki duka idan baki daina rashin kunya ba to kuwa bazaki fasa shan duka ba, ke fa baki fahimci Ya S.MAN bane, bafa zagin Baba yake ba, wai ke daga zaran yakira sunan Baba sai ki jingina hakan da zagi, gaki ke a dole zaki iya tsare masa fad'a haka zakiyi ta shan duka a banza."
kallon Suhailat take cike da bakin ciki tama rasa me zata ce sai kawai ta mike ta shige bayi..
wanka tayi tafito bata ganta cikin d'akin ba.

Suhailat ko tun shigarta bayin tafito parlour tana zaman jiran S.MAN ya sauko.
ta b'ata tsawon lokaci zaune har ta fara tunanin ko ta haura samanne ta same shi,
nan ta jiyo takon sauka daga step's da sauri ta d'ago ganin shine tashiga wani kwarkwasa da fari da idanu.
ya iso cikin parlour'n can kan kujerar daya zauna d'azu ya isa ya d'au wayar sa daya bari a gurin dan dama abin da ya sauko da shi kenan.
ganin yana kokarin barin parlour'n ta yi saurin ce wa
"Am Ya S.MAN dama fa gurin ka nazo."
da ido ya bita batare da yace komai ba
ganin haka yasata kuma narke murya tana wasa da yatsun hannunta sannan tayi d'an kasa da murya ta ce
"Ko zaka iya bani wayar ka na saka maka lamba ta."
"Babu bukatar hakan zaki iya tafiya."
yafad'a tare da nuna mata kofar fita.
zata kuma magana ya d'aga mata hanu tare da kuma yi mata alama da ta tafi,
simi-simi taja kafa tana waigen sa tayi waje.
shiko tsaki yaja ya haura sama.

Kwanan Sagir uku yakoma Kano dan acan yake da zama da matar sa da 'yarsu d'aya.
shima d'an Kaduna ne aiki ne yakai sa can Kano aduk san da yashigo Kaduna har idan S.MAN na kasar gidan sa yake sauka har yagama abin da zaiyi ya koma...

Bayan kwana biyu

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08034690723_

*___________________________________*

*🌈 K AINUWA W RITER'S✍🏼*
* A SSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga  shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*___________________________________*
```

.

Yanda yake tsotsar bakin ta da kuma kankame ta, shiya farkar da ita daga nannauyar baccin da take.
idanunta suna rufe dan har alokacin bata gaskata farkawan nata ba, dan tafi yar da duk acikin bacci take.
kokarin juyi take dan son gusar da wannan mafarkin da take amma ta kasa, duk yanda taso tayi juyin ta kasa sai taji kamar duk an daddanneta.
a hankali tashiga bud'e idanunta,
dishi-dishi take gani duk da kuwa hasken wutan daya haske cikin d'akin, dan da zata kwanta bata sami damar kashe wutan bama tayi kwanciyar ta.
kuma ware idanunta tayi sosai tana kikkifta su.
ta dage ala dole dai so take ta farka a baccin dan abun da take ji da gani yanzu taki gaskata idanunta biyu ne.
sosai ta ware idanunta a kan fuskarsa, idanunsa a lumshe sai tsotsar bakin ta yake kamar ya sami sweet.
wani irin razana da firgici ne suka dirar mata,
da gaske ba mafarki take ba. da karfi ta daddage ta janye bakinta wani uban ihu ta kurma da karfin tsiya, da ya sashi dawowa cikin hayyacin sa.
"Wayyo Allah nashiga uku na wayyo Mama wayyooo!!."
takuma fasa kara mai karfi.
da sauri ya sake ta ya zare jikin sa ya mike a kanta yana dafe kai.
cikin matukar tashin hankali tamike ta janyo zaninta tana kare jikin ta.
tsoro ne mai tsanani ya rufe ta murya na rawa tashiga nuna shi da yatsa tana fad'in
"Me kamin? kamin wani abu ko? wlh idan har kamin wani abu kotu ce zata rabamu da kai mugu azzalumi."
duk maganar da take a matukar tsorace take daganin yanayin sa.
 imagine tashiga yi gashi nan yana sex da ita,kara ta saka tashiga yamutsa gashin kanta nata fad'in
"A'a wlh a'a idan kamin wani abu wlh bazan yafe maka ba sai na d'au mataki a kanka."
"Shiiit rufamin banzar bakin nan naki ko na fasashi bacci ne yakawo ki gidan nan ko aiki."
maganar ya ke cikin wata iriyar murya da ta gama narkewa cikin wutar sha'awa, ya kuma murtuke fuska tamau alamar ba wasa.
da kyar ya iya tattaro jarumtarsa ya sauka akan gadon da kyar ya mike tsaye yana gyara zaman MAN d'in sa dake kokarin fasa wando ya fito batare da nuna wata damuwa ko shakko ba.
rumtse idanunta tayi da karfi kirjinta na dukan uku-uku.

dai-dai ta tsayuwar sa ya yi, ya na tangad'i kamar wanda yasha wani kayan maye ya nufi kofa ya bud'e ya fita.
tana jin fitarsa ta bud'e idanunta da sauri ta fad'a jikin pilo ta saki kuka.
sosai take kukan cike da bakin ciki da takaici,
cikin muryar kuka sosai ta ke fad'in
"Wayyo na
shiga uku na Allah wadaran nauyin bacci irin nawa, dama Mama da su Aunty Suhailat sun sha fad'a min watarana sai an sace ni ina bacci, to gashi yau mugun  nauyin bacci na ya janyo anyi min fyad'e ba tare da na sani ba, shi ke nan rayuwa ta ta zamo ragaggiya."
kuma saka kuka tayi, tana tausayin kanta tabbas ta zamo abin tausayi.
i dan ba dun kariyar arzikin daya sami Baba ba me zai kawo ta gidan sa har ya nimi keta mata haddi. lallai talauci masifa ce,
badun kariyar arziki ba da bai karb'i bashin sa ba ko da ya karb'a kuma da ya mai da masa da bata zo gidan nan amatsayin 'yar aiki ba, da duk haka bai faru da ita ba.
ganin kuka bazai mata magani ba ta mike tashiga bathroom.
 dudduba jikin ta tayi sosai bata dai ga alamar fyad'e tattare da ita ba hasali ma kuma pant d'in ta yana jikin ta kuma babu wani d'igon damshin wani abu.
ko da ta fito a bakin gado ta zauna tana tunanin ta ina ma ya shigo d'akin ita da ta kulle kofar kuma taga da zai fita ma sai da ya bud'e da key d'in da ta bari jikin kofar,
"To ko ta sama ya shigo."
ta d'aga kai ta kalli saman d'akin babu ta in da mutum zai iya shigowa a yanayin tsarin ginin gidan.
"To ko tsafi ya ke ya shigo ta hanyar tsafin sa."
haka tayi ta tambayar kanta bata sami amsa ba.
daga karshe dai rakub'ewa tayi a gefen gado tana jiran gari ya waye dan bazata kuma komawa wannan baccin nata mai kama da mutuwa ba..

Washegari bayan ta idar da sallar asuba tana zaune kan sallaya tana azkhar, aka turo kofa  da sauri ta d'ago tana duban kofar.
daga bakin kofar ya tsaya ya hard'e hannu a kirji cikin tamke fuska ya ce
"Oya tashi ki fita yanzu ki fara aiki ki b'ata lokaci ki gani."
yana kaiwa nan
ya juya ya fita.
bayan sa tabi da harara tare da jan tsaki a fili ta furta
"D'an rainin hankali ko ya d'auka kowa irin wancan karuwar da ta ke kawo masa kanta har gida ne, d'an iska kawai missttt."
takarashe maganar da jan dogon tsaki.
sai da ta kammala addu'o'i'n ta kafin ta mike
 tafito batare da ta cire hijabin jikin ta ba.
can ta hango sa gurin motsa jiki da sauri ta wuce ta haura sama ta gyara kana ta sauko ta shiga kichin.
ko da ta gama had'a breakfast tafito baya gurin ta haura masa da breakfast d'in.

yana zaune a parlour ya d'au sigari yana kokarin kunnawa, ta iso ta dire masa tray'n a saman table d'in gabansa tana yamusa fuska.
ta mike da zumbar barin gurin ya ce
"Wad'an can kayan da kika ciresu cikin wanki su ba kayan wanki bane?."
"Bazan iya wanke su ba."
ta fad'a a takaice ta na kokarin barin gurin
"What." yafurta tare da aje sigarin hannun sa ya nuna mata kofar bedroom d'in sa ya ce
"Wuce ki je ki wanke su."
fuska ta yamutsa wai tunanin sa zata wanke masa gajeren wando da boxes da kuma singilet ne, duk da bada hannunta zata wanke ba washing machine ne zai wanke su, bazata iya d'aukarsu da hannunta ta zubasu cikin injin ba.
ta ce "Ni fa bazan iya ba su d'in ma bazaka iya wanke su ba sai an maka."
ganin yana kokarin mikewa ta d'aga kafa da sauri zata bar gurin ya fizgota ta garu da jikin sa.
kiciniyar kwatan kanta take tana fad'in
"Ka sake ni na rantse bazan wanke ba sai dai ka wanke abin ka."
d'an zubawa lips d'in ta ido ya yi yanda take motsasu.
lumshe idanunsa ya yi tare da kuma bud'e su lokaci guda.
ya sakalo hannunsa guda kan kugun ta ya janyo ta zuwa jikin sa.
ido ta waro jin abun da ya matan zaton ta wani salon muguntan ne yake shirin yi mata.
sai kawai taji ya tallafo kanta da d'aya hannunsa ba zato taji bakinsa cikin nata.
wani irin waro ido tayi ya yin da zuciya da jikin ta duk suka d'auki rawa.
duk yan da taso ta kwace kan ta ta kasa yakai tsawon mintuna biyar yana tsotsar bakin ta.
kana ya sake ta ya zube kan kujera tare da d'aukar sigarin sa ya kunna yashiga zukarsa da sauri-sauri.
wani irin mutuwar tsaye tayi mamaki had'e da tsoro suka lullub'e ta.
sosai jikin ta ke rawa amma ta daure ta dube sa cicin dakiyar zuciya ta ce
"Wlh Allah ya isa tab'a jiki na da kayi, wai ma me ka d'auke ni ne kam?, kana tunanin kowa irin wancan 'yar iskan da ta ke kawo kan ta gare ka ne,
to wlh kada ka kuskura kasake yunkutin tab'a min jiki dan wannan jiki mai daraja ce da ki ma, ba irin na ballagazan mataye masu raba jikin su sadaka a titi ba."
hayakin sigarin sa ya buso tare da d'aura yatsansa kan lips sa ya ce
"Shiiit wu ce ki b'ace min da gani."
ya yi maganar tare da lumshe idanunsa yana cigaba da zukar hayakin sa.
"Mssstt." ta ja dogon tsaki kana ta juya tab'ar gurin tana maganar zuci
"D'an iska d'an kwaya d'an shaye-shaye bayi da aikin yi sai shan taba, yawani samin bakin shan tabarsa cikin baki msstt."
takuma jan wani tsakin.
tara miyau tayi cikin bakinta tawuce bathroom taje ta zubar, ta d'au burosh ta wanke bakin ta tana yamutsa fuska.
tafito ta zauna bakin gado tana d'aga kiran Kamal da ya shigo wayar ta yanzu.

Bayan kwana biyu

Da yammacin ranar SEEDRAH na like da waya tana waya da abar kaunarta Kamal suna karantowa junar su karatun soyayya.
cikin hirar ta su ya ce.
"My SEEDRAH." ya kira sunanta ta ce
"Na'am My Kamal."
"Kifito gani a kofar gida."
ido ta d'an waro ta ce "Wani kofar gidan?."
"Gidan S.MAN nagaji ina bukatar ganin ki kin san dai zuciyata tayi matukar kokaki na tsawon watanni bazata iya ci gaba da hakuri ba ki fito na ganki dan Allah."
numfashi taja a zahirin gaskiya itama tana bukace da son ganin nasa.
"Gani zuwa." tafad'a tare da mikewa tsaye ta kashe kiran.
bata jima da yin wanka ba dan haka bata bukaci yin wankan a yanzu ba.
kaya ta ciro cikin wardrobe riga da siket na les had'e da gyale ta saka kayan daya zauna d'amas a jikin ta,
pauda da man lips kad'ai ta shafa amma fuskarta yayi wani irin sihirtaccen kyau.
ta saka 'yankunne da sarka kalar kayan kana ta kashe d'auri mai kyau.
ta zura takalmi mara tudu sosai kana ta feshe jikinta da turare ta yafa gyalen a kafad'a ta d'au wayar ta ta fito ta nufi bakin get..

Baki da hanci maigadi ya bud'e yana kallonta harta nufowa inda yake,
"Masha Allah kai Allah yayi halitta anan wai ashe dama haka take ban tab'a ganin ta a haka ba, kullum da katuwar hijabi fuskarta a d'aure." yafad'a a fili yana washe baki.
SEEDRAH kuwa kayataccen murmushin dake shinfid'e kan fuskarta ta dad'a fad'ad'awa ta karaso in da yake.
wani murmushi takuma sakar ma sa ta ce
"Barka da warhaka sannu da aiki."
baki ya kuma washewa ya ce
"Yauwa yauwa barkanki dai sannunki."
kai ta gyad'a da murmushi ta ce
"Akwai bako a waje kabud'e masa ya shigo."
d'an jim ya yi kana ya ce
"Yallab'oi fa bai sanar min da zuwan wani ba, yau wa gashi can ma daga sama yana hango mu."
yayi maganar yana nuna S.MAN dake tsaye can saman bene ya zura hannunsa d'aya a aljuhu d'aya hannun nasa kuma na kare da waya a kunnensa yana magana.
kai ta d'aga ta kalleshi,
taga idanunsa a kanta.
ta saki murmushi kana ta maida dubanta ga maigadi ta ce
"Au ashe bai fad'a maka ba shi ya ce nazo na sa abud'e masa kofar."
"Au to haka akayi to bari a bud'e masa." da saurin sa yamasa jikin kofar yakuma washe hakora yana bud'e karamar kofa..

S.MAN na tsaye yana kallon su, duk da baya jin abun da suke fad'a. amma ya fahimci dashi ta yi karya maigadi ya bud'e kofar, dan yasaka masa dokar da bazai tab'a iya ketare shi ba muddun idan ba shi yasa shi ba.

Kamal ya sako kansa cikin gidan yana amsa gaisuwar da maigadi yake mika masa fuskarsa d'auke da murmushi.
ya yin da gaba d'aya hankalin sa ke kan SEEDRAH da ganinta ke kokarin zautar dashi.
wani murmushi mai cike da so da kauna suka rika sakarwa junan su tamkar zasu rungume juna.
"Bismillah."
ta fad'a tana nuna masa hanya da hannu.
a hankali suke takawa suna cigaba da sakar wa junan su murmushi had'e da daddad'an kalaman kauna da soyayya irin na wad'an da sukayi kewan junan su.

Daga can sama kuwa S.MAN har lokacin na nan tsaye  yana kallon su, sai dai a yanzu fuskarsa babu annuri.
ganin ta nufo da Kamal gurin hutawar sa da sauri yajuya yanufo kasa..
suna kokarin zama S.MAN yakaro gurin.
ganin sa yasa Kamal fasa zaman cikin nuna farinciki da jin dad'in ganin masoyin sa agaban sa ya mika masa hannu yana fad'in
"Barka dai gwarzon jarumin mu nayi farinciki ganin ka sosai."
Kamal ya ruko hannunsa batare da ya mika masa hannun nasa ba, yarike gam yana mai farin cikin ganin d'an kwallon da ya fi kauna arayuwarsa.
yaciro wayar sa yamusu selfee yana cigaba da fad'in
"Yau zansha comments a media  dan kuwa yanzu zan d'aura hoton nan."
SEEDRAH kuwa fuska ta yamutsa ganin yanda Kamal d'in yawani zake,
shiko S.MAN sai wani shan kamshi yake.
ta ce "My Kamal zauna bari na kawo maka ruka."
ta d'an dubi S.MAN ta ce
"Wannan shine Kamal mijin da zan zaura."
takarashe maganar da kad'a narkakkun kwayar idanunta.
kana tajuya ta nufi ciki dan d'auko wa Kamal abin sha.
kichin ta shige ta d'au d'an madaidaicin tray ta d'aura drink's kala biyu a kai had'e da glass cup.
ta juyo zata fita sai ganin mutum tayi a gaban ta.
wani kallo ya wasa mata
"Yaushe kika sami gurin zama da har zaki shigo min da wani gardi d'an kauye cikin gida, har da d'aukar drinks zaki kai masa, da kud'in Alhj Musa aciki a ka siya."
harara ta wurga masa tare da murgud'a masa baki ta ce
"Kagode Allah ma da har wani yashigo gidan ka yaci abinci ko sha wata kilama ta sanadiyyar haka kasami gafara da rahamar Allah, kan abubuwan da kake aikatawa na sab'on Allah, Kamal mutumin kirki ne mutumin kwarai in har iskanci da shaye-shaye shine waye wa to har abadan bazai tab'a wayewa ba zamansa a hakan kuwa yafiye masa rayuwar shaye-shay...."
bata kai ga karasawa ba taji saukar mari a fuskarta.

zafin marin yasata  sakin tray'n yafad'i kasa ya tarwase.
ya fizgota ya had'ata da jikin garu ya matse ta, sosai kake iya hango b'acin rai kan fuskarsa.
cikin kakkausar murya mai nuna zallar b'acin rai ya ce
"Kin tab'a kamani da kwaya ne?! kin tab'a ganina ina shaye-shaye?! kin tab'a ganin wani kayan maye cikin gidan nan!!?."
yafad'a cikin karaji sosai yakuma matseta.
"Idan kika sake jifana da kalmar d'an shaye-shaye sainaga wan da ya tsaya miki!,
 bantab'a shan wani kayan maye ba ni ba d'an shaye-shaye bane, sigari kad'ai nake sha shin ban tab'a fad'a miki bane!."
waye kema da har sai na rika fad'a miki abin da yashafi rayuwata iye!."
yasaka kafarsa ya take nata had'e da murkushe sai da ta saki karar azaba, kana yacigaba da fad'in.
 "Kefa 'yar aiki ce wakawai wacce ubanta yaci bashi ya kasa biya, wlh idan kika sake dangantani da d'an shaye-shaye sai na b'ab'b'allaki na taraki anan!!."
ya hankad'a ta gefe yajuya yafita a kichin.
"Wlh Allah ya isa mugu azzalumi kawai."
ta tsunkuya ta rike kafarta tana yarfe hannu.
Allah ya isa tarika ja masa yafi cikin kwando,
ba karamin zafi da rad'ad'i kafarta yake mata ba.
Kiran Kamal ne yashigo wayarta bayan ta d'aga ya ce "My SEEDRAH natafifa yayan mu ya ce akwai abun da yasaki kiyi masa a ciki zan dawo idan
kin gama."
shiru tayi bata iya cewa komai ba. ab'angaren Kamal d'in ma kashe wayar ya yi, SEEDRAH ta mike tana bin wayar da kallo ta ja kafarta tana d'in gishi ta fito.
a parlour ta ganshi zaune da waya a kunnensa yana magana.
harara ta wurga masa tare da jan tsaki mssttt.
harta gotashi ta ji ya ce
"Zo nan fitsararriya mara kunya wa kike wa tsaki."
a kufule cike da jin haushinsa ta ce
"Da wan da ya tsargo."
takarashe maganar da murgud'a baki cike da tsiwa tashige d'aki.
tana kokarin rufo kofar ya sako kansa cikin d'akin.
ido ta kura masa tar cike da tsana kana ta yamutsa fuska.
shiko kan lab'b'anta ya kura wa ido kana ya matsota.
tabud'e baki zatayi magana kawai ta sinci bakin sa cikin nata, wani irin tsotsa yake mata mai had'e da mugunta.
ido tarika ciccirewa tana ture shi a jikinta,
kana daga bisani ya sake ta, ya ture ta gefe yafice cikin d'akin.

Zubewa tayi a bakin gado tare da sauke numfashi mai sauti, sai kuma da sauri takai bayan hannunta ta goge bakinta.
A fili ta furta "Bazai yiwuba."
sai kuma da sauri ta mike tafita bata ganshi a parlour'n ba, sama ta haura nan ma baya parlour,

ta isa bakin kofar bedroom d'in sa ta bubbuga da karfi, zata kuma bugawa taji an tab'ata ta baya.
da sauri ta waigo ad'an razane hayakin sigarin daya zuka ya fesa mata a fuska.
da sauri ta kawar da kanta had'e da d'anyin tari.
hannu yasaka yajuyo fuskarta tare da yi mata tambaya da ido alamun me ya kawo ta.
da sauri ta janye fuskarta tana kokarin barin gurin dan hayakin bakaramin tada mata hankali ya yi.
ya dakatar da ita ta hanyar ruko hannunta ya janyo ta jikinsa kana ya maidata ya mannata da jikin garu yasaka hannu ya kare ta ta hanyar dafe jikin garun.
sigarin hannunsa ya yar kasa kana ya take da takalmin sa, d'aya hannunsa yakuma sakawa ya dafe jikin garun yazamana da yasata a tsakiyarsa.
da ido yakuma yi mata tambayar me ya kawo ta.
kai ta kawar gefe tare da saka hannu tashiga ture kirjinsa.
rankwafo da kansa ya yi gefen wuyan ta tare da fesa mata numfashi batare da ya d'ago kansa ba
ya ce
"Idan rashin kunya kika zo min zaki gwammaci dama baki zo ba, oya wuce kibar nan."
yafad'a yana janye hannayensa, ai kuwa da sauri taja kafafunta tayi gaba.

Sai da ta dawo d'aki take jin haushin kanta dama tsayawa tayi ta ja masa layi a kan abubuwan da yake mata.

A b'angaren S.MAN kuwa bathroom ya wuce yana matse MAN d'in sa daya ke ta zillo cikin wando.
kayan jikin sa ya tub'e ya sakarwa kan sa ruwa yana jan tsaki.
ya b'ata lokaci yana tsaye ruwa na sauka a kansa bai kuma sa Man d'in sa ya kwanta ba tamkar dad'a kara masa girma da kumburi a ke.
jin ana kiran salla yasashi yin al'wala ya fito.
yayi shirin zuwa masallaci ya tafi.

Bayan SEEDRAH ta idar da sallar isha ta fito ta nufi kichin.
kayan tea d'in sa ta had'a masa had'e da ruwan zafi a flas ta kwasa ta haura sama.
bedroom d'in sa ta nufa sanin bataji motsin dawowar sa daga masallaci ba.
tana kokarin dire tray'n saman bedside d'in da take aje masa a kai ya bude kofar bathroom ya fito d'aure da towel a kugunsa.
hannunsa na kan MAN d'in sa yanata  kokarin gyara zaman sa dake son kwance towel d'in sai tsaki yake ta ja akai-akai.
da sauri ta waigo jin karar kofa ai kuwa ta ture flaks d'in yafad'i kasa ruwan ciki ya wasu mata a kafa.
kara ta saka tare da tuma tsalle tana yarfe kafar bata ankara ba taji tayi karo da abu, ga kuma wani abun da yawani zungure ta kamar wani muciya.
"Wayyo Allah." takuma fad'i tana cigaba da yarfe kafar.
hannu ya saka ya rukota gaba d'aya yan da take wani tsalle had'e da juyi gaba d'aya ilahirin

jikinta motsawa suke, hakan kuwa ya haifar masa da wani irin mashahuriyar fitinanniyar hautsunar kwakwalwa.
MAN d'in sa dayake ta fama da shi tun d'azu sai wani zullo yake tamkar zai tsinke yakara kumbura tamkar zai fashe.
matseta ya yi sosai ajikinsa yashiga kissing d'inta tamkar zai cinye ta.
tuni ta nimi zafin nan ta rasa tashiga kokuwar kwace kanta hankali a matukar tashe.
wani irin waro ido tayi jin hannunsa na yawo kan ababen kirjinta yayin da bakinsa kuwa ke sarkafe cikin nata, hannunsa guda kuwa na bayan ta yana kokarin zuge zip d'in rigarta.
"Innalillahi wa Inna ilaihirraji'un."
abunda take furtashi cikin zuciyarta ke nan.
da karfi ta daddage ta ture shi a jikin ta dai-dai lokacin da ya zuge zip d'in rigar nata da gudu tabar d'akin amatukar tsorace.
tana shiga d'aki ta maida kofar tarufe tajingina da jikin kofar tare da dafe kirjin ta.
"Fyad'e fyad'e zaiyi min innalillahi wa Inna ilaihirraji'un,
lallai wannan ya tabbata tabbataccen mara imani mugu azzalumi."
ta furta murya na rawa cike da mugun tsoro.
a b'angaren S.MAN kuwa tana fita yazube bakin gado tare da jan tsaki,
hannu yasaka yad'an matse kasan marar sa dake murd'a shi, tsaki yakuma ja ganin yan da MAN d'in sa take ta wani irin zillo wane zata tsinke.
wani tsakin yakuma ja tare da fad'in
"Mayyar yarinya kawai."

A daren ranar duk bacci irin nata sai da ta raba daren kafin bacci ya d'auke ta. shima d'in cikin tsoro da fargaban kada ya yi jingina bango yakuma shigowa kamar yanda ya shigo rannan, ta kwanta da shirin goge zatabar gidan dan bazata cigaba da zama tana ji tana gani ayi mata fyad'e arage mata kima ba, yazama dole ta tseratar da kanta daga faruwar hakan.
washegari guri nayin haske tafito da sauri dan tasan zuwa yanzu yagama motsa jikin sa.

Da sauri ta isa bakin get bataga maigadi ba addu'a take Allah yasa kofar a bud'e take, ai ko tana tab'awa taji ta a bud'e da sauri tasa kai tafita.
tana jin mai gadi yana fad'in
"Hajiya dawo wa ya ce ki fita."
Shafa gefen fuskar sa S.MAN ya yi dake kallon duk abin da ke faruwa daga can saman bene ya juya yana cigaba da zukar sigarin sa cikin kwanciyar hankali..

Tafiya take da sauri har lokacin zuciya da jikin ta basu dai na cirawa.
sai da tayi tafiya mai d'an nisa kafin ta d'an sami nutsuwa kana ta tsari adai-daita zuwa unguwar su Nasiba.
a hanya ta kira Kamal ta ce su had'u a gidan su Nasiba.
tana isa ta ce wa mai adai-daitar yad'an jira bari ta karb'o masa kud'i dan bata fito da ko sisiba.
ta shiga ta karb'a kud'i gurin Nasiba ta kawo masa.

Kamal daya hango saukarta daga can kofar gidan su yakaraso.
murmushi suka sakarwa junan su sai kuma ta b'ata fuska.
a d'an marairaice ya ce "Me kuma nayi?."
ta ce "Dan ya ce katafi sai ka tafi ko da ma ba son gani na kake da gaske ba, kabi ka ishe ni da kana son ka ganni."
murmushi ya yi yakama kunnuwan sa ya ce
"Ayi min afuwa amma tabbas babu ko shakka ke nake muradin gani, sai dai gaba da gabanta shid'in babban wa uba ne, ayi hakuri kar a cinye ni da tsiwa."
hararar wasa had'e da so da kauna ta sakar masa kana ta juya ta nufi ciki.
da sauri yabi bayan ta yana fad'in
"Ranki shi dad'e kimbiya ayi hakuri mana."
maman Zeey dake sakar gida tana aiki ganin Kamal nabiye da ita had'e da hannu alamun roko tayi murmushi, tana jinjina girman so irin wannan.
fuska ya marairaice kamar karamin yaro ya dubi Maman Zeey ya ce
"Maman Zeey tayi fushi ki ce baki yardaba idan ta bari zuciyar d'anki ya fashe."
murmushi mai sauti Maman Zeey tayi.
Zeey dake wanke-wanke kuwa waka ta soma musu
"A hayye soyayya ruwan zuma masoyiya tana wahalar da masoyi masoyiya kara wahalar da masoyi idan yana so haka zai jure."
harara ya wurga mata ya ce "Yar sa ido kawai."
tintsirewa da dariya tayi ta ce
"Oh Ya Kamal ni kuma meye nawa."
"Yi fama da wanke-wanken ki." cikin muryar dariya ta ce "Ina kai ma kuwa."
Murmushi SEEDRAH tayi tawuce sashin Nasiba bayan ta kuma gaida Maman Zeey dake ta zolayar ta tawuce sashin Nasiba cike da jin kunya Kamal ya biyo bayan ta.

Tana shiga Nasiba ta taho ta rungume ta cike da murnar ganin ta.
ido SEEDRAH ta waro ta ce
"Ke wai oyoyon naki baya kare wa ne ina shigowa ta d'azu kinyi min so kike ki murkushe mana baby."
dariya Nasiba tayi ta ce
"To ai duk murnar ganin ki ne rabon da nagan ki wata nawa, ga Nabila can ta kullace ki fushi sosai take da ke, har ta haihu taje wankan gida tadawo bakije jin dubata ta."
kai kawai ta girgiza akan ranta ta ce
"Bazaku gane bane wancan bakin mugun daya maida ni matar kulle a gida kamar wacce aka bashi ni abakin bashinsa ya siyeni haka ya maidani."
taja kwafa a fili.
kusa da Nasiba ta zauna inda Kamal ya zauna kusa da abokin sa Mukhtar ke zaune.
SEEDRAH ta dubi cikin ta daya d'anyi girma ba cancanba irin dai girman cikin fari ta ce
"Wai yaushe ne zaki haihu ne kam?."
fuska Nasiba ta marairaice ta kalli Mukhtar fuska a marairace ta ce
"Abban Seedrah yaushe ne zan haihu."
murmushi ya yi ya ce

"Kin kusa saura kad'an Ummie'n Kamal."
baki da hanci SEEDRAH ta bud'e ta ce
"Wai sunan baby's d'in ke nan sunan mu?."
Nasiba ta ce "Eh ai Kamal ne ya saka ya ce idan aka haifi mace sunan ki za a saka mata idan kuma na miji ne sunan sa, jimin son kai fa ni da ma Mukhtar zan saka idan najimi ne."
dariya duk sukayi SEEDRAHA ta ce
"Kai amma naji dad'i sosai My Kamal gaskiya ka burge ni."
ido ya kashe mata ya ce
"Wani abun ma sai kin shigo hannuna zakiga abubuwan burgewa."
hararar sa tayi ta ce "Kafara ko ni bari ma naje gidan Nabila naga baby."
"Sai dai kirika zuwa kina ganin baby'n mutane ke bazakiyi zuciya aga baby'n mu ba ko."
Kamal ya fad'a yana dariya kasa-kasa.
harara takuma wurga masa. Mukhtar shima dariyar ya yi yana bugun kafad'ar sa kana ya ce
"Yakamata kam ayi duba da lamarin nan gimbiya SEEDRAH."
ita dai mikewa tayi Nasiba ma ta mike ta ruko hannunta cikin yin kasa da murya ta ce
"Ya dai naganki haka tun d'azu nake ta karantar yanayin ki kamar ba a dai-dai kike ba."
"Uhm ba komai kawai bana d'an jin dad'i ne."
shiru Nasiba tayi bawai ko dun ta yarda da abin da kawar tata tafad'a ba sai dai dun bata son yawaita yi mata tambaya gaban su Kamal ne amma tabbas ta fahimci tana cikin damuwa.
itako SEEDRAH bata jin zata iya sanar mata da abun da ke faruwa dan tana ganin abun kunya ne a gare ta duk da kuwa Nasiba aminiya ce a gare ta.
tayiwa Nasiba sallama suka fito da Kamal, Mukhtar zai bisu Kamal ya ce ya zauna basa bukatar rakiya bare yaji abun da zasu fad'a.
suna fita kofar gidan SEEDRAH ta dubi Kamal da kyau ta ce
"Kamal kana so na kuwa?."
da sauri ya waro idanunsa ya ce
"Anya kinsan me kike fad'a kuwa amma sam banji dad'in fitar kalmar nan daga bakin ki ba, ko makaho ne ya dafa zuciya ta na tabbata zai fahimci irin girman so da kaunar da nake miki."
ido ta rumtse da karfi kana ta bud'e su a kansa ta ce
"To gobe kaje ka kai kud'in aure na gidan mu."
wani irin tsalle ya tuma tare da fad'i
"Yes yess yesss."
sai kuma ya d'an dai-dai ta nutsuwar sa yana son karantar yanayin ta kana ya ce
"Are you okay."
kai ta girgiza ta ce "Yess I'm okay kayi yadda nace."
"Insha Allah." ya fad'a kana suka nufi gidan  Nabila a kafa suna d'an tab'a hirar su.
ko da suka isa da fari Nabila ta nuna fushin ta kan rashin zuwan SEEDRAH da ta haihu, SEEDRAH tayi ta bata hakuri har ta huce ta d'auki babyn data ci suna Ishmat tayi ta mata wasa kana daga bisani tayi mata sallama suka baro gidan, Kamal ya d'auko mashin d'in sa ya kaita gida.

Tayi missing d'in Mama bata tsaya hira da shi a waje ba ta ce anjima ya dawo, ta shige gida da sauri a sakar gida ta tadda su Mama da gudu tafad'a jikin Mama tana fad'in "Oyoyo Mama."

murmushi Mama tayi dan tayi kewar d'iyar tata ba kad'an ba.
SEEDRAHA ta mike jikin Mama ta zauna gefen ta kana ta gai da Umma sannan ta gaida Maman.
duk suka amsa cikin sakin fuska suna tambayar ta ya aikin nata.
Suhailat da Halimatu kuwa har rige-rigen tambayar ta ya S.MAN ya ke.
mikewa tayi tana fad'in
"Me zai hana kuje gidan ku gano sa."
"Mara kunya halin naki na nan dai."
Halimatu ta fad'a tana hararar ta, bata kuma bi ta kansu ba ta shige d'akin Mama tana shiga ta haye gado tayi kwanciyar ta, ai ko ba jimawa bacci yasami nasarar sace ta, nan tashiga rama baccin da bata samu tayi shi yadda ya kamata ba jiya.
sai wajen karfe biyar da rabi ta farka, tashiga bayi ta yi al'wala ta fito tagabatar da sallar la'asar.
tana zaune kan sallaya Mama ta shigo ta dube ta cikin kula ta ce
"Kin ta shi?."
kai ta gyad'a ta ce "Eh." kana ta langwab'ar da kai gefe ta ce
"Mama yunwa ban karya ba."
zama Mama tayi a bakin gado tana fad'in
"Ga ragowar kunu can da jiya na dama sauran gari daddare nasha na rage,
da safe nasha naso sha da rana naji kirjina na suya sai na hakura ganin zai tada min olsa."
murya ta mararirace ta ce "Kunu kuma Mama abinci dai."
"Uhum SEEDRAH ke nan muna dai kan jiran Baban ku har yanzu bamuga aike ba."
jikin ta ne ya mutu ya yin da taci wasu zafafan kwalla sun ciko mata ido, wato dai Mama bataci abinci ba kenan tun safiya bayan kunun da ta sha wan da jiya ma haka shi d'in ta sha.
"Innalillahi wa Inna ilaihirraji un ya Allah ka kawo mana mafita cikin lamuranmu."
a hankali ta rarrafo ta kwantar da kan ta kan kafar Mama ta ce
"Mama bakiyi waya da su kawu Yusufa bane."
kanta Mama ta shafa ta ce
"Banyi musu waya ba SEEDRAH nauyin tambayar su nake ji duk da nasan bazasu tab'a son gani na cikin wani haliba, amma abaka yau a baka gobe yawuci wasa, wan da ya haliccemu shine kad'ai baya gajiya da bamu kuma munakan rokon sa zai warware mana lamuran mu,
ki tashi ki koma bakin aikin ki ga magriba ta kusa kada dare ya yi miki a hanya."
hawayen da suka zubo mata ta share kana ta d'ago ta gyara zaman ta kan sallaya sannan ta ce..............!

Mommyn Twins ce

🌺 *KARSASHI!* 🌺

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

( _Book 1_)

~Free page~

( _Bismillahirrahmanurrahim_)
_Alhamdulillah Ina yiwa Ubangijin buwaye gagara misali godiya daya kuma a ramin lokaci na kuma dado wa a wannan karon a cikin littafi na mai suna KARSASHI kada ku manta kafin zuwan KARSASHI HAMDAH ya zo muku masoya ku baza kunnuwan ku ku kuma biyo ni cikin labarin nan mai suna ƘARSASHI ina mai yi muku albishir da faranta wa kamar yadda HAMDAH da sauran littatafai na suka saba zuwar muku🤗 KARSASHI salon sa da banne labari ne mai ƙwanƙwasa zuciya salon labarin na daban ne. ku dai ku biyo ni cikin labarin nan kada ku mance da sunan sa KARSASHI! KARSASHI!! KARSASHI!!!_

_Littafin na kud'i ne 400 Account no 3170524141 Rashida Salihu first bank kokuma katin Mtn ta wannan number 08034690723 a tura shaidar biya ta WhatsApp number ta 08034690723_

*__________________________________________*

*🌈KAINUWA WRITER'S✍🏼*
*ASSOCIATION🤝🏻*
```{United we stand and succeed;Our ambition is to entertain & motivate the mind of readers}```
https://www.Facebook.com/kainuwawritersassociation

*_domin shiga shafin mu na Bakandamiya danna nan_*👇🏻
```

https://bakandamiya.com/group/71/Kainuwa-writers-association

*______________________________________*

page 20

"Mama nifa bazan koma ba na dawo gida ke nan, yafad'i wani abun da za ayi masa ya fanshi kud'in sa, ni nagama yi masa aiki, ga su Aunty Suhailat da Halimatu su je suci gaba da yi masa, tun da duk suna son zuwa gidan sa da ma."
"SEEDRAH kasa zaki wasa min a ido, ina kawazucin iyayen nan da nake gani tare da ke?, idan baki taimake ni ba wazai taimaka min SEEDRAH, ke yake da bukatar yi masa ai ki basu Suhailat ba."
suka jiyo muryar Baba daya fad'o cikin d'akin yana sauke waya a kunnen sa, ko ba a fad'a ba tasan S.MAN ne yakira sa yaku yi masa barazanar daya saba.
Baba yacigaba da fad'in
"SEEDRAH ko mai na dad'a tab'arb'arewa ko dubu talatin bana da shi nawa na kaina bare miliyan 30,
a ina zan samu na biya sa, zaman ki cikin gidn shi kina yi masa aiki shine rufin asirina, idan kika ce zaki bar aikin nan to tabbas muma zamu bar gidan nan, ko kud'in d'akin haya d'aya bani da shi sai dai mukoma titi rayuwar mu ta kare a can."
ido ta rumtse da karfi ya ilahi ya lillahi me yake shirin faruwa da ita ne kam.
Baba ya fita ya na fad'in
"Kiyi tunani dai SEEDRAH."
Mama ta ce "Hakuri zakiyi ki koma hakan shine kad'ai rufin asirin mu."
sai a sannan ta bud'e idanunta wanda kake iya hango damuwa had'e da tsoro da fargabar faruwar wani abu cikin su. ta ce
"Mama shin bakwa tunanin me duniya zasu ce a kanmu, ina gidan wani da bashi da mata ina yi masa
ai ki kada kusa duniya tafara zargin mu mana, Mama ina jin tsoro ina jin tsoro Mama, kuyi hakuri ku barni na zauna a nan kusa Halimatu ko Suhailat suje suciga da yi masa aikin dan Allah Mama."
ta karashe maganar da rike hannun Mama gam.
shiru Mama tayi tana nazartar ta, sai kuma ta girgiza kai sannan ta ce
"Ko ma mene ne kisa Allah cikin lamuranki ki tabbatar da tsoran sa gare ki,
duniya kuwa zasu fahimci cewa kima da darajar mahaifinki kika tsare,
kije Allah ya kareki, a kullum da ko yaushe ban gushe ba ina kan yimiki addu'a, ina da tabbaci

da yakini a kan tarbiyyar dana baki."
shiru Mama  tayi da tunani irir-iri a zuciyarta, sai dai bata bari mugun tunani yasami matsuguni cikin zuciyarta ba, addu'a take ubangiji ya tsare mata d'iyarta aduk inda tasa kafarta.

Mikewa tayi ta ce "Mama makaranta na fa?."
"SEEDRAH a wannan halin da muke ciki, kuma  haryanzu ma ba a dawo daga yajin aiki ba."
kai ta girgiza kana ta d'au wayar ta ta dubi Mama zuciya a raunace ta ce
"Mama na tafi." jiki a sanyaye Mama ta ce
"Ubangiji Allah ya tsare ki da tsarewarsa ya kare ki da kariyarsa, a duk inda kike ki kasance da tsoron Allah, domin shi Allah baya bacci ko cikin kasa katona ka shiga ka aikata sab'on Allah yanaji kuma yana ganin ka, zakuma kaje ka tarar da shi."
kai ta jinjina kana tayi mata sallama ta fito sakar gida.
Mama tabi bayan ta da kallo yayin da wani irin rauni ya ziyarce ta, 'yarta d'aya tu tilo a duniya bata da ikon magance mata damuwar da take gani tattare da ita.
hannu biyu ta d'aga sama ta ce
"Ya Allah dan isarka da buwayar ka dan girman al'arshinka ka tsare min 'yata aduk in da take."
ta mike tashige bathroom domin yin al'walar sallar magriba da ake ta kiraye-kirayen sa yanzu.

A sakar gida kuwa SEEDRAH tayi wa Umma sallama, ta shiga d'aki gun su Halimatu suma tayi musu sallama, Suhailat ta ce
"Yauwa SEEDRAH tsaya dan Allah in tambayeki."
SEEDRAH ta tsaya daga bakin kofar.
Suhailat ta karaso in da take ta ce
"Dan Allah wasu irin abinci S.MAN yafi so."
kallon shekeke SEEDRAH tabi ta da shi sannan ta ce
"To ni kuma ina zan sani, nawa a wanne."
"Dakata da Allah ni irin wannan bakin halin taki ce take had'a ni da ke, zaki ce baki san abincin da yafiso ba akan bakya yi masa girki ne."
sai kuma ta d'an sassauta murya
"Kina ji ko SEEDRAH friend's d'ina ne suka bani shawara daga girki ma kad'ai zan iya karkato da hankalin S.MAN gare ni, dan Allah kiyi min wani taimako a matsayin ki na 'yar'uwata zanyi masa girki gobe na kawo masa."
baki bud'e SEEDRAH ta ke kallonta ta ce
"Amma lallai Aunty Suhailat bakiyi dogon nazari ba, yanzu a ce gidan nan akwana ba a d'aura tukunya ba, bazaki iya badawa ayi girki ba amma zaki d'au kud'i kiyiwa wani koton gardin banza can girki, lallai kuwa aiki bai ishe ki ba,
to ni banma san wani irin abinci yafi so ba dan ni ko wanne ma girka masa nake."
"To bance kiyi min rashin kunya ba jeki basai kin fad'a ba zan bincika da kaina, da ma ke asu wa ga uwarsa can ita tasan komai nasa ai zanje gidan gobe."
"Da yafi miki kuwa."
SEEDRAH ta fad'a ta juya tayi gaba abinta.
a can wajen get ta sami Baba ya bata kud'in abin hawa yanata sa mata albarka ta tafi.

Ko da ta isa knocking tayi maigadi ya bud'e mata kofa, ta nufi ciki zuciyarta na bugawa, wani irin tsoro ne yake ta son danne jarumtarta duk da kokarin da take tayi wajen ganin hakan bai faruba.
babu kowa a parlour'n taji dad'in hakan dan haka ta shige d'aki.
bayan ta idar da sallar isha kuma ta fito, ta nufi kichin ta had'a masa kayan tea ta haura sama, a kan table d'in tsakiyar parlour ta aje masa dan batajin zata iya shiga cikin bedroom d'insa.
da sauri ta sauka kasa ta shige d'aki ta kulle.

A b'angaren S.MAN kuwa yana can gurin party da a ka gayyace shi, sai waje karfe 1 na dare ya dawo gidan, ko da ya iske kayan tea d'in sa a parlour ya kwashe ya yi cikin bedroom da shi.

Tun daga lokacin SEEDRAH bata kuma yunkurin shiga d'akin sa kai tsaye ba, sai ta tabbatar da baya ciki kafin ta shiga, da sauri-sauri kuwa zatayi abun da zatayi ta fita.
bata kuma yarda ta cakale shi da fad'a sosai dan ta ga kamar hakan ne yake sa yarika samun da mar tab'a jikin ta, ta hanyar yunkurin dukanta ko yi mata mugunta, har ya kaiga shan bakin ta cikin salon mugunta ko akasin haka.
duk wani abun da zaiyi mata na tozarci takan yi kokarin kawar da kanta, dan kuje wa faruwar hakan sai ta tura masa aniyar sa tasawa ranta cewa ita 'yar aiki ce kawai mai son kub'utar da mahaifinta daga kaidin sa.

Yau kwanan S.MAN biyar da barin kasar nan, yakuma hanata tafiya gida kamar wancan lokacin.

Wani katafaren babban filin kwallo ne da ke cikin kasar Spain, gudu ya ke kamar akan iska yake yana juya kwallo son ransa.
sai lale mutane yake cike da kwarewa had'e da KARSASHI!.
yana daf da wurga kwallo cikin raga ya durkusa kasa tare da dafe mararsa da tayi wani irin tsarga masa.
hannu Sagir ya d'aura a kai tare da fad'in
"Ohh bull sheettt!." yawani naushi iska, da gudu yakaraso gurin sa ya durkusa yana leko fuskarsa da ke sunkuye yana wani irin taunar lips d'in sa na kasa, ya yin da idanunsa suke rumtse.
hankali tashe ganin ga ci ga rashi Bashir ya ce
"S.MAN wai me kake yi ne haka Zinari ne fa akasa saura kad'an kaciwo mana shine zaka sakar musu."
bud'e idanunsa da suka gama rinewa ya yi ya zuba masa kana ya ce
"Kasan adadin Diamond d'in da naciyo dan yau an bawa wasu damar samu ai bai zama laifi ba."
ya yunkura ya mike tsaye da kyar, yana dai-daita tsayuwar sa ya kuma rumtse ido da karfi tare da taunar lab'b'ansa kad'an ya rage suyi jini.
yashiga jan kafarsa a hankali da sauri Sagir ya sha gaban sa ya ce

"Wai me ke damun ka ne kam S.MAN baka da lafiya ne?."
kai ya gyad'a masa kawai yaci gaba da tafiya har ya fita daga filin kwallon.
mota ya shige da sauri Sagir shima ya shiga dai-dai lokacin da couch d'in su wani d'an kasar Thailand yakaraso hankali a tashe yana tuhumar S.MAN kan abun da ya aikata bayan sun saye shi da miliyoyin kud'i masu yawa.
kai ya kawar gefe dan a inda yake jin kansa bama fahimtar abun da yake fad'a yake ba.
Sagir ne ya ce masa baya da lafiya ne nan yaba da okay a maida shi masauki, Sagir yaja motar suka d'auki hanyar zuwa masaukin su.

Ko da suka isa da kyar yaja kafarsa zuwa cikin d'akin su, yana shiga yazube kan gado ya yi rufda ciki.
Sagir ya karaso ya zauna gefen sa cike da tausayawa ya ce
"Sannu S.MAN bari na sa a kirawo Dr."
"A'a kada ka kira sa."
yafad'a yana juya kansa ta d'aya gefen.
sanin halinsa ya sa Sagir bai kuma cewa komai ba, sai sannun da ya cigaba da jera masa.
lamo ya yi yana amsar azabar da mararsa yake basa, sai aikin taunar lab'b'a ya ke, yayin da yashiga kokawa da tunanin da ke barazanar tarwasa kwakwalwarsa.
a hankali ya mike jin marar ya d'an lafa masa da murd'ar da yake.
ido Sagir ya waro cikin mugun mamaki ya ce
"Me nake gani haka."
yafad'a ya na nuna gaban wandon S.MAN da ya yi wani tozo, Man d'in sa ya kunbura ya mike samb'al kamar zai faso wandon ya fito, da kuma gurin da ya kwanta ya jike da ruwa mai yauki.
sai kuma ya kece da dariya har da buga kafa. cikin muryar dariya sosai ya ce
"Wai kai da ma ciwon da ke damin ka kenan kasani zama kusa da kai inata jera ma sannu, na d'auka wani muhimmin ciwo ne na daban, to wlh Allah kayi gaggawar magance damuwarka tun kafin tayi ma illa."
tsaki S.MAN ya yi, ya janyo towel ya rataye a kafad'ar sa sannan ya ce
"Ina ruwan ka."
dariya Sagir ya kuma ya ce
"Ruwana ya na jikina kuma ina da gurin juye shi."
wani tsakin yakuma ja kana ya shige bathroom, ya tub'e kayan jikin sa kana yasakarwa kansa ruwa.

Shiru ya yi yana jin yanda ruwan ke sauka a kansa, ya yin da gefe guda kuwa tamkar kara masa wutar fitina ake, idanunsa ya rumtse da karfi.
zuwa yanzu kam ya fahimci irin fitinanniyar  sha'awar da ke damin sa, sha'awa mai matukar zafi wacce yake ji za ta iya illata shi ma.
ido ya bud'e kan Man d'in sa da ya yi wani irin zillo sakamakon gilmawar da tayi cikin kwayar idanunsa.
matse abar tasa ya yi da karfi yana juya kai cikin mawuyacin hali, har sai da ya durkusa kasa ya sa guiwowinsa a kasa.
da karfi ya fizgo numfashi tare da jujjuya kai.

ya kai tsawon minti biyar a tsunkuye kafin ya mike tsaye ya ja towel ya d'aura ya fito.
Sagir ya zuba masa ido sai kuma yaji tausayin sa ya kama shi.
ganin yad'au jaka yana had'a kaya yasa Sagir mikewa yazo in da ya ke ya ce
"Me zakayi S.MAN?."
"Nigeria zan tafi yanzu."
"Haba kabari mana sai angama wasa, kuma ba lallai bane ma kasa mi jirgi yanzu tun da bakayi bukin ba."
"Ni nasan yadda zanyi ai."
yacigaba da had'a kayan sa Sagir dai na tsaye yana kallon ikon Allah.
yana gamawa ya dube sa ya ce
"Zaka iya kaini airport ko naje na hau taxi."
"Me ya yi zafi muje na kaika."

Ya yi gaba Sagir yabiyo sa a baya, ko da suka isa airport jirgi zuwa dubai yahau, ya kwana a dubai washegari kuma ya nufo Nigeria.
da misalin karfe 2 na rana ya iso Nigeria.

SEEDRAH ce tafito daga cikin bedroom zata kichin sai ganin mutum tayi cikin parlour.
d'an duban ta ya yi kana ya ce
"I need a shot tea just now."
kai ta kawar ta wuce abinta.
shiko sama ya haura yashige bedroom d'in sa dan in da yake jin kansa bazai iya tsayuwa bi ta kanta ba.
kayan tea d'in ta had'a kan tray ta haura sama taje ta dire masa shi sakiyar parlour ta sauko ta koma d'aki abinta.

Bayan sallar la'asar tana kichin tana kokarin d'aura girki ta ji an turo kofar kichin d'in.
tad'an juyo ta kalleshi sai kuma ta kawar da kai taci gaba da abin da take.
"Ke zo nan."
ya fad'a idanunsa a kanta.
batare da ta d'ago ba ta ce "Ina jin ka fad'i ko ma mene ne ai ba sai na zo ba naga dai sakanin mu babu rata."
a kufule ya ce "Tun da na tafi baki gyara bedroom d'ina ba awani dalili, to kud'in aikin ki na wata biyu nayi sizin nashi baya daga cikin kud'in bashin da zan cire."
ido ta waro da sauri ta waigo in da yake ta ce
"Wlh bazai tab'a yiwuwa ba, sai akace kuma baka nan lallai sai an gyara maka d'aki, yanzu dai da ka dawo zan iya gyarawa amma haka kawai ba mai kwana cikin d'aki bazan gyara ba."
ta aje wukan da take gyaran kayanmiya da shi tawuce shi da sauri tanufi sama tana fad'in
"Wlh wahalata bazata tab'a tashi a banza ba, zan gyara d'akin yanzu dan ba a isa a tauye min hakki ba."

Tana shiga d'akin tasoma kad'e shi tana yi tana mita ita dai bataga wani dattin da d'akin ya yi ba,
in banda mutum da shegen kalen fitina ba mene ne.

Ab'angaren S.MAN kuwa, wuce san da zatayi ta gogi jikin sa wan da ita kam ma bata ma san tayi ba. tana alla-alla taje tayi gyaran kada ya aikata abunda ya ce zai aikata wahalarta yatashi a banza.
hakan kuwa ba karamin fama masa mikin da yake ta kokarin magance sa ta hanyar shan wasu tablet's, da zasu rage masa rad'ad'in abun da ke damunsa tayi ba.
dakyar yaja kafafunsa zuwa cikin parlour ya zube kan kujera yana sauke numfashi tare da rumtse idanunsa. akasan ransa ya ke ayyana
"Wannan yarinyar ba karamar mayya bace."

SEEDRAH nagama gyaran ta sauko baki ta tab'e ganin yana zaune yawani rumtse ido cikin kasa da murya ta ce
"Kamar wani mutumin kwarai msstt."
taja gajeren tsaki dai-dai tazo zata gotashi, saiji ta yi ya fisgota tafad'o jikin sa.
waro ido tayi tashiga yunkurin mikewa ajikin sa ta na fad'in
"Meye haka nifa bana son irin wannan is."
batakai ga karasawa ba ta had'iye ragowar kalmar a gigice jin in da ya sauke hannunsa, tayi wani irin yunkurawa ya dawo da ita tare da matseta gam.
hannayensa nakan ababen kirjinta.
sai a lokacin ya bud'e idanunsa cikin wani irin yanayi mai wuyar fassara yakife fuskarsa a gefen wuyanta yana binsa da wani irin sumba da latsa, ya yin da yake matse ababen kirjinta.
SEDDRAH da gaba ki d'aya tagama firgita hankalinta ya yi masifar ta shi, kub'uta kad'ai take nima duk yanda taso kwatar kanta abun ya faskara.
da sauri har jikinsa na b'ari ya mike tsaye tare da ita a jikinsa, kana ya juyo da ita ta gaba suna fuskantar juna.
tana kokarin kub'ucewa ta gudu ya rungumota sosai yakai hannu kan zip d'in rigarta yana kokarin zuge shi.
cikin muryar zallar tsoro ta ce
"Wlh Allah idan ka sake kayi min wani abu sai kayi dana sani, kasake ni karabu da ni, kada ka cire min riga Allah ya isa mugu."
ket ta d'auke wuta jin ya rabata da rigar, kara ta kwalla cike da bakinciki da takaici ta rumtse idanunta da karfi tana jin wani irin tsanarsa na shigan ta.
cirota ya yi a jikin sa yana bin ababen kirjinta da wani irin mayataccen kallo da suke cike tup-tup cikin bra farare soll da su,wan da bra'n bai rufesu duka ba saman bababen kirjin nata duk awaje suke, sabo da girman su girman nono mai kyau ba irin girma mai muninnan ba.
nannunsa na rawa ya sauke saman d'ayan ya shafo shi, wani irin shock yaji tundaga tsakiyar kansa har zuwa tafin kafarsa.
SEEDRAH kuwa zamewa tayi ta sulale kasa tana kare kirjinta da hannayenta.
yabi ta da sauri ya kwanto jikinta kokarin kuma rabata da bra'n yake tasaki kuka mai ciwo cikin

muryar kuka sosai ta ce
"Kaji tsoron Allah idan ka cutar da ni bazan tab'a yafe maka ba, idan kafi karfina bakafi karfin Allah, tun anan duniya zakaga karshen ka, ya Allah kakawo min agaji kada ka barshi ya cutar dani."
wani kuka ta kuma sakewa jin yanda yake wani shafata da kissing d'in sassan jikinta, hannunsa na yawo asaman ababen kirjinta.
idanunsa sunyi jajir sai fidda numfashi yake da sauri-sauri.
rumtse ido tayi da karfi jin yanda wani abu yake gogar jikinta kamar tab'arya sai danna MAN d'insa yake da gogashi a jikinta.
hannunta ya ruko ya d'aurashi kan gaban wandonsa daya gama jikewa Man d'insa yawani irin mugun kumbura, ya had'e shi da hannunta ya matse.
kara ya d'an sake tare da fad'in
"Ohhhhh ahh ohh my good."
dad'a had'e hannunta ya ke da abartasa yana wani irin jan numfashi mai had'e gurnani yagama susucewa gaba d'aya kamar zai shid'e.

Da karfi tayunkura jin yana kokarin zare sket d'in jikinta,
ta takarkare ta sake masa cizo a kafad'a da karfi, ba shiri ya d'aga hannunsa daga kokarin rabata da siket d'in da yake.
hakan yasa ta sami da mar kufcewa tamike da gudu tashige d'aki tarufo kofa tamurza key.
a bakin kofar ta zube kasa tare da sakin wani irin kuwan bakinciki.

A parlour kuwa jingina ya yi da jikin kujera tare da dafe kai. da kyar ya mike yaja kafarsa ya haura sama, duk wani kwayan da yarika afawa cikin sa baisa yaji sassauci daga abun da ya ke ji ba, yazube kan gado yana damke mara.

A b'angaren SEEDRAHA kuwa da sauri ta mike kamar an zabure ta tashiga share hawayen idanunta, kana tabud'e wardrobe tad'au jakarta ta kwashi kayanta duka, kana ta sauya wani kaya.
ta saka hijabi tad'au jakarta tafito.
can ta hangi rigarta yashe sakiyar parlour ta isa da sauri ta d'auka, kusa da rigar taga wasu kud'i masu yawa 'yan dubu-dubu nasa ne garin kokawa suka zube a gun, ta zari guda d'aya, cikin hanzari tanufi waje.
a bakin get maigadi ya tare ta.
